# KAWAR ZUCIYA

# 2

**Sumayyah AbdulQadir**

**07030137870 (whatsapp only)**

**babbangoro2015@yahoo.com**

**takorikabara@gmail.com**

*Assalamu alaykum TAKORITES.*

**Kafin mu fara ina farin cikin tallata muku Hajiya Aisha Umar Dauda mai A&A Incense & Collections.**

**Dealers ne nadukkan kayan Oriflame Products & GHT Products. Sanan suna da Room Freshener, Toilet Cleaner, Tiles Cleaner, Glass Cleaner, Dish Wash, Hand Wash, Shoes & Bags, Hand Made Shoes, Atamfa, Shadda, Materials, Kid's Wears, Electronics, Perfumes and many more.**

**Domin sayen daya ko sari ana iya tuntubarsu a;**

**No.1 Beside Lolo Dakare's Filling Station Hajj Camp, Katsina State.**

**Suna aikawa ko'ina. Ko a tuntubesu kai tsaye a wannan lambar waya don saka order.**

**08067303736**

**08054647489**

“Rabbana hablana min azwajina wa dhuriyyatina qurratu a’ayunin wa ja’alna lil muttaqina imaama”.

**SADAUKARWA NE GA**

**“TAKORI’S LOUNGE”.**

**Ina alfahari da kasancewa tare daku har tsayin wannan lokacin. Allah da ya hadamu haka, a inuwar al’arshinsa ya barmu tare cikin Alherinsa… har zuwa ranar da muka daina numfashi.**

*–Sumayyah Abdulkadir*

**01/01/2025**

# KAWAR ZUCIYA ( Littafi na 2

**W**

**ani abu da ya ja hankalin Mama akan Safiyyah shine har zuwa wannan lokacin Safiyyah ba haihuwa, ba ko batan wata balle a saka ran samuwar ciki. Duniya kam daidai gwargwado suna cikinta itada mijinta suna juya jin dadinta son rai, itada Zayyan basu nemi komai sun rasa ba, amma haihuwa shiru kake ji ko sama ko kasa kamar an aiki bawa garinsu, tuni anyi auren duka 'ya'yan Mama saura Hatoon, itama din da saka ranarta a kanta.**

**Mama tana Katsina bata zuwa Abuja, amma kullum Zayyan yazo gabanta sai ta yada zance akan rashin haihuwar Sophie, in kuwa suka hadu, Mama sai ta fada mata baka koda ta cikin ruwan sanyi ne akan rashin haihuwa. Amma Zayyan bai taba damuwa da korafin Mama ba. Hasalima shi mantawa yake da wata haihuwa saboda yawan hidimdimun dake kansa.**

**Har ya zamana Safiyyah bata marmarin abinda zai kawo ta Katsina, Mama tayi nata, su Zubaidah suyi nasu gorin, rannan Zubaidah take tambayarta "wai sau nawa ake yi musu kwasar masai a shekara?"**

**Safiyyah ta dubeta cikin rashin fahimta ta ce "kamar yaya?" Sai Yaya Zubaidah ta gyara zama cikin izgili, da shakiyanci, tayi dariyar rainin hankali tace mata.**

**"Yo dole in miki wannan tambayar. Don na san a wata guda kike cika masai da kashi, tunda kin gaza kasaye Da ko 'ya ko guda daya, shine nake mamakin ina kike kai buhunhunan abincin gidanki da basa ko shekara sun kare in ba masai ba?".**

**Wannan magana ta yiwa Safiyyah ciwo. Har ta kira mahaifinta a waya a ranar tana kuka, tace "Malam kayi min addu'a Allah ya bani haihuwa idan inada rabo". Kuma sune kalaman da**

**suka sa ta fara kwadayin son haihuwar itama. Amma da fari bata ko damu ba.**

**Malam Usman kuma yace "Zan yi miki addu'a Nana Safiyyah, Allah ya baki mai albarka, daina kuka kinji baya saka komai kuma baya hanawa. Komai kika ga ya faru da rayuwar bawa haka Allah ya riga ya rubuta masa. Idan haihuwa alkhairi ce zan roka miki ya baki, idan ba alkhairi bace a gareki ya baki abinda ya fita alkhairi".**

**Idan kuwa sune suka zo Abuja yin wata hidimarsu suka sauka a gidanta to har su tafi babu alkhairi a tsakaninta da 'ya'yan Mama, sai gori da bakar magana da habaici cikin lumana. Yanzu sun bar kiranta diyar Alaramma sai "Barren Lady".**

**Ko su ce "'Yar kauyen Dandume an sha jar miya an yi bulbul. Amma har yau babu Da ba jika a gidanmu balle musa ran zamu samu mai sunan Babanmu".**

**Cikin wasa da Dariya kadai zasu gaggasa mata magana mai sosa rai akan haihuwa, wanda sai ta yi wata yana damunta a rai. Har ta soma tsangwamar kanta da tunanin shin ita me ya hanata haihuwa ne??? da gaske "Barren" din ce ita???**

**Zayyan bai taba sanin wannan sunan da Zubaidah ta kirata dashi ba, don koda wasa shi bai taba damuwa ko ankara da rashin haihuwarsu akan lokaci ba, duk yawan korafin Mama a wurin yake tashi ya barshi bai taba sakawa a ransa ya dameshi ba. Sannan yawan harkokin dake gabansa ma basu barin shi ya tuna wai bashi da Da a gabansa, haka korafin Mama bai taba sawa yayi zancen haihuwa da Safiyyah ba, sai wannan fateful ranar, da Mama ta zaunar dashi tace.**

**"To Hatoon dai, an saka ranar aurenta, nikuma bazan iya zama nikadai a gidannan ba, babu Da ba jika, sai ka**

**san inda zaka samomin 'yan dugui-dugui da zasu dinga taya ni zama da debe min kewarta".**

**Zayyan bai gane me Mama ke nufi ba yace "Au toh, sai na je na dauko miki Baba Ladidi daga Rumah, ta cigaba da zama anan bayan bikin ko?" (Kanwar mahaifinta data riketa).**

**Mama ta zabga masa harara tace "Ladidin ce 'yan dugui-dugui?"**

**Shi har lokacin Zayyan bai gane ba, sai da Mama tayi masa fashin-baki, tace.**

**"Humm! Ita diyar Alaramma ashe 'bakarariya' ce ka auro? Sai uban ladabi da uban sunkuyar da kai da bazai amfaneni da komai ba? Shin ko kana kirge da shekarun aurenku? Babu wata albarkar aure kota bari a gidanka Baffana?"**

**Dariya sosai yayi yace.**

**“Mama rigima, menene kuma bakarariya?” Mama ta fassara masa cikin gatse, “juya” mana (wadda bata haihuwa). In maka da turanci; BARREN! Da Larabci kuma ince ‘Aaqira’. Tunda kai hausa bata isheka ba?”.**

**Sai yayi shiru. Kamar a lokacin ya fara jin Safiyyah bata haihu ba har yau. Jim kadan kuma ya daure yace,**

**“to Allah bai kawo mana ba Mama, zamu baiwa kanmu abinda Allah bai bamu bane?”**

**Mama ta katse shi tace “kada ka dorawa Allah, saidai in tsarin iyali take yi, don taci duniya da tsinke, ko kuma bata da mahaifa sam a jikinta, ko bata da kwan haihuwa.**

**Ni kawai jika nake so, ba kuma na kowa cikin ‘ya’yana ba sai naka Baffa”. Yayi zugudiii yana kallon ta kafin yace cikin shanye damuwa,**

**“duk ‘ya’yan da su Yaya Zubaida suka tara miki a gidannan Mama basu isheki ba? Sai nawa kadai kike jira? Ko jiya kince min Zahra ta haihu, Zaitoonah ta kusa, in kawo akwatin kayan barka…”.**

**Mama tace “bazaka gane ba Baffana, naka daban ne, ina son ganin ‘ya’yanka gabana. Allah shine shaida ko dama can nikam Allah ya shaida diyar Alaramma ba wani sonta nake ba, don dai Allah ya jikan rai Baba ya daure maka gindin aurenta ne, ba kuma wai na sota daga baya bane, illa yadda naga baka korafi akan ta, tana maka biyayya daidai gwargwado kuma, ya tabbatar min kana samun kwanciyar hankali a tare da ita, shiyasa na zauna lafiya da ita har wannan lokacin.**

**Amma akan matsalar rashin haihuwa shekaru takwas da aure yanzu Baffa?! Dole a ji mu a kan ‘drum’ nida ita, da kai dake daure mata gindi, zamu**

**hau samu fado nida ku, na rantse da Allah Baffa.**

**Duk cikin jikokina da kake ikirarin an haifa min, ka gayamin in akwai wanda zaiyi *bearing* sunan Bello Rafindadi in ba naka 'ya'yan ba???**

**'Ya'yan wasu ne ba nawa ba, naka sune nawa. Ko kuwa so kake daga kanka ya zama cewa bayan Bello ya yanke?"**

**Anan inda sukayi maganar nan da Mama, anan wurin ya barta, don bai ji Tauhidi da technology da ikhlasi a cikinta ba shi, sai kace su zasu halicci dan cikin jikinsu. Bai ko tashi da zancen a ransa ba. Rigima da digimin Mama wanne ne bai sani ba?**

**Ko wace irin kalar rigimar ta in tanason wani abu ne bai sani ba? Babu! Baba Bello ya sha fadi cikin raha cewa Mama rigimammiya ce, bai kara yarda da irin rigimar tata ba sai yau data**

**dawo kan rashin haihuwar Safiyyah ta saki layin korafinta na baya na malunta da mallakarsa a minjaye.**

**Tun kuma bayan rasuwar Baba rigimarta a kansa shi Zayyan din ta karu. Komai shi komai shi. Bata ko iya sati biyu bata saka shi a idanunta ba yanzu zata bashi *query* akan Safiyyah ta rike mata shi.**

**Kenan kuma yanzu rigimar tata ta dawo kan haihuwarsu kenan ko?**

**Toh banda Allah wa zai bada haihuwa a lokacin da aka kayyade maka, in banda abin Mama?**

**Yana tafe akan hanyarsa ta komawa Abuja daga Katsina yake wannan tunanin, yau dai Mama ta saka shi a damuwa dolen dole, bayan ya baro Mama a safiyar yau ya kamo hanya. Wasu gungun shanu ke tsallaka titi saura kadan ya kwashe kafafunsu sabida tsabar tunani, Allah ya**

**taimakeshi ya kauce musu, ya dafe sityari sosai.**

**Wani ikon Allah kamar Safiyyah tasan meke faruwa tsakaninsa da Mama a Katsina jiya a kanta, kodayake kamar hadin baki, a dan tsukin itama rashin haihuwar damunta yake yi sosai.**

**Ya shigo gidan yanata sallama bai ji motsinta ba. Ya duba dakinsa da nata duk bata nan, kuma bai ji alamar zubar ruwa daga toilet ba.**

**Duk da haka yace bari ya duba nata toilet din, sai ya murda kofar toilet dinta, Ilai kuwa, a can ya sameta zaune dirshan a dandaryar kasan tayal din bandakin, ta hada kai da guiwa da wani siririn abu rike a hannunta.**

**"Sophie?".**

**Zayyan ya kirata a tausashe, with concern and love in his voice tone, kuma cike da fargaba, don baya raba dayan**

**biyun kuka kashirban Safiyyah take yi mai tsanani.**

**"Me kike yi anan haka? Meke faruwa haka?"**

**Ya tambayeta yana takowa zuwa cikin toilet din. Safiyyah bata amsa ba sai ma jin zuwansa da tayi yasa kukanta ya karu harda da gunji da jin shigowarsa.**

**A hankali kuma cikin faduwar gaba Zayyan ya tako har zuwa gabanta, yasa hannu ya zare abinda ke hannunta ya duba, nan ya gane Pregnancy Test Strip ne (PT Strip).**

**Ya mikar da ita tsaye. "Hey! Is this Pt strip? Me kikeyi dashi to? *Tell me, are you pregnant?"***

**Ya dago ta ya tallafota ya fito da ita zuwa falo. Ya kwantar a jikinsa yana tambaya.**

**"Safiyyah menene hakan? Na kasa ganewa. Menene wannan abun, me kike yi dashi a toilet kamar wata likitar mata?"**

**Saida ya zage sosai da lallashi da banbaki, ta tabbatar ya shiga damuwa irin wadda take ciki, sannan ya samu ta daina kukan. Ya rungumeta sosai a kirjinsa, ya barta ta kwanta lamoo! Kawai tana sauke ajiyar zuciya. Suka baje a dandayar toilet. Kamshin Ultraviolet (*Paco Rabanne)* dinsa yana ratsasu tare, yace "Safiyyah kin dagulamin lissafi, na kasa gane me ya faru dake, kin tsoratani daga dawowata. Ba ko sannu da zuwa? Please explain. Kin sani a duhu!**

**Wani abu ya faru da bana nan? Me ya sameki kike kuka? Me kuma kikeyi da PT Strip? Wani ya zo ya gaya miki wani abu ne daga Katsina?"**

**Duk yabi ya sha jinin jikinsa akan zancen da suka gama jiya a kanta da Mama.**

**Da kyar ya samu motsin bakin Safiyyah inda tace "ba wanda yazo nan. Period dina ne yayi jinkiri, inata murna ko bukatata a wurin Allah ta shekara da shekaru ta biya, ko Allah ya amsa min roko na, shine nayi pregnancy test, but it shows "negative" yau ma kamar kullum".**

**Murmushi yayi ya tallabo habarta saman tafin hannunsa, ya sumbaci saman lips dinta lightly, yace,**

**"ke likita ce da zaki yiwa kanki PT ko karambani da giggiwa na nemowa kai damuwa irin naki Sophie? Haba Nana Safiyyah! Da ilmiki na addini kike damuwa akan abinda kinsan nufin Allah ne? Ko na taba ce miki na damu ki haihu yanzu?"**

**Ido fal hawaye Safiyyah ta dago tana kallonsa da takaici, ba tun yau ba ta san shi ba abinda ya dameshi da rashin haihuwarta, most important abinda yafi baima muhimmanci shine 'soyayyah' da kuma a inganta masa shimfidar aurensa, tunda kullum yana samun yadda yake so dinnan kuma a shimfidarsu, batareda wani cikas din ciki ko hayaniyar yara ko kailular dake cikin shayarwa ba kuwa me zai dameshi?**

**Ko kuma don ba shi ake cewa "Barren Lady" ba.**

**Amma tana kirge da cewa aurensu ya tasarma shiga shekaru takwas bata taba ko batan wata ba, sai a wannan lokacin da period dinta ya dan yi delaying.**

**Itama da farko ai bata damun ba, amma banda yanzu da take neman kaiwa shekaru talatin, don data kokantawa Ammi damuwarta kan**

**matsalar rashin haihuwar nan a can baya Ammi cewa tayi wai "lokaci ne".**

**Ta kuma kara da cewa komai data gani a duniyar nan yanada lokacinsa, in Allah ya nufa. Ta cigaba da gayawa Allah kawai, amma kada tasa damuwa a ranta, ta kuma saka a ranta ba haihuwa ce kadai farinciki ko alkhairin rayuwar aure ba, zama lafiya ma cikin soyayyar miji wani abu ne, ba kuma itace kadai ke samar da zaman lafiyar aure a duniya ba, sannan ba ita ce zata kaita aljannah ba".**

**Wadannan kalaman na Ammi suka sa tun daga lokacin Safiyyah ta sanyawa ranta salama, amma kwanan nan abun ya zo yana barazana ga kwanciyar hankalinta, musamman saboda gorin 'yan uwan mijinta, da uwar mijin kanta, duk sanda ta tuna shekara takwas ba ribar aure tsakaninta da Zayyan, wanda shi zai zama sanyin idaniya a garesu, ya**

**kara dankon soyayyar tasu, sai taji wata irin damuwa ta lullubeta.**

**Musamman saboda habaicin da Mama da 'ya'yanta suke sakar mata** ***directly and indirectly.***

**Ta jima tana sayen PT Strip a boye, bada saninsa ba tana gwada kanta, in taga babu komai haka zatayi kuka a toilet ta gaji ta wanke fuskarta ta fito, ta shiga harkokinta.**

**Ya zamanto cewa Safiyyah ko dan ciwon kai take yi ko zazzabi sai ta roki Allah yasa laulayin ciki ne. Haka zata shige toilet yin PT, amma kullum amsar daya ce "negative".**

**Safiyyah ta fara tunanin ko bata gamsar da mijinta ne shiyasa ta kasa daukar ciki? Gashi ita bata yarda da wani abu wai shi maganin mata ba. A hankali abin har ya zamar mata tamkar 'desperation' ba tareda sanin Zayyan ba, don ba kowanne lokaci damuwar**

**take zuwar mata ba, musamman in suna tare, sai idan ta kadaice ko tana tare da danginsa. Na yau ne kadai Allah yasa ya ritsa da dawowarsa.**

**Don haka Zayyan yau ya sha mamaki don bai taba ganin Safiyyah cikin wannan yanayin ba, jage jage da hawaye gashin kai a hargitse zaune dirshan a tayal din toilet. A saninsa matarsa Safiyyah macece jaruma, mai tawakkali kuma, da iya shanye damuwa komai girmanta.**

**Da kyar ya samu ya lallabi Safiyyah ta daina kukan amma ta bullo da sabuwar rigimar cewa dole suje asibiti a binciki lafiyarsu. Tace duka tsararrakin aurenta daga mai 'ya'ya uku sai mai biyu. Hatta Zaitoon da Zahra da aka aurar a bayan bayanta sun haihu wannan shekarar.**

**Zayyan sai ya fara harzuka, ya dago da mamaki ya dubeta, yace.**

**“Safiyyah ban fahimce ki ba, haihuwar abin *competition* ta koma? Ko kuwa don ace kema kin haihu kikeson haihuwar?**

**Ban sanki da haka ba sam. Kada shaidan ya samu gurbi kuma. Don idan don dayan biyun wannan ne kike son zuwa asibitin, to ni ba inda zanje, sai kije su rakaki inda aka basu nasu maganin haihuwar ki karbo naki”.**

**Haka suka kwana a ranar baram-baram kowa zuciya a kusa, a ganin Safiyyah Zayyan bai damu bane sam da rashin haihuwarsu, saboda bashi ake yiwa habaicin yana cika masai da kashi ba.**

**Rashin nuna damuwar tasa akai ya kara ninka tata damuwar, don a ganinta damuwar ba tata bace ita kadai, tasu ce su duka, inda alkawari.**

**Haka ya jefa filo akan *center carpet* na dakin barcinsu yayi kwanciyarsa ya**

**rabu da ita. Yanata sake-sake a ransa. Ko dai wani yayi musu labe ne yaji kalaman Mama Fatu shine yazo ya tseguntawa Safiyyah ta waya ya daga mata hankali?**

**Kalmar Mama ta 'bakarariya' ko shi tayi masa babu dadi.**

**Yana wannan tunanin ya ganta ta cikin dan hasken *dim light* din dakin, ta mike a hankali ta shige toilet, ta dauro alwallah ta fito, ta canza sutturar jikinta daga rigar barci zuwa hijabin sallahrta, ta shafa turaren 'musk' a hannayenta.**

**Safiyyah ta fuskanci gabas ta tada sallah.**

**Yana daga cikin manyan dabi'un Sophie dake burgeshi. Suke kuma kara mata matsayi a ransa. Cikin halin farin ciki ko akasinsa, bata bari shaidan ya jagoranceta ko ya rinjayeta tayi wani abu ba daidai ba. Tafi gane tayi sujjadah ta gayawa Allah kukanta.**

**Haka yaga ta raba dare a kan abin sallarta, shima kasa barcin yayi, yana jin tsigar jikinsa na tashi da kukanta, tana kuka tana yiwa Allah kirari, tana kambama shi cikin sujjadarta ta hanyar kururuta girman izzarsa da buwayarsa, cikin rokonsa itama ya bata haihuwa, kamar yadda yake baiwa daukacin bayinsa. Ta san ba wai ya manta da ita bane".**

**Daga kwancen da yake Zayyan ya tayata amsawa a ransa da;**

**"Ameen, idan alkhairi ce a garemu da addininmu Safiyyah Allah ya bamu!".**

**Ganin yau bata da alamar sanya hakarkarinta a katifa har goshin asubahi, balle kuma yasa ran zata bi ta kansa, yanzu tafi son samun 'ya'ya akansa ma kenan, humm. Mata iyayenmu!**

**Hakan yasa ya ji kishi a ransa na ko ta haihu 'ya'yansu zatafi so a kansa. Duk kulawar da take masa kansu zata koma. Shi kuma ta rage kulawar da take bashi, haka ya hakura yayi barcinsa ya kyaleta yana tunani mara hujja. Ya manta ko inji ne yana son hutu musamman idan bashi da *service*.**

**Washegari suna karya kumallo ya daga kai daga kurbar tea kadan ya dubeta da kulawa, sai yaga duk ta zabge a dare daya, saboda daurawa kanta damuwar da ya kira ta babu gaira babu dalili.**

**Yaga cewa shi dai a karan-kansa da bakinsa bai taba cewa "*Sophie, meyasa baki haihu ba har yanzu? Ko sai yaushe zaki haihu min? Ko me ya hanaki haihuwa, ko ni Zayyan ina son haihuwa*" ko ire-iren *accusations* dinnan marasa dadi makamancin wadannan da ake yiwa wadda ta samu jinkinrin haihuwa koda wasa bai taba hadashi da ita ba, to**

**na menene zata bi ta damu kanta shima ta saka shi a damuwa rana daya?**

**Domin sanin kanta ne rashin walwalarta tabbas ta san dole zaiyi tasiri akan tashi walwalar.**

**Tana ta faman juya cokali a cikin *tea* ta dan dago, jin yayi *clearing voice* dinsa, sai suka hada ido, kuma duk sai ta bashi tausayi. Ganin ta ko kasa kurbar ruwan shayin da ya hada mata, sai juya cokali take a cikinsa. Zayyan ba tareda dogon tunani ba yace.**

**"Na yarda, muje asibitin a duba mu Sophie. In dai shine abinda zai baki kwanciyar hankali, na lura dake jiya ko runtsawa bakiyi ba.**

**Don haka on one condition zamu je gaban likita; duk abinda sakamako ya nuna, inma nine da matsala ko kece da matsala kada ki daga min hankalinki ki yi tawakkali ki karbi kaddara".**

**Ai kuwa ga mamakinsa nan da nan Sophie ta ware. Ta kurbe shayin da gaggawa har tana kone bakinta. Ta furzar da ruwan zafin a gefe da sauri, yayi mata sannu. Tace "Habiby nagode, tashi mu tafi". Yace "dole ki gode min mana Sophie, tunda kin ci ni da yaki.**

**Ni Zayyan ban taba fatan zuwa teburin likita wai da sunan neman haihuwa ba, because I believed time ne bai zo ba. Kuma nasan dukkunmu lafiyarmu kalau tunda kina regular period".**

**Safiyyah bata saurareshi ba tuni tayi daki ta hau shiryawa.**

**** **** ****

**Zayyan da Safiyyah ne zaune a gaban teburin Dr. Muwadda a ABUTH. Duk wata babbar lalura ta rashin lafiya kota 'medical check-up' iyalin Baba Bello sun fi ganewa zuwa ABUTH, sun fi yarda da kwarewarsu. Da wuya ka ga**

**sun canza asibiti sai 'on emergency case'. Don haka takanas Zaria suka taho daga Abuja, bayan samun appointment na ganin kwararriyar likitar mata Dr. Muwadda Abdullahi Shinkafi.**

**Likitar ta yi ma Safiyyah duk wani bincike da bature ya tanada ta hanyar tasatasai (test-test), sannan ta koma kan Zayyan shima ta bincike lafiyarsa tsaf. Kwana uku a jere suna zarya a asibitin ana gwaje-gwaje da aune-aune, inda sukayi masauki a Zaria Guest Inn, kafin fitowar sakamakonsu.**

**Ranar da aka tattaro sakamakon suna waiting room na ganin likitar, kafin a kirasu ofishin likita Safiyyah saida ta zaga bayi ya kai sau uku, saboda fargabar abinda likiciyar zata ce mata.**

**Shikuwa Zayyan ko a jikinsa, don ya riga ya sakawa ransa haihuwa ba ita kadai ce farin ciki tsakanin shi da Sophie ba.**

**Akwai tsantsar soyayya mai haddasa farin cikin da walwala, wadda ta riga ta haifar da fahimtar juna mai girma a rayuwar aurensu.**

**To na meye zai damu kansa kan abinda Allah bai ga damar basu ba???**

**Sakamako dai ya nuna cewa Safiyyah ce mai matsala bashi ba, tanada lalurar PCOS (polycystic ovary syndrome). Likita Shinkafi, ta kira matsalar Safiyyah da suna 'unexplained infertility' na sanadin matsalar PCOS.**

**Ta dorata kan *treatments* masu kyau na masu lalurar pcos, da magunguna masu tsada wadanda zasu iya taimaka mata tayi *conceiving* idan tanada rabo.**

**Tun a hanyarsu ta dawowa Abuja Safiyyah ke fakar idonsa tana dauke kananan hawaye a idonta, alhalin yana tuki. Ya saka musu karatun Al'qurani a cikin motar cikin qira'ar Salah Bukhatir, a cikin karatun ne Sheikh**

**Bukhatir yazo ayar da take addu'ar samun zuri'a dayyibah cikin Suratul Furqan. Ya karanto ayar nan cikin qira'arsa ta *hafsu* mai dadin sauraro;**

***"Wallazeena yaquluna Rabbana hablana min azwajina wa zurriyyatana qurrata a'ayunin wa ja'alna lil muttaqeena imaama…".***

**Sai kukan Sophie ya kasa boyuwa a wannan gabar, domin ta kasa cotrolling dinsa, ta soma sheshshekarsa a fili tana bin Ayar tana maimaitawa cikin kuka.**

**Kuka sosai Safiyyah ke yiwa Zayyan a cikin motar har saida kukannata ya soma rikitashi, yace cikin rawar murya.**

**"Safiyyah kina so in zubar damu a motar nan ko?"**

**Ta girgiza kai, ita tafi kowa sanin yadda Zayyan baya son kukanta don fitar dashi yake a hayyacinsa. Amma yau dole tayi kuka a gabansa. Ashe-ashe**

**itace mai matsalar! Kukan nata ya karu, fiyeda na baya. Ba shiri Zayyan ya faka motar a gefen titi.**

**"Sophie, so kike ki daga min hankali akan abinda banida ikon baki shi ko? So kike in dorawa kaina damuwar gazawata da kasawata ga baki farin cikin da kike so?"**

**Safiyyah ta girgiza kai tana share wasu hawayen da suka kawo mata caffa da gefen gyalenta, tace "ba haka bane Habiby, inaso ne ko yaya ne nima in ga dan kaina, wanda zai zama *fruit to our love*. Nima in zama UWA inyi *experiencing* abinda ake ji a *motherhood*.**

**Shekaruna kullum gaba suke yi, har gashi ina neman dosar shekaru talatin banida Da ko daya. Kuruciyarmu kullum karewa take yi, ba baya take komawa ba.**

**In ban haihu yanzu ba sai yaushe Habiby? Sai na kai *menopause*? Banida**

**sanyin idaniyar da kowa ke alfahari dashi wato DA. Banida bakin da zan kira kaina Maman wane ko Maman wance.**

**Kaima da kanka Zayyan watarana zaka tsaneni, tunda na kasa maida kai UBA. Ta hanyar ajiye maka abinda kowanne uba ke fatan samu".**

**Karo na farko da yaji Safiyyah ta kirashi da suna ZAYYAN wanda ya nuna tashin hankalinta a fili yake, bata ma san ta fada ba, a kwanakinnan ya fahimci Safiyyah ta zama *desperate* ga son haihuwa kadai.**

**Zayyan ya rungumo Safiyyah sosai a jikinsa, ya ma manta a kan hanya suke, ya sumbaci saman goshinta zuwa karan hancinta, ya ja birki yayi togaciya a lips dinta, inda yayi mata kykkyawar sumba mai zurfi. Yace "Sophie ni ba abinda zaisa na tsaneki, haba Safiyyah, haba Sophie na, nifa Safiyyah na aura**

**ita kadai bada tunanin zata haihu min ko bazata haihumin ba.**

**Ta yaya kuma don baki haihu ba sai in tsaneki akan lalura, bayan daidai gwargwado nasan cewa Allah ke bada haihuwar nan?**

**Kada ki kara wannan shirmen tunanin bana so, abinda ni Zayyan na yarda dashi shine haihuwa ta Allah ce, da ya bamu da bai bamu ba *you will forever remain my alter ego*!"**

**Da haka yayi ta lallashinta har ya samu tayi shiru tana ajiyar zuciya a kan kirjinsa. Can kuma tace "Habiby, babbar damuwata itace PCOS dinnan yanada magani ne ko a'ah, ni da ace ma tace unexplained infertility kadai ne, sai inga kamar zan fi samun sauki a raina fiye da ace mun PCOS gareni. Ni ban gamsu da binciken wannan likiciyar ba, don a tarihin zuri'ar gidanmu kaf! Babu mai PCOS".**

**Zayyan yace da karfafawa "to hell with PCOS and whatever! Ni Zayyan Sophie kawai nake so, haihuwa in Allah ya kawo ina maraba da ita, haka in bai bamu ba, muna cikin godiyarsa *as well.***

**Ya hada hannuwansa biyu yana rokonta. "Chapter closed, don Allah Sophie. Bana son kara jin zancen haihuwa a bakinki daga yau. Kuma kada ki kara kai mu gaban Likita".**

**Amma ina! Safiyyah bata hakura ba saida tayi bincike ta hanyar tuntubar wadanda ta sani akan kwararriyar likiciyar matan da tafi kowa kwarewa a Arewa, nan aka bata labarin Dr. Hadiza Shehu Galadanci, ta jihar Kano.**

**Ta samu labarin Dr. Galadanci ne ta hanyar Anti Dije, ta kudire in ta samu Zayyan ya kaita Zaria bikin Ni'iman Anti Dije sai ta biya Kano ta ga Dr. Galadanci tunda kwana uku zata yi a Zaria. Watakila Dr. Shinkafi bata san aikinta ba, ita a zuri'ar su Ammi ba mai**

**PCOS, kuma ance shi mostly gado akeyi.**

**Hakan ce ta faru. Lokacin bikin diyar Anti Dije Safiyyah ta samu Zayyan ya kaita har Zaria, daga nan sukayi sallama shikuma ya wuce Katsina gun su Mama, a can zaiyi hutun karshen mako, ita kuma ta ci biki a cikin 'yan uwanta, duk da bata da walwala, ga kannenta duka sun zo suma daga Dandume.**

**Biki yayi biki gida ya cika da dangi da abokan arzikin su Anti Dije, ita da su Sabah daki daya suka kwana, washegarin saukarta a Zaria Safiyyah sai ta zare jiki ta tafi Kano ita kadai ba tareda Zayyan ko wani nata ya sani ba, ta hau motar Kanoline daga Zaria, daga nan ta nufi asibitin Standard da Anti Dije ta bata labarin a can aka yi mata maganin barin ciki data yi ta yi shekarun baya .**

**Da tambaya da taimakon wayewar kanta sai ga Safiyyah akan layin mata masu son ganin Dr. Galadanci.**

**Bata sha wahalar samun asibitin Standard ba, saboda babban asibitin kudine da yayi kaurin suna ga matan Kano.**

**Duk da Sophie bata taba zuwa Kano ba sai wannan karon. Hakan bai sa ta rikice ba. Mai Keke Napep ta dauka drop tace ya kaita Standard na Tarauni. Shikuma da yake ya riga yasan asibitin nan da nan ya kaita ya zabga mata kudi.**

**Safiyyah ta bude file ta biya duk abinda aka cajeta na ganin Prof. Dr. Galadanchi, kasancewar Safiyyah sammako tayi bana wasa ba, daga Zaria zuwa Kano, yasa karfe goma na safe ma tana cikin garin Kano. Aka dorata akan layin da mata uku ne kacal a gabanta.**

**Ta samu kujera ta zauna a *waiting lounge* na ganin likiciyar, bata dade da zama ba wata farar mata da ba zata fice tsirarta ba itama tazo ta zauna a kusa da ita, bayan tayi wa Safiyyah sallama. Sai zuba kamshin Humra matar take.**

**Suna nan zaune matar na amsa waya lokaci-lokaci, can kuma ta jefa wayar a kyakkyawar Jakarta, cike da shishshigi ta dubi Sophie, don taga kalar hutu sosai a jikinta itama, ita kuma dama da irin kalar wadanda take kawance kenan, sai ta hau jan Sophie da hira kadan-kadan babu alamu na bakunta, ko irin yau ta fara ganinta dinnan.**

**"Baiwar Allah sannu fah. Na ce sannu fah. Halan kema matsalar rashin haihuwa ce ta kawo ki ganin Dr. Galadanchi?"**

**Safiyyah sai da taji gabanta ya fadi, matar tayi murmushi ganin irin kallon da Sophie tayi mata na mamaki, sai tace,**

**“yo meye abin mamaki don na canki matsalarki? Ai daidakun mata ne ne da sukazo Standard da ba matsalar data kawo su kenan ba, musamman masu fama da lalurar (PCOS)”.**

**Sophie ta bita da kallo kawai, don bata ma san menene ‘PCOS’ din ba ita har yau, bata taba jinsa ba, sai a bakin Dr. Muwadda Shinkafi. Ta ce a ranta,**

**“wasu matan dai Allah ya zuba musu surutu da shiga sharo ba shanu!”.**

**Matar bata san tunanin da Sophie ke yi a kanta ba, ta cigaba da cewa.**

**“Alhalin basu san cewa wahalar da kansu kawai suke yi a banza ba. Ni dinnan da kike gani wane kalar asibitine banje neman haihuwa ba, kasashen duniya manya da kanana babu inda bamu taka don neman haihuwa ba nida maigida na.**

**Mun zubar da dukiya da lokacinmu kamar me a yawon asibiti, duk a banza.**

**A karshe dole nabi hanyar da ta bulle dani, yanzu haka yara na biyu. Wannan zuwan kuwa na zo ne likita ta rufe min bakin mahaifa in samu in huta da haihuwar haka ko na shekara biyu ne, yarana kuma su kara girma".**

**Safiyyah sakin baki tayi tana kallon matar, wadda ta laqawa suna "fadi ba'a tambayeki ba". Hankalinta ya dan fara daukuwa ga abinda matar take labarta mata, amma bata gane zaurancen hanyar da take nufi ta bi, wadda ta bulle da ita din ba.**

**Zata so taji wannan kowacce irin hanya ce, da har haihuwar tazo ta isheta tana neman dakatarwa, ko itama ta gwada, ko Allah zai sa ta dace.**

**Safiyyah sai ta saki jiki da matar nan wadda tace sunanta Ammara, nan suka shiga hirar haihuwa, kamar sun dade da sanin juna, abinki da irin ka gamu da mai irin ciwonka, wanda ya rigaka samun waraka.**

**Ammara tace "shekaruna ashirin da aure kafin na samu haihuwar yaran da nake dasu yanzu. Kema kinsan mun sha damuwa nida maigidan".**

**Safiyyah kuma tace "ita kuma shekara takwas kenan da aure, ko bari bata taba yi ba". Sai hira ta kara mikawa tsakaninsu akan hakan.**

**Ammara tace "haka kawai naji kin kwanta min a rai, gaki kyakkyawa ga kuruciya ga hankali, ga hutu, banda haka banida sakewa da bakin fuska sam.**

**Naga damuwa baro-baro a tare dake, haka kawai yarinyar ki dake zaki bar ciwon damuwa ya kamaki a banza saboda haihuwar da samunta ruwan sha yafi ta saukin sha.**

**'Yar uwa ki rabu da wani yawon asibiti ana cin kudinki a banza, kibi hanyar da zata bulle dake kawai.**

**Rayuwar nan saida dan kaucewa sannan ake ganin daidai".**

**Ta kara saka Safiyyah a duhu, har ta kai da tambayarta "dan kaucewa kamar yaya shin? In ji dai ba kauce hanya ta addini ba?"**

**Ammara tace "kusan hakane, amma ba sosai ba, zauna nan 'yar uwa kiyita walagigin bin likitoci suna jagwalgwala miki mahaifa suna cika ki da surutan wofi, kuma basu da maganin da zasu baki ki haihun".**

**Nan ta bude wayarta ta nuna mata hotonta tare da maigidanta da kyawawan yaransu maza biyu kanana kamar haihuwar kwanika, nan ta kara *brainwashing* Safiyyah wadda a lokacin nan ba abinda ta dauka a matsayin farin ciki da kwanciyar hankalin dan adam sama da 'ya'ya.**

**Haka Ammara tayi ta kwance kan Sophie, tana kara zurmata ga bin irin**

**hanyar data bi ta samu haihuwa. Wadda har zuwa lokacin ta ki fitowa fili ta fadeta sai *indirectly* take maganar.**

**Allah sarki Sophie, ita da kanta bata san ta zama *desperate* ga son haihuwa ba sai yau. Ta yadda har ta dan rasa kyakkyawan tunaninta ta kuma kasa zurfafashi, tarbiyyar shekaru kusan 28 da ilmin addini da mahaifinta Malam ya bata basu sa ta yi tunanin meye ita wannan hanyar da ake ta muku-muku da ita ba'a fito da ita fili an gaya mata ba?**

**Haka ilmin bokonta duk bai yi amfani a wannan lokacin ba. Biyan bukata kawai take nema.**

**Ammara tayi nasarar yiwa Sophie famfo mai yawa a wannan danzaman nasu, har take ce mata ta rabu da zancen kawai na mijinta (Zayyan) da yake cewa shi bai damu ba, tace zance ne kawai na mazan da ke son kwanciyar hankalin matansu, karya yake yi yace**

**wai bai damu da haihuwa ba karya ne, maza sun fi mata son 'ya'ya.**

**Ta kara jefa Sophie a tagumi da damuwa mai tsanani. Tace "da yawan alfarmomin da take samu yanzu a wurin mijinta (wanda babban dan siyasa ne a jihar Kano) a baya data kasa haihuwa bata samesu ko guda ba".**

**Tace mata "saboda matsalar rashin haihuwa taga bala'in dangin miji kala-kala, dana uban miji, don mahaifiyarsa ta jima da rasuwa.**

**Tace bata samu daidaito da martaba a idon su ba sai bayan data yi musu haihuwar fari, Da namiji, tace uban mijinta ya kafa mata karan tsana, har ya taba yin umarnin da aka saketa saki daya, tace da Safiyyah "a karshe dana ga ba sarki sai Allah sai na bazama, na hada da (dan kaucewa) sannan na samu biyan bukata.**

**Wadda a halin yanzu ta sayomin kwanciyar hankali a gidana, da zama lafiya da miji na da ubansa da 'yan uwansa.**

**Nice tauraruwarsu, tunda na aje masu 'ya'ya kuma maza".**

**Safiyyah wadda a cikin kowanne harafi na labarin da Ammara ke bata soyayyarta da da burinta da haihuwa na karuwa (to an extent), haka tsoron ta da rashin samunta shima yana ta kara ninkuwa. Har taji a ranta ko dai itama ta bi hanyar data bulle da Ammaran, komai tsananinta?**

**Wadda har yanzu dai bata kai ga yi mata bayaninta baro-baro ba, aka kira Safiyyah ganin likita, Ammara tace zata jirata ta fito itama ta shiga ta fito, sai su karasa maganar.**

****** **** ******

**Safiyyah a teburin Dr. Galadanci. Bayan ta gaya mata matsalarta na cewa**

**shekarun ta 8 da aure babu haihuwa babu alamarta, likitar tayi mata 'yan tambayoyi na cewa ko ta taba ganin likita akan matsalar? Ta ce eh, sun je ABUTH da mijinta ba jimawa sun ga gynaecologist, sai Dr Galadanci ta nemi ganin result din ABUTH din.**

**Sakamakon Safiyyah na ABUTH shi likitar ta karba ta fara budewa, sai taga cewa ba wani banbanci da duka gwajegwajen da itama zatayi mata. Duk da haka Dr. Galadanchi tayi nata binciken yadda ya kamata ta kuma ce Safiyyah ta koma *reception* ta dan jira fitowar sakamako.**

**Wannan gap din na jiran sakamako ya baiwa Ammara da Safiyyah damar sake hadewa a *waiting lounge* suka dora daga inda suka tsaya kafin sakamakon Safiyyah ya kammala.**

**Safiyyah ta kasa maida kwadayinta kan haihuwa da labarin Ammara, har tace da ita don Allah ta gaya mata**

**kowacce irin hanya ce hanyar data bi ta samu haihuwa, Ammara tace "da dan wuya fa, amma in har kin yarda yafi komai sauki, tunda dai ba a garinnan na Kano kike ba zuwa kikayi kuma a yau zaki koma inda kike, mafi kyau shine a yau muje na raka ki, da zafi-zafi akan bugi karfe 'yar uwa, daga can zaki samu motar Zaria tunda kan titin Zaria ne kauyen yake dama, ba sai kin dawo ta Kano ba zaki samu mota daga can har Zaria. Tafiyar mintuna talatin ce kacal daga Kano zuwa kauyen na Daka-Tsalle.**

**"Kauye kuma?" Safiyyah ta tambayi Ammara, ta ce "Eh a can ne malamin yake. Koyaushe aka je kuma ana samun shi saidai layi". A can kasan ran Sophie taji dan tsoro, ta ji fargaba da darsuwar wani abu, saboda dai ta fahimci komai yanzu, wato ta hanyar bin malamai ake samun haihuwa.**

**Amma data tuno gore-goren Mama Fatu da 'ya'yanta, ta kuma tuna cewa**

**‘ya’ya fa zata samu itama kamar kowa, sannan wadanda su kadai ne zasu dorar da soyayyarta da Zayyan dinta, da kara mata matsayi a zuciyarsa data mahaifiyarsa ta daina kyararta, kuma sune kadai (‘ya’yan) zasu tsaya tare tare da ita a ranar da kowa ya gujeta ko ya juya mata baya ko ranar da bata da karfi ko ta tsufa, amfanin haihuwa da ‘ya’ya yanada yawan da bazai kidayu ba, sune zasu kula da ita idan bata da lafiya, sune….sune…sune komai na uwarsu kamar yadda suka zama sanyin idaniya ga Ammi, aminanta abokan shawärarta, itada Sabah, Rayyah da Rayha.**

**Amfanin haihuwa yanada yawan da bazai lissafu ba, kuma damuwar rashin ta yana da girman da zaisa ka gane dalilin halin yanayin dokantuwa da desperation din da ita Safiyyah ta samu kanta a ciki.**

**Har sai ranar daya faru gareka, wato ranar daka budi ido shekarunka kusan goma da aure babu ko barin ciki balle batan wata a tare da kai sannan zaka gane irin yanayin data ke ciki.**

**Sakamakon binciken Dr. Galadanchi dai ya nuna kusan abu daya dai dana Dr. Muwadda Shinkafi ta ABUTH. Bakinsu yazo daya cewa; polycystic ovary syndrome (pcos) shi ya hana Safiyya ovulating.**

**Fasihiyar Likitar tace "amma ki kwantar da hankalinki ke da mijinki duk kuna da kwan haihuwa, nashi kwan lafiya kalau yake. Amma naki kwan baida kwaliti (inganci) a dalilin cutar 'polycystic ovary syndrome'.**

**PCOS cuta ce wadda 'cyst' wato 'maruru' yake fitowa a cikin 'ovary' din mace (wajen kwan haihuwa) wanda yake hana mace 'ovulation' har hakan ya haifar da rashin haihuwa. Akwai mata da yawa dake fama da lalurar pcos**

**wadanda basu san sunada shi ba, haka akwai da yawa da alamun pcos ko daya baya nunawa a jikinsu, misali daga cikin alamominsa akwai fitowar gashi a kirji kona kasan fuska da sauransu.**

**Kinada pcos wanda alamominsa basu nuna a jikinki ba. Kuma babu alamun cewa naki na gado ne. Pcos an fi gadonsa, amma akwai wadanda keda shi ba tareda sun gada ba. Ana kuma iya maganceshi a hankali.**

**Ta taimaka mata da shawarwarin da suka kamata ta bata, ta rubuta mata magunguna masu kyau da tsada da zasu taimaka mata ta dauki ciki da taimakon Ubangiji dana treatment data dorata akai. Ta kuma bata lambar wayarta don su dinga communicating kai tsaye ta waya ba sai tazo ba, akan duk wani cigaba da aka samu ko akasinsa, tace ta yarje mata kiranta kai tsaye.**

**Dr. Galadanchi tace ita tana ganin matsaloli na pcos iri-iri daga mata**

**wanda ke hana su haihuwa. Tace "a yanzu dai babu likitan da zai ce miki ga hakikanin lokacin da zaki iya samun haihuwa sai dace, maigidanki na bibiyi nashi results din daga binciken ABUTH ya nuna lafiyarshi kalau, don haka kada ki fidda rai, da taimakon Allah zaki iya haihuwa a sanda Allah ya nufa with treatment, ki dage da shan magungunan nan dana rubuta miki".**

**Wannan bayani ya kara jefa Safiyyah cikin damuwa maimakon ya sanyaya mata, har fiyeda damuwar da result din ABUTH ya saka ta. Wannan ya sa ta kara amanna da maganganun kawarta ta Standard, wato Ammara, tun kafin ta baro gaban teburin likitar.**

**Na cewa ba abinda likitoci zasu iya kullawa wanda baya haihuwa, sai dai su saka ka kayi ta asarar kudinka wajen sayen kwayoyin banza, da surutun wofi mara tabbas wadanda bazasu taimaka maka da komai ba.**

**A iya hange da tsinkayen Sophie na lokacin sun amince ta yarda da shawarar wannan matar kawai, in dai hakanne kadai hanyar da zata samar da haihuwa gareta da gaggawa, akwai alamun gaskiya sosai a cikin maganganunta, saboda babu alamun karya ko damfara a tare da ita, ko wani alfanu takeson samu daga gareta, face taimako da haduwar jini, don da ganin ta tafi karfin neman komai a wajen wani.**

**Allah shaidarta ne akan cewa tayi addu'a kuma tana kan yi, ta sha duk wasu tsadaddun magungunan da Dr. Shinkafi ta rubuta mata na tsayin lokaci, wadanda ta duba ta ga duk kusan irin wadanda Dr. Galadanci ta rubuta mata yanzu ne ba wani banbanci mai yawa. Amma Allah bai sa ta dace ba. Watakila mafitar kadai itace wannan da Ammara ta kawo.**

**Watakila Allah ya nufeta da zuwa Standard Hospital ne yau don ta samu mai taimaka mata, don haka bari kawai tayi kundumbala ta bi shawarar Ammara, wannan dogon bayanin na likitoci ya isheta, bata ko son sake jinsa.**

**Tana wannan tunanin sai ga Ammara dinma ta fito itama daga ofishin likitar, take gayawa Safiyyah cikin far'a,**

**"an daure min bakin mahaifa (IUCD insertion), muna iya tafiya yanzu".**

**Suka fito tare, Ammara ta bude motarta wata kankanuwar (Peageout 507). Ta bude ta shiga ta kuma mika hannu ta budewa Safiyyah kofar gefenta tace,**

**"in har kin yarda da shawarata kin kuma yarda bazan cuce ki ba, to kawai ki shigo mu wuce in kaiki Daka-Tsalle. Daga can zan saki a motar Zaria".**

**Without a second thought Safiyyah ta amincewa ranta bin Ammara gidan malami. Ta kama murfin mota ta bude tashiga ta zauna ta rufe kofar.**

**Ammara ta fizgi motar da gudu suka harba kan titi. Suka bullo ta Tarauni suka hau kan Titin Naibawa Zaria Road, wanda titi ne da zai kai ka har garin Kura, ya kuma mike dakai babu shan kwana har Daka-Tsalle.**

**Suna tafe a hanya Ammara na tuki tana kara yi mata famfo irin na matan masu kudi da suka saba da harka da malaman tsubbu. Take ce mata "ta saki ranta, ta ganta kamar ace "kyat!" ta zura da gudu. Tace ai da yawa yanzu mata wayayyu sunfi ganewa zuwa wajen malaman tsubbu akan duk wasu matsaloli da suka sha musu kai ba haihuwa kadai ba, ke har rashin lafiyar da aka rasa gane kansa da gindinsa malaman kauye sunada maganinsa, hakan yafi musu sauki fiye da su**

**dauwama cikin bakin ciki da ciwon, bacin rai da *inferiority complex*, irin na rashin daukar ciki da haihuwa kamar na kowacce mace, da kuma bibiyar likitocin da bazasu kulla musu komai ba sai karerayi da surutan banza.**

**Tace Allah na tuba duk da ana cewa zuwa wajen malaman tsubbu haramun ne, to ai Allah mai afuwa ne mai gafara, bayan bukatarka ta biya kawai sai kayi sahihin tuba, da niyyar bazaka sake aikatawa ba, ba shikenan ba?"**

**Safiyyah sai ta soma shakkah, ta soma tunanin anya ita a matsayinta na Safiyyah diyar Malam Usman wanda ya koyar dasu Tauheedin cewa ba'a yiwa Allah wayo, kuma ba'a tursasashi, saidai ayi ta rokonsa, anya wannan hanyar ta dace da ita?**

**Idan ta bulle da Ammara, itama zata bulle da ita ta samu haihuwa?**

**Ba duka abinda yayi wa 'A' ne yake yiwa 'B' daidai ba.**

**Anya ma wannan hanya ta kaucewa kamar yadda Ammara ta kirata ta arziki da Alheri ce a gareta? In Ammi da Malam da Zayyan suka ji ta taka kafafunta wajen bokaye neman haihuwa wane irin hukunci zasu yi mata? Tunda dai taji ana daga baya sai ta tuba ta shiga rudani.**

**Amma *as a desperate and hopeful as she is* da haihuwa, sai tace bari dai ta daure, in har zata samu haihuwa shi Allah Gafurun Raheemu ne.**

**Daidai lokacin da suka isa dan karamin kauyen, daga can nesa Ammara ta faka motar tace gangarawa zasu yi cikin gonar can dake gabansu, har su tadda waccan bukkar da suke hange daga nesa.**

**Haka suka dage zannuwansu sabida duwatsu suka soma taka tudu da gangare suna shiga cikin gonar.**

**Cikin sa'arsu basu sha wahalar samun dogon layi bama, mata biyu suka tarar akan layin, don haka suka zauna har suka gama suka fito kafin suma suka saka kai a bukkar.**

**Jikin Safiyyah ya soma sanyi da ta yi arba da irin abubuwan dake cikin bukkar, da babu kwana-kwana ko wani shatale-tale sun fi kama da kayan tsafi.**

**Babu Ayar Alqur'ani ko daya ko Gafakarsa, irin na shigifar mahaifinta, wanda shima yake amsa sunan malami kuma ake zuwa wajensa neman taimako.**

**Nan Qaho ne da kawunan matattun dabbobi, can korrai ne da busassun matattun tsuntsaye, da fatun namun daji babu kyan gani sai doyi suke, korayen cike da wasu bakaken abubuwa**

**marassa kyawun gani a cikin kowacce kwarya suna motsi, wanda hakan ya baiwa bukkar *smell* mara dadi mai hamami da wari, daga saman bukkar kuma an sakale konannen kan Damisa, abun dai zallah kyankyami. Saida ta hadiye numfashinta.**

**Wani dukunkunannen mutum ne zaune a kan fatar Akuya, dan tsurut dashi kamar (Dwarf) wato (Wada).**

**“Ku koma ku shigo da kafar hagu, kuma kada ki kara yi mana sallama.**

**Tuni ai Tsimbirbira ta san da isowarki Safiyah ‘yar Usmanu da Hafsatu matar Zayyanu”. Bokan yace da Safiyyah cikin fushi.**

**Saura kadan Sophie ta saki fitsari a wando, ko ta taka da gudu ta koma. Ammara ta gane hakan, sai ta rike hannunta cikin karfafawa ta jata suka koma suka yi yadda yace din.**

**“Maraba – lale da uwargidan Zayyanu. Magajin Bello Rafindadi masu kashin arziki na gidaje har ‘ya’ya da jikokinsu.**

**‘Ya’ya tsakaninki da Zayyanu akwai su, saura taki kadan su riskeku.**

**‘Ya’Ya fal! Har sai kince sun isheki”.**

**Safiyyah ta kara tsurewa, jin ya ambato sunan wadanda suka haifeta da Zayyan, kuma har sana’ar gadon gidansu Zayyan din ya sani, zuwa yanzu ta fara gayawa kanta gaskiyar lamari gidan BOKA ta kawo kanta, bama na malaman Tsubbu ba, irin masu aiki da aljanu da rauhanai don gani har hanji, wadanda kullum Malam yake gaya musu ziyartarsu don neman biyan bukata halakace babba. Domin mu’amala dasu “shirka ne”.**

**Suka yi zaman Rakuma a gaban sa, kamar masu neman gafara. Ammara**

**tace da shi "itama dai ba sai na fada ba na sani, tazo neman haihuwa ne itama. Allah ya taimaki Tsimbirbira a taimaka mata, saboda yadda naji dadin taimakon da aka yi min na cika alkawarina na kawo duk mai bukata.**

**Itama gata na kawo ta Tsimbirbira ta share mata hawaye (wa'iyazu billah). Haihuwa kawai take so, walau mace walau namiji, da gaggawa".**

**Tsimbirbira ya fashe da dariya yace "tuni ai labarinta ya iso garemu da bukatarta tun kafin isowarta.**

**Abu daya zuwa biyu muke bukata daga gareta; jan zakara da jar kaza (fingi-fingi) da za'a hada kwanciya, sai kuma kwan haihuwarta da maniyyin mijinta. Za'a yanka bunsuru a baiwa Tsimbirbira jinin, mu zamu dauki kwan haihuwarta da kanmu, bayan kwana biyu kuma zata dawo ta kawo mana na mijinta, wanda shine mahadin da za'a hada maganin da zan bata.**

**Shekara bazata zagayo ba sai ta haifi 'yan biyu maza biyu zar".**

**Safiyyah *was shocked and frightened* yanzu kam, don ta gama amanna ta kusa fita daga addinin musuluncima gabadaya, saboda rashin tawakkalin ta da Zayyan ya jaddada mata karba da muhimmancin yinsa ga musulmi.**

**Kamar yaya ta bada kwan haihuwarta ta ina za'a dauke shi? Da sperm din Zayyan kuma, ko ta wace hanya hakan zata yiwu?**

**Don haka ta juya a firgice ta dubi Ammara da fuskar tsoro da firgici mai yawa.**

**Nan Ammara ta kashe kunya tayi mata bayanin da a baya bata yi mata ba dalla-dalla. Ta yi mata 'yar rada (whisper) a kunnenta.**

**"Ai dama na gaya miki sai an dan kauce hanya, sannan za'a samu biyan bukata, ke zaki san yadda zakiyi ki**

**kawo masa duk abinda ya bukata, na jikinki kuwa zaku shiga daga cikin shigifar can ne ya dauka, ta hanyar saduwa dake! Mijinki ba ganewa zaiyi ba".**

**Safiyyah ido ya raina fata. Boka ya mike ya shige dan dakin wai yana jiranta, ta bishi da kallon razana da firgici mai yawa cikin kyawawan idanunta.**

**Ammara ta shiga *convincing* dinta cikin kyakkyawan lafazi cewa "is just a simple thing, bai fi ya tara dake na 'yan mintunan da basu gaza biyar ba, kokari zaki yi kawai ki jure ki daure warin jikinsa, don kin ganshi dan tsurut dinnan amma ba karamin fitinanne bane, and you will enjoy him morethan your husband…..".**

**A wannan lokacin ne Safiyyah ta samu kalmar "Innalillahi wa'inna Ilaihi Rajioun" ta fado cikin kwakwalwarta,**

bakinta kuma yayi maza ya kama, ya furtata a fili.

A hankali ta runtse idanunta. Nutsuwarta da tsoron Allahnta suka dawo jikinta. Taji ta tsani haihuwar ma bakidaya in dai son ta ne yau ya kawo ta ga wannan halakar.

Ta tuno tarbiyyar da dattijan iyayenta suka kare rayuwarsu a dorata a kai. Sun kuma sha gaya mata akan damuwarta na rashin haihuwa cewa babu mai baka abinda Allah bai ga damar baka ba.

A yau a bayan idon Ammi, Malam da Zayyan gashi rashin hakurinta ya kawo ta ga halaka har guda biyu; shirka da zina, zinar ma da aurenta….. yau ga inda rashin tawakkalinta, da rashin jin lallashin mijinta ya kawo ta, wai za'a yi zina da ita da aurenta…. kuma da wannan kazamin mushrikin.

**Kafin Ammara ta ankara Safiyyah tayi wuf! Ta mike ta kama hanyar fita bukkar. Tana fitowa kuma sai ta taka da mugun gudu. Gudu take da gaske tun karfinta kamar mai gudu akan iska, ita kanta bata san ta iya gudu ba sai yau, domin gani take kamar Bokan zai biyota ko yasa rauhanansa sau daukota su maida masa ita kota wane hali.**

**Gudu take babu waiwaye har ta samu ta fita daga gonar, ta shiga ainahin cikin kauyen Daka-tsalle.**

**Jama'ar kauyen na kallonta sai gudu take kamar wani ya biyota, ba tareda ta san inda take jefa kafarta ba, ba kuma ta waiwaye, tana rokon Allah in mafarki ne take yi saboda damuwar rashin haihuwa yayi gaggawar farkar da ita haka daga wannan mummunan mafarkin.**

**Gudun neman tsira, nadama da ceton Imani Safiyyah ke yi, wanda yafi kama da gudun famfalaki, har ta hau**

**kan babban titin kauyen, ba tare data sani ba. Bata lura ba wata mota kirar Honda ta taho da gudun gaske duk kokarinta na kaucema Safiyyah hakan bai samu ba. Direban kawai ganin Sophie yayi ta fado gabansa, yayi kokarin cin birki ya hango trailer a bayan sa, dole ya zabi bige Safiyyah don ceton kansa da motocin dake bayansa, wadanda cin birkinsa a lokacin zaisa trailer din ta danne su gabadaya.**

**Haka ya kwashe Safiyyah ya jefar a gefen titi, sannan shima ya gangara gefen titin ya tsaya yana ambaton "innalillahi wainna ilaihi rajioun".**

******* ***** *******

**Motocin da ke tahowa daga bayansu duk suka yi wucewarsu babu wanda ya tsaya, yamma tayi sosai, burin kowa ya kai gida ko gari mafi kusa kafin shigowar dare.**

**Sai tsirarun mutanen da abin ya faru akan idon su ne suka kawo agaji,**

suka rufu akan Safiyyah da aka wancakalar a gefen titi, suka taimaka masa aka saka ta a motar wanda ya bigeta din. Wani dattijo ya shiga gaban motar don nuna musu asibiti mafi kusa. Safiyyah kwance a bayan motar, aka doshi babban asibitin garin Kura da ita.

Da kyar likitocin suka yarda suka amsheta saboda babu report din 'yansanda, wanda ya buge tan yace basu hadu da police ko daya ba daga Daka-Tsalle har suka iso Kura, don haka asibitin ne suka kira police aka rubuta report, shikuma ya biya kudin duk treatment din da ya kama za'a yi mata.

An yi sa'a Sophie bata samu karaya ba amma dai akwai gocewar kashin kafa dana hannu, sai kananun raunika da kukkujewa, abinda ya daukesu har bayan isha'I ana mata treatment kafin Safiyyah ta fara dawowa hayyacinta.

**** **** ****

**A can kuma Tudun wadar Zaria, wato gidan Anti Dije, hidimar biki data jama'a bata sa Antin ta gane Safiyyah bata nan tun sassafe ba. Sai bayan azahar da Rayyah kanwarta ta gane rashin dawowarta gidan, ta tuno tun safe data ganta tana shiryawa lokacin su Sabah suna barci ita kuma ta farka tace mata zata dan fita ne, amma yanzu zata dawo, to bata dawo din ba.**

**Kuma har la'asar ta kawo kai Safiyyah bata dawo ba wanda hakan yasa kannenta da suke tare a daki daya duk suka damu, suka soma kiran wayarta ana cewa "not reacheable".**

**Daga bisani Sabah ce taje ta samu Anti Dije cikin kawayenta cike da damuwa, a lokacin ana shirin tafiya Mother's Eve. Tace.**

**"Anti Dije, ko Yaya Safiyyah ta gaya miki inda zata je ne? Tun safe fa data fita bata dawo ba, kuma bata gaya mana ina zata je ba".**

**Anti Dije ma sai a lokacin ta ankara tun safen itama bata ganta ba, jama'a ne suka sa hankalinta bai kai wurin ba, tace**

**"to ina Safifi zata je haka tun safe bata gayawa kowa cikinmu ba? Amma kira Zayyan ki tambayeshi, bazai kasa sanin ina taje ba, babu inda zata je bada saninsa ba, in kin bibiya ma suna tare".**

**Sabah ta kira Zayyan, bugu daya ya dauka suka gaisa yana ta tsokanarta da amaryar robarsa, yadda ya saba tsokanarta don ita ke bin Safiyyah a haihuwa, amma bata biye shi a wasan ba yau, cikin damuwa tace,**

**"Yaya Zayyan, aunty Safiyyah ta gaya maka inda zata je ne in bi bayanta?"**

**Yace "kamar yaya? Ba kuna gidan Anti Dije ba?" Sabah ta kara shiga cikin rudu, ta ce "eh, duk muna can, kuma tare muka kwana da ita a daki daya, amma da safennan tace ma Rayyah zata dan fita bazata jima ba, amma har zuwa yanzu**

**karfe hudu bamu ganta ta dawo ba, kuma wayarta bata shiga, Anti Dije tace watakila kuna tare a kiraka a ji".**

**Shima ya tuna da safe wajen karfe goma sun yi waya da ita, lokacin isarta Standard Hospital kenan, tace masa "she will call him back" bata jinsa sosai, saboda tana cikin mutane, sai ya dauka 'yan bikin gidan Anti Dije take nufi. Nan kuwa a lokacin tana magana da kawarta ta kan layin asibiti Ammara ne. Tun daga lokacin kuma bata kira shi din ba, shima kuma yaje Batsari gidan Yayarsa Zubaida ta tsare shi da zance irin nata na kullum, wato na kushe rashin haihuwar Safiyyah har yau. Don ma har yau basu san wanene mara haihuwar tsakanin shi da ita ba, da bai san ya zai kare dasu ba.**

**Zubaidah tace "sun lura Safiyyah ta tsare gabansa da bayansa, ta hana shi auren diyar kowa, ta shiga rigar arziki tana wadaka son ranta, tana bakin cikin kada wata tazo ta ci, ta hanashi auren da**

**zai karu dashi sai tatse shi suke itada iyayenta kamar hanji.**

**Ita kuma Safiyyar ta kasa tsinana masa komai tunda har yau ta kasa mayar da shi Uba, cikakken namiji mai iyali kamar kowa.**

**Tace "kwarai zan so sanin me Safiyyar nan ta taka da take juyaka har haka Baffa, ita ba wani shahararren kyau ba, ita ba aji ba (class) ita kuma ba iya kwalliya ba, kullum ka ganta cikin ragga, wai ita me addini, ko sabida sun saka sunanka a minjaye sun wanke sun baka ka shanye ta bakin Mama?".**

**Tsaki yayi "mtssw!". Ya mike yayi bakin kofa ya hau saka takalmansa. A karshe dai basu yi rabuwar dadi ba shi da Yaya Zubaida, don har yace mata ba zai kara tako kafarsa gidanta ba, shi zumuncin Allah ne ya kawo shi baizo don ta aibata masa mata ba.**

**Ire-iren yadda yake kare martabar Safiyyah dinnan a wajen danginsa, yana matukar kara mata bakin jini a wurin ahalinsa bakidaya, ba tun yau ba.**

**Bacin ran Yaya Zubaida ne yasa bai kara kiran kowa a waya ba ranar, har itama Sophien, ya juyo zuwa gida Katsina, inda cikin rashin sa'a kafin ya kai ga isowa Rafindadi Yaya Zubaida ta kira Mama Fatu ta mata korafin ya yi mata rashin kunya akan bakarariyar matarsa, don kawai tace yazo Batsari ya ga 'yammata gasu nan fululu, ya auri mai haihuwa. Shine ya zageta tatas (a cewarta).**

**Don haka yana dawowa Mama ma ta dira a kansa, tace matsayin Zubaidah agareshi yafi na duk wani kwashe-kwashensa da zai zageta sabida mace, Mama ta kara masa zafi bisa zafi, bai samu sararin sake kiran Safiyyah ba saboda kuncin ran da suka hadu suka saka shi.**

**Da faduwar gaba a ransa kadan yace da Sabah "yana zuwa". Sai ya kashe nata kiran, ya soma kokarin gwada kiran layin Safiyyah.**

**Abinda dai ake gayawa su Rayyah din shima shi aka shiga gaya masa wato "not reacheable" wanda hakan yayi matukar tada hankalinsa, domin ba abinda ya zo ransa a lokacin sai *kidnapping*.**

**Dama dai yau tun safe yake fama da faduwar gaba, don haka jikinsa ya gama bashi ba lafiya ba, jikinsa har tsuma yake a lokacin, yace Sabah ta hada shi da Anti Dije.**

**Sun dade suna magana na cankar ina zata je, don itama Anti Dije duk da tana cikin sabga yanzu hankalinta yafi daukuwa ga ina Safiyyah ta shiga, ta tabbatar masa bata san ina Safiyyah taje ba, kuma bata da kawaye a nan Zaria. Cikin fara shiga damuwa Zayyan yace, to gashinan tahowa Zariyan yanzu, su hadu su san abin yi, in**

**cigiya zasu bada su bada cigiyarta, da *report* ga 'yan sanda.**

**Kwarai hankalinsa ya soma tashi. Don haka akan hanyarsa ta zuwa Zaria daga Katsina, tuki kawai yake amma hankalinsa baya jikinsa. Da tunanin ina Sophie zata je babu sanin sa, ba izninsa?**

**Yaushe suka fara 'yar haka shida Safiyyah?**

**Me take boye musu shi da 'yan uwanta da Antinta?**

**Babu irin tunanin da bai yi ba akan ina Safiyyah zata je haka ba tareda ta gaya masa ko kannenta ko Antinta ba, a dai wannnan rayuwar da muke ciki ta kasarmu Nijeriya, ta insecurity da insurgency (rashin tsaro da ta'addanci)?**

**Amma ko kusa bai kawowa ransa cewa Safiyyah zata iya zuwa wani wuri ba tareda izninsa ba, yardar da yayi mata da amincin dake cikin aurensu masu yawa ne, don haka ko kusa Zayyan bai kawo a**

**ransa bata ji nasiharsa ba, da yace su dauki tawakkali akan maganar haihuwa, cewa da yayi sun rufe batun haihuwa da gaske yana nufin hakan baka da zuci, bai zaci ta saka kafa ta wofantar da zancensa ba.**

**Ko yaya Zayyan zai ji a ransa, in yaji cewa Safiyyah ta yi kunnen uwar shegu dashi ne ta kama hanyarta ta fita duniya neman haihuwa ta kowacce hanya???**

****** **** ******

**Sanda Safiyyah ta dawo hayyacinta ta kuma fahimci a inda take kwance asibiti ne, tana kuma jin ciwo ko'ina a jikin ta, ba karamin firgici ta shiga ba. Likita da Nas din dake duba ta suka dinga kwantar mata da hankali, har suka ce ta godewa Allah da babu karaya, shi kuma wanda ya buge ta ya dinga bata hakuri, da kyar suka samu ta nutsu, tace dashi babu komai ai tsautsayi ne. Nan suka tabbatar mata an gyara gocewar kashinta**

**na kafa dana hannu. Kuma mutumin yayi settling bill din gabadaya, aka ce ta bada lambar wani nata a kira su a gaya musu halin data ke ciki suzo su kula da ita, don bazata iya tafiya gida a yau, kuma cikin wannan halin ba.**

**Sai a lokacin Safiyyah ta tafi ga tunanin ainahin abinda ya faru, da kuma sanadin afkuwar hakan, tabbas gagarumin laifi ta yiwa Zayyan. In fact, ta ci amanar aure, bayan ta fita babu iznin mijinta yanzu da bokannan ya samu nasara akanta fa, itada Zayyan shikenan ko! Aurensu ya lalace kenan! Yanzu gashi alhakin Zayyan da Allah yasan bashi da hakkinta, yasa mota tayi awon gaba da ita, don Allah ya nunawa Zayyan bata ji wa'azinsa da ban bakinsa ba, har gashi yanzu bata san ranar warkewarta ba, babu kafar yawon asibiti neman haihuwa data zuwa gidan Malaman tsubbu, balle ayi maganar kafar komawa gida.**

**Kawai sai Safiyyah tasa kuka, ta soma yinsa kadan kadan da sheshsheka. Sannan *with a heavy heart* ta fado/rattabo musu lambar wayar Zayyan, wadda ke kwance a kokon kanta tamkar karatun sallah.**

**'Guilt' ne dai gashinan duk ya lullubeta, don hakika taci amanarsa (tayi satar fita) abinda bata taba yi ba tun aurensu, har anyi kokarin yi mata fyade da aurenta.**

**Tunda sai da yace mata tayi tawakkali ta hakura da batun haihuwa in dai don shi take nemanta, amma kafiya da ci da zuci irinnata yasa taki ji.**

**Wani ikon Allah Zayyan yana shiga garin Kano inda daga nan zai dauki titin da zai kai shi Zaria, wajejen karfe takwas na dare wata bakuwar lamba ta kira shi.**

**Zayyan bai ko kalli wayar ba saboda halin da yake ciki, yana tuki yana azkar, da fari kamar bazai amsa kiran ba**

**don baya cikin yanayi na iya amsar wayar mutane, amma ganin nacin mai kiran a karo na uku yasa ya daure ya dauka, murya a dashe.**

**Nan aka yi masa sallama, aka ce daga Asibitin gwabnati na garin Kura ne, suna tareda mai dakinsa wadda tace sunanta Safiyyah, mota ce ta bigeta akan titin garin Daka-Tsalle, taji raunuka amma da sauki.**

**Zayyan saura kadan sityarinsa ya kwace masa ya shiga fadin….. "Innalillahi…". Allah ya taimake shi ya rike sityarin sosai. Yace musu yanzu ya shigo Kano, nan da 'yan mintuna zai iso asibitin Kuran ya dauketa.**

**Cikin mintunan da basu gaza talatin ba, da taimakon kwatancen mutumin da ya buge Safiyyah ya isa asibitin kauyen.**

**Safiyyah kasa hada ido da Zayyan tayi, ta runtse ido tana hawaye lokacin da**

**taji sallamarsa a dakin, cikin muryarsa mai ratsa zuciyarta yace "AsSalamu alaykum" sannan ya murdo kofar dakin ya shigo cikin nutsuwarsa, a nitsensa yake tsaf bai bari rudewar tasa ya gigice ba yanzun daya ganta kwance hajaran majaran a kan gadon asibiti, makale da allurar karin ruwa a hannunta, gadon da take kwance ya nufo kai tsaye gabadaya hankalinsa ya dauku gareta. A hakan kuma yake gaisawa da jama'ar dakin.**

**Tana ji suna gaisawa suna kuma jajantawa shida mutumin daya bugeta da kuma likitan da ya kula da ita da kuma Nas din.**

**Ya nemi alfarmarsu kan cewa a darennan zai wuce da ita Zaria bazasu kwana ba, tunda alhamdulillah ba karaya a jikinta. Amma Safiyyah taki yarda su hada ido sam.**

**Da taimakon ma'aikatan jinya mata aka sa Safiyyah a gaban motarsa. Zayyan yayiwa ma'aikatan da suka kula da ita**

alkhairi na kudi sosai. A daren wajejen karfe tara na dare suka kamo hanyar Zaria.

Tsakanin Kura da Zaria, bai fi tafiyar awa daya da rabi ba, tun basu yi nisa ba ya kira Anti Dije ya gaya mata ga inda ya tsinto Safiyyah.

Anti Dije ta dinga salati da sallallami, kannenta kuwa sai kuka, jin wai ta samu accident a wani kauye, ita kuwa tun hawansu titi ma tayi barcin gajiya da wahala a seat dint ana gefen damansa, sakamakon allurar barcin da aka yi mata.

Kai tsaye ABUTH ya nufa da Safiyyah don a kara bincikar lafiyarta da kyau, bai yarda da kwarewar asibitin kauyen ba, ta kuma samu kyakkyawar kulawar data dace, kai shi yana tantama ma yanzu akan lafiyar kwakwalwarta, in ba haka ba me ya kaita wani kauye Daka-Tsalle, wa ta sani a can? Ko dai son

**haihuwa ya soma motsa masa kwakwalwar Sophie ne?**

**Don a cikin handbag dinta da aka bashi wadda duk uban gudun da taci bata yarda ta yasar da ita ba, yaga takardun tasa-tasai (test-test) na wani asibiti a cikin jakar.**

**Sannan tun isowarsa Kura da suka hada ido uffan bata ce masa ba, bata ma kara yarda ta hada ido dashi ba, ignoring haduwar idonsu take, don gani take daya kalli idonta zai ga tamkar Tsimbirbira ya aikata abinda ya ambata da ita.**

**Daman dai iyalin Baba Zayyan in har ba asibitin koyarwa na Ahmadu Bello ba, basa gane kowanne asibiti, hatta daga Abuja suna tahowa suzo ABUTH idan lalura bata gaggawa bace, tun bayan rasuwar Baba Bello ya zama addicted da asibitin ABUTH.**

**A can asibitin Anti Dije ta samesu, tare dasu Sabah su duka ukun har ita hudu gabadayansu a rude suke.**

**Duk da ransa a mummunan bace yake da Safiyyah amma haka ya daure yayi ta hidimar lafiyarta, ya shiga nan ya fita can tare da likitocin dake dubata a A&E ko a fuskarsa bazaka ga fushin sa ko bacin ransa da Sophie ba.**

**Har saida ya tabbatar an bincike lafiyarta sosai ba wani mummunan rauni bayan gocewar kashin da kukkujewa da buguwa. Aka bata magungunan rage zogin ciwo ta sha. Tsakanin Anti Dije dasu Rayyah kadai ake tattauna wannan abu da ya daure musu kai, ko ina Safiyyah taje a Kura da Daka-Tsalle ba tareda ta bari dayansu ya sani ba? Don Zayyan ya tabbatar musu acan ya daukota. Har lokacin Safiyyah barcinta take sadidan, an bata maganin barci don ta huta daga azabar ciwon kashi, kuma alhamdulillah iyaka abinda likitan Kura ya fada suma**

**shi kawai suka gani. Iyaka tsinkayensu sun kasa cankar inda taje, da kuma abinda ya fitar da ita ana tsaka da bikin 'yar Antinta wato Ni'ima.**

**Da daddare bayan Anti ta kawo musu abincin dare tace "Zayyan kaje dakin bakin Babansu Ni'ima ka kwana ka huta mana, mu sai mu kwana da ita, akwai gajiya a tare da kai sosai". Amma Zayyan yaki, yace da Anti Dije shi zai kwana su su tafi. Anti bata tafi ba saida ta tabbatar ta zuba mishi abincin data kawo da kanta ya ci, tuwon semo da miyar egusi, har lokacin Sophie bata farka ba, ya kai su Anti Dije gida ita dasu Rayha ya dawo asibitin, sai ya biya ya taho ma patient din tasa da Rufaidah Youghurt, don ya san tana sonta sosai, kuma ya samo mata wanda tafiso (thick and creamy) da fresh milk din Hollandia. Da duk abinda zasu dan bukata na kwana biyu a asibitin harda su brush da maclean da sabulun wanka, don an bata (bed rest) na kwana biyu.**

**Yana tafe yana waya da Anti Dike. Inda ya hana su Anti Dije gayawa Malam da Ammi komai akan fitar Safiyyah, yace shi zai iya tackling koma menene, tunda dai bata taba yin hakan ba. Kuma tunda alhamdulillah ba mummunan rauni sosai a jikin ta, to ba sai sun ji ba, don kada a daga musu hankali.**

**Daga shagon Rufaidah masallacin asibitin ya nufa yayi sallar magriba da isha da suka subuce masa, ya rokawa Safiyyah lafiya, a ransa yana addu'ar Allah yasa alkhairi ne ya fidda Safiyyah daga gida. Wanda ya bigeta ya tabbatar masa a Daka-Tsalle ya buge ta kuma da ganin ta ba cikin hayyacinta take ba, da gudun gaske ya ganta tsakiyar titi a gabansa. Sai ya soma karfafa tunaninsa na anya kwakwalwarta lau take? Hakan kuma bai danne fushinsa ba, amma ya danne fargabarsa.**

**Sanda ya dawo dakin wajejen karfe goma sha daya na dare ne Safiyyah ta**

**farka. Yana shigowa suka hada ido, ba yadda zata yi tayi *ignoring* ya riga ya ga idonta biyu. Sai ta tsayar da idanunta suna kallon nasa cike fal da hawaye.**

**Ya dauke kai kamar bai kula ta farka din ba shima, kwarai yaga razana da rashin gaskiya a tattare cikin idanunta, sai ya ja kujerar dake gabanta can daga saitin kanta ya zauna, ya bude lemun da ya shigo dashi na gongoni na 'Schweppes' ya soma sha.**

**Sosai Zayyan ya share Safiyyah, a ransa yana kissima irin 'silent punishment' din da zai yi mata, har sai ta fallasa abinda take boye musu da bakinta, yayi kamar bai ankara da cewa ta soma sakin sassanyar kukanta cikin in'inarta na nuna nadama ba, ga firgicin tuno Tsimbirbira. Data rufe ido shi take hangowa ya biyota. Jikinta ya hau rawa da kyarma. Rashin ganin fuska daga Zayyan yau, da yadda yayi murtuk da ita ya hade giran sama da na kasa shi yafi**

**komai tsoratata da kara sakata a damuwa.**

**Ga mamakinsa shi kansa, yau kukan Safiyyah ko kadan bai sosa ransa ba, don ya san na rashin gaskiya ne, duk da babu abinda ya tsana irin kukan Sophie, balle kuma bacin ranta akan komai, amma yau kwarai ta yi abinda bai taba zato ba, (satar fita) zai kira abun ko cin amanar yardar da yayi mata? Har shaidan na kimsa masa ko tun yaushe Sophie take yin hakan gareshi bai sani ba?**

**Kuma ina da ina Sophie take zuwa in tace masa zata je Zaria gun Anti Dije? Har sai yau da Allah yayi niyyar nuna masa, shine yasa mota ta kadeta, yadda bata da damar komawa gida bai ganewa idanunsa inda taje ba? Da yake shi Ubangiji ya san bashi da hakkinta, duk wata kyautatawa da *trust* dinsa ya mallaka mata su. Ransa ne kawai bai cire**

**ya baima Sophie don soyayyah, kauna da yarda ba.**

**A irin yardar da yayiwa Sophie, da nagartattun halayenta daya riga ya shaida, da tarbiyyar da yake da tabbacin ta taso a cikin ta, baiyi zaton abinda zuciyarsa ke zargi yanzu a kanta ba gaskiya bane, amma fisabilillah bai taba kawowa a ransa Sophie zata iya ketare iyaka a cikin aurensu ko ta ha'ince shi ba. Tunda ta san ko me take so in ta nemi izninsa bazai hanata ba, gashi yanzu taje tana neman salwantar da rayuwarta a banza.**

**A zahiri Sophie bata taba bata masa rai ta bakanta masa, ta kuma sa masa zato da shakku akanta irin yau ba. Wani matsanancin kishi da bai san yana dashi a kan matar tashi ba sai yau yake fiddo kansa sarari, cikin fushin da yayi da Sophie.**

**Tun Safiyyah na kuka kadan kadan har kukan nata ya fito fili. Ta soma rera**

**masa shi kamar ana busa sarewa ko yaji tausayinta ya saki fuskarsa. Sau tari ta san Zayyan baya bata bakinsa wajen cewa kayi masa ba dai-dai ba. Kuma baya son kayi masa laifi kayi ta bashi hakuri. Shiru yake yi ya dafa mutum da manyan idanunsa da shirunsa har sai ka gwammace ya bude baki yayi maka balbalin fada, ko ya zane ka da bulala fiyedawannan *long silence* din da zaiyi maka. Don zafin kallon data ke gani cikin idanunsa yafi na bulala radadi a jikinta da zuciyarta.**

**To irin abunda yayi mata yau ma kenan. Da kukan nata ya fara damunsa sai ya mike ya shiga toilet yana daura alwala don dare ya nausa yanaso yayi nafila, kasancewar a (amenity room) suke su biyu kacal, ya gama alwala ya wanko bakinsa da brush da maclean dinda ya sayo musu na 'Longrich' sannan ya fito ya fice daga dakin. Ya bar mata kamshin ultraviolet dinsa kadai a dakin asibitin.**

**Can anjima sai gashi ya dawo tare da nurse mace guda daya. A lokacin tana tsane hawayen idanunta tana harhada kalaman da zata yi masa bayani dasu a ranta, don kawar da zargi data lura ya samu muhalli a zuciyarsa da wanke laifinta. Suka shigo shi da nurse din, ganin ta farka kuma ruwan da aka saka mata ya kare sai Nurse din ta cire mata ruwan da allurar dake hannunta don ta huta.**

**Tace "to kukan na menene kuma Mrs. Safiyyah Rafindadi? Bayan gaki ga Oga a gefenki, tunda ya kawo ki ko sau daya bai zauna ba, yanata dawainiya dake. Likita yace ki maida hankalinki wajen shan magani cikin lokaci, in sha Allah sati daya yayi yawa za ki ji dadin jikinki".**

**Safiyyah ta gyada kai. Sai nurse din ta bata maganinta na dare. Sannan tayi musu sallama ta fita, bayan tace inda wani abu shi Zayyan ya kirata.**

**Dakin sai ya koma wani irin tsit, bayan fitar nurse din. Zayyan ya yada kansa bisa kafadarsa akan kujera yana zaune bisa kujera kwaya daya dake dakin, wadda ke fuskantar Safiyyah dake kwance.**

**Ko ya tambayeta ya akayi ya tsintota a Kura? Ko ina kika je a Daka tsalle? Kawai yaja bakinsa yayi shiru. Ita kadai ta gane cewa 'silent anger' ne a kwance kan fuskarsa ma'abociyar kwantaccen saje da gargasa, kuma 'silent punishment' dinsa na shiru dinnan da yafi komai kidimata yauma yake son yi mata.**

**Daga baya Zayyan sai ya lumshe idanunsa yana sauraron kukanta, har barci yayi awon gaba da ita.**

**A washegari ma haka ta wuni kuka, sikuma ya wuni zaune gabanta *silently*. Sallah kadai ke fiddashi masallacin asibitin. Su Anti Dije sai yamma suka zo musu ranar za'a kai amarya Ni'ima**

**gidanta kenan, washegari su Sabah kuma zasu koma Dandume.**

**Har magriba suna tare dasu sai bayan isha suka tafi. Bayan sun tafi *again* zata cigaba da kuka ya bar mata dakin, bai dawo ba sai da ya tabbatar tayi barci.**

**Washegari aka sallamesu suka tattaro suka kamo hanyar Abuja, ko gidan Anti Dije basu koma ba, sai a waya ya gaya mata sun wuce. Tayi addu'ar su sauka lafiya.**

**Sun wuce Kaduna sosai amma ba umh ba umh umh tsakaninsu. Sai ta kukan a fili tana so ya kulata, at least ya tambayeta daga ina kike Sophie mana? Yadda zata samu gangara tayi masa bayani. Amma mutumin saima ya hade giran sama dana kasa yana tukinsa hankalinsa kwance, ransa a bace, hankalinsa ya dauku sosai ga tukin da yakeyi.**

**Data tabbatar Zayyan bazai kulata ba kuma bashi da niyyar hakan, sai ta soma magana cikin rishin kuka.**

**"Kayi hakuri, kayi hakuri Habiby, ka dubi halin da nake ciki ka gafarta min. Wanda ba komai ya janyomin ba sai rashin jin maganarka, da rashin daukar nasiharka, kace inyi tawakkali amma na kasa.**

**Ka yarda koma ina naje, kuma kowanne irin hadari na sanya kaina ciki, sannan na hadu da wannan tsautsayin duk ya faru dani a dalilin son mu rayu tare ne, da son samun 'ya'ya daga gareka, da son cigaba da rayuwa da kai cikin kwanciyar hankali da soyayyar mahaifiyarka data 'yan uwanka dana rasa, kwadayina kullum yana ga samun tsatso daga gareka Habiby!".**

**Tayi shiru kadan tana kallon yadda yake sake hade girar sama data kasa, tana son gane ko bayaninta yayi wani tasiri? Sai bata gane komai ba.**

**Sophie ta gyara kwanciyarta a gefen damansa, jikinta duk ya mata tsami, ta fuskanceshi sosai cikin damuwa da zafin ciwo, fuskarta kan tafukan hannunta tace "wallahi Habiby….." sai tayi shiru, ta kasa karasawa ta kuma saka kuka, ganin yau Habiby ko alamun gezau ya ki yi da damuwarta, balle yayi alamun zai karbi rauninta da tubanta.**

**Sai a lokacin zuciyar Zayyan ta dan fara russuna, yace "Umh? Ina jinki Sophie, kin shirya magana yanzun? Ko na kara miki lokaci ki kara *deciding* me zaki gayamin? Bana son ki takurawa kanki sai kin yimin wani bayani. Bana cikin damuwa kuma banida matsala akan hakan".**

**Da sauri tace "na shirya zan gaya maka gaskiya tsakanina da Allah, amma don Allah kayi hakuri…" ai kawai sai in'inar ta taho mata gabadaya ta sarqe ta, dama in bata cikin nutsuwa sai ka nutsu**

**sosai zaka gane me take cewa in tana magana in'inar bakidaya afkowa take yi.**

**Amma da yake Zayyan da Safiyya sai Allah duk abunda take fada ya gane tsab, bashi da matsala ko kadan da in'inarta, dadima take masa, nan ta fara bashi labarin zuwanta gurin Dr. Hadizah, da haduwarta da Ammara, da zuwansu gurin Tsimbirbira la'ananne.**

**Haka kawai yaji zuciyarshi na bugawa, gumi na karyo mishi, ya rasa ma zafi yake ji ko sanyi, daga inda tace ance sai ta kawo sperm dinsa.… baki daya jikinshi kyarma ya shiga yi har tukin ya soma kokarin gagararsa. Kafin ta kai aya daidai inda tace ance sai Tsimbirbira ya sadu da ita zata haihu, Zayyan bai tsaya yaji karshen ba ya daka mata tsawa jikinsa na zikiri, yace "bana son jin labarin, bana son ji, please ya isheni haka!!!"**

**Ya fada cikin tsawar data kada 'yan hanjinta, kafin ya gangara motar gefen**

**titi a hankali ya kasheta gabadaya, don tsoron kada ya kifar dasu.**

**Ya fara ambaton "Innalillahi wa inna ilaihi rajioun".**

**Ya kura mata ido cikin mamaki da tsoro da tarin disappointment a cikin kallon dake fitowa daga idonsa. Yace.**

**"Safiyyah!" (Sunanda tun suna *dating* wato tun kafin aure rabon shi da kiranta da shi), kafin ta farfado daga wannan *shock* din na kiran asalin sunanta yace.**

**"Kinci amana Sophie, kinci amanar aure, me ya kaiki binta *in the first place?* Gaskiya kinci amanar tarbiyyar da Malam da Ammi suka yi miki yau.**

**Ya buga sityarin da karfi yana fadin "Ni Zayyan kika yiwa haka Safiyyah yau? I can't believe it!".**

**Ya ma rasa me zai ce da ita, saboda tsabar kaduwa. Sophien shi wani ya kusa**

**ketawa rigar mutumci da aurensa saboda son zuciyarta. Ya sake maimaita "Innalillahi wa inna ilaihi rajiun". Zayyan ya dade bai shiga tashin hankali irin wannan ba. Yace.**

**"Safiyyah *why*? Don me kika je? Ko saboda rashin godiyar Allah? In ba haka ba ni Zayyan na taba nuna miki wani abu da ya nuna na damu da haihuwa ko rashinta? Ko na taba matsanta miki akan inason haihuwa da har yasa kika kusa jefa kanki a fushin Allah saboda son wata haihuwa da ni bata gabana, wannan rashin tawakkali har ina?"**

**Sai taji kaman saukar aradu akanta. Tayi suman zaune ta kasa cewa komai, domin ya dauki al'amarin da girma har fiyeda yadda ta zaci zai dauka. Shi gani yake ma kamar Tsimbirbirar ya keta masa haddi sakayawa kawai tayi a gaban idonsa.**

**Wannan tashin hankalin da Safiyyah ta gani a tare dashi yasa ta kasa cigaba da kuka, don ta san duk abunda ya gaya mata ta cancanci ya gaya mata ko don ya huce bacin ransa.**

**Sai ya koma magana cikin rauni. Yace "Safiyyah Allah shaida na ne kan na soki da zuciya daya, rashin haihuwa bai taba sawa na rageki da komai ba, shi ne zaki saka mun da wannan butulcin, ki kai kanki ga wani zindiqi mushriki, kin butulcemin, kin butulcewa Allah, kaicon ki da rashin tawakkali Safiyyah".**

**Ya ja motar a hankali kamar wanda kwai ya fashewa a ciki suka cigaba da tafiya. Har suka shiga Abuja bai kara ce mata ko uffan ba. Kuka Safiyyah ta yi shi har ta ji babu dadi. Kamar hawayenta zasu kare.**

**Taimakon Allah kadai yasa ya iya karasa tukinnan, ya kuma kawo su gida lafiya.**

**Yana fita daga motar ta biyoshi da sauri tana bashi hakuri, zata rike hannunsa yace "idan kika tabani wallahi zan bata miki rai, sai kinyi dana sanin zuwa kusa dani". Ya shige ciki ya barta a wurin.**

**Nan Safiyyah ta zauna a kasa a harabar gidansu a salube, don kafarta ta kasa daukan nauyinta. Ba jimawa da shigarsa ya sake turo kofa ya fito ya fice, bata san ma inda ya nufa ba.**

**Zayyan dai tun daga ranar ya canzawa Safiyyah, wato ya dauke mata wuta, suka koma zaman marina ko zaman doya da manja shi da ita, baya shiga harkarta, baya kulata a shimfida, punishment sosai yake mata, amma in ta gaishe shi zai amsa yana cigaba da tafiya.**

**A lokacin ya maida kanshi wani irin *busy machine* saboda aiki, dare da rana zane yakeyi, yana baiwa kanshi wahala yana ta zane-zane ba gajiyawa, in ya fita harkar neman kwangilarsa ma sai can dare yake dawowa.**

**Safiyya duk ta sha jinin jikinta cewa Zayyan yana zargin Tsimbirbira ya riga ya cika burinsa a kanta, ta dai boye masa ne, don haka gabadaya Sophie ta tsangwami kanta, ta tsani kanta, ta rame ta zuge cikin kwana uku, ta tsani haihuwar bakidaya ma.**

**Gashi ba halin ta kira kowa ta nemi shawara, don tamkar ta yi kirari ta dabawa kanta wuka ne a ciki. Musamman Ammi da Malam, da tsine mata ne kadai bazasu yi ba in suka ji abinda ta aikata saboda son haihuwa. Ta yi istigfar ta nemi gafarar Ubangiji yafi sau shurin masaki. Tace koda wannan *punishment* din na**

**duniya Zayyan ya barta ya isheta kankarar zunubinta.**

**Yau dai Safiyyah ta kasa jurewa, Zayyan barin rayuwarta ne da bazata iya rayuwa babu shi ba, duk ta rame ta zaftare ta dawo rabi, dama jikinta ba wani jiki bane na azo a gani, gainin zata mutu a daki da damuwa sai ta tunkareshi yau, ta same shi a *master bedroom* dinsu yana changing zai shiga wanka.**

**Safiyyah ta tsugunna a gabansa hawaye na tsiyaya a idonta, tace "wajenka nazo Habiby, zan yi karin bayani, koda bazaka yarda dani ba, na rantse maka da Allah asibitin mata ne kawai naje a Kano don a duba lafiyata, a ganomin me ya hanani haihuwa. Don na kasa gamsuwa da binciken wannan Dr. Muwadda din, don ni dai ban taba jin wani abu wai shi (pcos) a dangina na uwa ko na uba ba.**

**Nayi tunanin in nace maka daga gidan Anti Dije zan je Kano asibiti *again* bazaka barni ba, musamman da yake**

**kace kar na kara yi maka zancen komawa asibiti, *which I find it difficult to obey* (wanda na samu kaina da kasa bin umarnin)".**

**Nan ma shiru, Zayyan baice komai ba, kokarin zagayeta yake ya wuce toilet ta sake shan gabansa, ta rungume shi tsamtsam tana hawaye "tace don Allah kayi hakuri ka yafeni Habiby, *I can't actually explain exactly what happened to me that day*… (bazan iya fassara hakikanin abinda ya faru dani a ranar ba) amma abun yafi kama da toshewar basira ….!".**

**Ya dago manyan idanunsa da nan da nan suka kada ya dubeta, saida hantar cikin Sophie ta kada, har 'yan hanjinta saida suka hautsina da ganin bacin ran dake kwance cikin idanunsa, yace.**

**"Safiyyah kece kuwa? Is it really my Sophie? Haihuwar da dole ake samunta ne haka? Har da zanyi magana ta karshe akai kice ta yi miki wahalar bi?**

**Lallai shaidan yana son taka rawa a tsakaninmu akan maganar haihuwa, kuma sai akayi yaya bayan nan?**

**Sai Tsimbirbira din ya ja ki dakinsa zai miki cikin haihuwa ki haihu, tunda ni mijinki ban iya ba…, ko saboda ni na kasa saka miki kwan haihuwa ko….?" Safiyyah ta kusa samun dan karamin hauka a lokacin, da wannan furucin nasa, da hanzari ta kai yatsu ta toshe kunnuwanta, kuka har da sheshsheka da majina tace.**

**"Maganganunka sun yi min tsauri Zayyan. Ni dai na rasa me ya sameni a ranar, amma na yarda shaidan ne, na rantse da wanda raina yake hannunsa bai taba ni ba, ban shiga dakin da yace in shigo ba na samu kaina da gudowa. Habibi ko Ubangiji ana masa laifi a bashi hakuri, ya yafe, (why not you Habiby?)**

**Ka yi hakuri ka yi min uzuri, koda da uzrin bacewar basira ta wucin gadi ne kadai".**

**Zayyan ya dago ya kalleta, Safiyyah ta kara fashewa da kuka tace "ka yarda wallahi komai nakeyi don mu haihu ne Habiby. Ina son 'ya'yanka, ina son samun 'ya'ya daga gareka koda guda daya ne, shiyasa na zama "desperate", amma na tuba daga yau na hakura, na bi Allah na bi ka. Bazan kara zuwa ko'ina ba sai da izninka.**

**Ta makalkaleshi kamar kyanwa, tana yamutsa shi kamar Baby a jikin uwarsa. Gabadaya Safiyyah ta jefa shi cikin wani tunani hade da tausayinta. Ya kuma gane da gasken gaske son haihuwar kawai take a ranta, in kuma bai taimaka mata ta samu ba, watarana zata jefa kanta a halakar da ba zata iya fita ba shima ta jefa shi, tunda an fara da bin kawaye gidan boka.**

**Tun daga lokacin ne, ya shiga tunanin neman *solution* ga wannan matsalar tasu, don hankalin Safiyyah ya kwanta, shima ya huta da kwarzabar da**

**yake sha a wajen Mama Fatu, akan zancen rashin haihuwarta. Ba don rashin haihuwar Safiyyah ya dameshi ba, ko ya zame masa matsala a cikin son da yake yi mata, ko ya zama nakasu a cikin rayuwar aurensu ba. Sai don kawai ya samo musu kwanciyar hankali bakidayansu.**

**Dole ya sauka daga fushin nasa, yasa hannu ya dagota ya tallafota zuwa jikinsa, amma bakinsa da ya tafi yake sumbatarta kusufa-kusufa, bai yi shiru da yi mata nasiha ba, akan ta barwa Allah maganar haihuwa. Don shima ta fara saka shi a damuwa da son haihuwar tun abin baya damunsa sam.**

**A wannan dan tsakanin Zayyan da Safiyyah bakidaya suka fada wani hali na soyayyar samun DA ta kowacce hanya, duk iya tunaninsa ya rasa mafita akan yadda zasu samu haihuwa, ga Mama Fatu ta kara bude wuta da matsa mata lamba a dan tsukinnan da 'ya'yanta mata suke ta**

**ajiye 'ya'ya, don kuwa hatta su Zahra sun haife mata jikoki saura shi, sun sake haifewa kowacce karo na bibbiyu, su da akayi aurensu bayan-bayan na Safiyyah. Maganarta dashi yanzu babu hira mai dadi irinta baya kullum sai korafi da shagube akan rashin haihuwar Safiyyah har fargabar zuwa gaida Mama yake yi. Bata wata hirar arziki dashi kamar da sai slogan dinta na gates cewa bakarariyar matarsa har yanzu dai babu labari. Tace bata ga riba cikin aurensu ba sai faduwa da asarar ciyarwa da bautar da yake yiwa mace.**

**Wannan magana da Mama Fatu tayi ta razana Zayyan da Safiyyah, wanda shi ya kara rura dimautarta da dokinta ga son haihuwa *helter-skelter,* abinda ya kaisu ga yin bincike na ilmi akan yadda ake samun haihuwa da gaggawa ga mai matsalar lalurar PCOS.**

**A garin binciken nasu ne a teburin likitoci daban-daban, kowanne likita**

**saidai ya kawo shawarar cewa suyi (IVF) wato (In vitro Fertilization) da aka fi sani (dashen haihuwa) da harshen Hausa.**

**Safiyyah duk da dokin abun ya cikata wato IVF din, don wannan ne karo na farko data ji 'hope' na zata haihu, in dai Dan kanta ne da ya fito daga jikinta kuma na Zayyan to ko ta wace hanya ce tana maraba da samuwarshi, indai addinin musulunci bai haramta ba, duk da haka basu yi saurin amsawa likitocin ba, sannan basu gayawa kowa ba, saida sukayi nasu binciken na addini ta hanyar neman fatawa daga daga malamai daban daban, sannan sukayi bincike sosai a yanar gizo suka tabbatar IVF baida illa daga fuskar addini, da kuma tabbacin da suka samu daga likitoci na cewa kashi 25-30% na *attempt* din farko ana samun nasara.**

**Duk irin bayanin da yayiwa Mama Fatu, na cewa sun je asibiti shida Sophie, kuma suna kan zuwa har gobe, da**

**bayanan da likitoci suka yi akan matsalar rashin haihuwar tasu, amma ya boye sirrin matarsa inda yace ance matsalar su (unexplained ifertility) ne shi da ita duk lafiya suke, hakan bai sa Mama ta tausaya ko ta tausasa kalamanta akan kaddarar Safiyyah ba. Tace.**

**“Fadi gaskiya kawai ka auro “juya” Baffana, ba wani ‘unexplained infertility’, tunda dai a shekaru kusan takwas da aure ta gagara haifa maka Da ko guda daya, ai JUYA ce kenan, musamman da babu bari ba batan wata mai nuna alamar haihuwa.**

**Wannan makauniyar soyayyar da kake yiwa diyar Alarammannan tayi yawa Baffa, na fadi na kara fadi meye ribarta? Ribar kowanne aure ai haihuwa ce, tunda bata da mahaifar haihuwa kuwa, aurenta babu riba a cikinsa sai asara”.**

**Ta kai ta kawo a yanzu Safiyyah ko gidansu Zayyan ya gagareta zuwa, bata iya shiga sha’aninsu na biki kona**

haihuwa, bama sa gayyatarta, abun nasu babu kawaici babu tausayi da alkunya, kai sai ka rantse da Allah ita zata halicci dan a mahaifarta. Idan kuwa tayi kuskuren zuwa wani sha'ani na iyalin Mama, kamar sunan haihuwar 'ya'yanta Zaitoon da Hatoon da akayi recently, yadda kasan mujiya haka take komawa a cikin su, saboda wulakanci da kaskancin da suke mata, ga yada mata mummunar magana cikin habaici a gaban kowa, akan rashin haihuwa kai sai ka rantse a kasuwa ake sayar da haihuwa.

A kodayaushe sukayi waya da Ammi kuka take tana labarta mata irin mawuyacin halin da take ciki da uwar mijinta da 'yan uwansa, Ammi ba abinda zata iya a kai banda ta kwantar mata da hankali, kullum tausarta kawai takeyi, tace ta kara hakuri kan wanda take yi, matsalar rashin haihuwa ba a kanta aka fara ba, ba kuma kanta za'a kare ba, kada kuma ta fidda rai. Saboda yadda Safiyyah ke gaya ma Ammi Hafsatu halin

**damuwar da take ciki da dangin mijinta, har auren Safiyyah ya soma fita daga ran Ammi, don ta kan ce a ranta sam Uwar Zayyan uwar banza ce, bata da Ikhlasi. Kamar bata haifi ‘ya’ya mata ba itama.**

**Amma a matsayinta na uwa bata nunama Safiyyah hakan ba, amma a ranta ta fara tsanar auren yanzu, don kwatakwata Safiyyah ta rasa nutsuwa da farin ciki a cikinsa, tsakaninta da mijinta lafiya kalau amma zuciyarta babu dadi, duk da ganin zaman daular da take ciki da kowa dake nesa da ita yake yi mata baya sata zama cikin nnutsuwa. Yes, da gaske Safiyyah tana cikin daular miji domin Zayyan kullum kara buda masa nasibi cikin harkokinsa Allah yake yi, har wata ‘yar kiba ya aje ta musamman irin ta kasaitattun mazan Abuja, masu murza naira da jin dadinta son rai. Ita kuma Safiyyah kullum ka ganta kamar marar lafiya kamar kudin guzuri, bata da karsashi da walwala a cikin tsararrakinta.**

**Ya nutsa sosai ga tunanin mafita a garesu. Har zuwa lokacin da Safiyyah ta kara bijiro masa da zancen baya, wato bukatarta na suje wani asibitin kudi a Kaduna, bisa shawarar da likitoci suka bata akan suyi (In vitro Fertilization).**

**Sai ya shiga tunanin ko hakan za'a yi kawai don Safiyyah ta samu kwanciyar hankali ta rike Da a hannunta? Su kuma huta da gori da fitinar Mama Fatu?**

**A daren suna waya shida Mama, yake yi ma Mama maganar cikin damuwa,**

**"Mama yanzu saboda Allah kinji dadin hakan? Mama uzzurawarki ga son Sophie ta haihu kota halin kaka, yasa Safiyyah fara tunanin muyi IVF kawai".**

**Mama ta tambayeshi cikin halin ka'in kula ko meye IVF din?**

**Nan ya yi mata bayanin cewa "Dashen Da a mahaifa".**

**Mama ta zabura, tace "to ba dai cikin zuri'ata ba, amma in kun ga shi zai fishsheku to kuje ku yi tayi.**

**Indai mutum yace ra'ayin Bature zai biyewa shi ya jiwo, shi dama kowa yasan halakakke ne, ku zai halakar ba ni Fatima ba".**

**Mama bata hana ba, amma ta nuna matsalarsu ce yin IVF ba tata ba. Don haka shi da kansa ya yarda suje Kaduna a yi musu Dashen, don itace kadai *last hope* din su.**

**Basu kara bi ta kan Mama akan zancen ba, suka shirya suka tafi Kaduna da niyyar ayi musu dashen haihuwa.**

**A wani babban asibitin kudi a Kaduna wai shi (Nisa Fertility and Gynae Center Kaduna) akayi ma Safiyyah da Zayyan dashen Da (IVF), sosai suka tsaya suka naqalci ilmin abun, ta yadda suka gane komai akansa, kafin su yarda aka yi mata.**

**** ****
****

# RANAR DASHEN

# S

afiyyah ta sha ‘yar wuya wajen yi mata dashen IVF, amma ta dade tana gayawa kanta babu wani dadi a duniya da ya wuce (samun Dan kanka).

Shikuma uban gayyar ba kananan kudi ya kashe akai ba, amma ya gayawa kansa shima gara su haihun, wato su samu Dan ko daya ne a rayuwarsu, in ba haka ba bazai taba samun kan Safiyyah ba. Haka Mama bazata barsu su huta ba.

Na farko idan har ba haihuwa tasamu ba bazata taba dawowa ‘Hijabhie’ dinsa ta baya ba, bazata dawo musu da farin cikin su irinna baya ba, da kulawar soyayyarta da yake ta kewa yazu dare da rana. Shima kuma ba zai huta da kwarzabar Mama data su Yaya Zubaida ba, duk dai akan rashin haihuwar matar tasa, itama Sophie bazata taba hutawa da gorinsu da wulakancinsu da habaicinsu ba wanda basa ko gajiya, kuma shi yafi komai saka mata *inferiority complex*. Kai sai ka rantse haihuwar nan kudi ake

**sakawa a sayota da arha a bakin titi, ko iyawar mutum ke bashi ita.**

**Abin farin ciki a garesu kuma shine kamar almara, daga *attempt* na farko, cikin ikon Allah watanni uku da yin dashennan aka tabbatar da zaunawar ciki na wata uku a jikin Safiyyah Usman (Mrs Zayyan Rafindadi).**

**Duk da cewa a mafi yawan lokuta kashi 25-30 cikin 100 na masu yin IVF a karon farko ne kawai ake yin nasara. Amma yiwuwar nasarar na karuwa bayan an sake gwadawa sau da dama.**

**Dole Likitocin suka rike Safiyyah a asibitin har tsayin watanni hudu don a samu cikin ya zauna da kyau, hutu zallah Safiyyah keyi a gadon asibiti, ta wanke goma ta tsoma biyar. Zayyan ya dauki nauyin komai na kulawarta da hutunta wato ya tsaya ma Safiyyah.**

**Samun miji tsayyaye akan damuwarka da bukatunka ma kadai irin**

**Arch. Zayyan Bello Rafindadi, ba karamar sa'a bace ga diya mace. Ta wannan fannin kam Safiyyah tayi sa'a, ta kuma ta yi sa'a, ta yi wa mata 'yan uwanta da yawa kwalele, na sa'ar samun mijin da ya tara wadannan *qualities* din. Shi Zayyan a halayyarsa da babi'unsa akwai kyautatawa iyali, *he's a caring husband*, baida son kansa, baida mugunta, abin hannunsa kakaf! Na iyalinsa da 'yan uwansa ne, mutum ne mai kulawa, mai tattalin farin cikin iyali, sannan mai sonta da tausayinta da son kwanciyar hankalinta, in ka dauke matsalar mahaifiyarsa Mama mace marar kawaici da rashin maida surukin da baiyi mata ba nata, da 'yan uwansa mararsa kara da zumunci ga Safiyyarsa, da kiyayya da raini gareta maras dalili, to da sai ace Safiyyah tafi matar gwamna sa'ar rayuwar gidan miji kam, saidai kawai matar gwamna ta nuna mata firda-firdan motoci da kantamemen gida da rashin hutu da rashin kwanciyar hankali.**

**Yo kiyayyarsu maras dalili mana? Don ta ko'ina ta duba ta hanga dalilin kiyayyar Mama da 'yan uwan Zayyan a gareta, bata iya ta hango ta ina ta kuskuro su kota ragesu ba, bata ga hujjarsu mai ma'ana na kinta ba, iyaka kokarinta kullum tana yi wajen kyautata musu, duk wani abu da ya zama hakkinsu ne a wuyanta Safiyyah babu jinkiri tana kokarin saukeshi ba sai Zayyan ya fada ko ya sani ba, ba kuma sai ya saka ta ba, hannunta a mike yake kullum ga kowa nasa, wajen kyauta da yawan alkhairi, balle ga su dangin mijinta da haihuwarsu barkar haihuwarsu ko bikinsu baya wuce alkhairinta, kuma sai tayi babbar bajinta take jin dadi, kai har da wanda ba hakkinta ba, Safiyyah yi musu take, saboda kaunar data ke yi ma Zayyan. Amma Mama Fatu da 'ya'yanta babu ragayya ko kankani a tsakaninsu, babu godi bare an gode kawai don bata haihu ba, ko tace Allah bai bata haihuwa dasu ba, babu mai yaba kokarinta, bata da**

**wani farin jini a idonsu saboda ubanta ba mai kudi bane, ba mai Mulki ba, kuma ba mai irin tsarin rayuwarsu ta 'yan boko ba, babban dalilinsu kuma na yanzu an doshi decade bata haihu da dansu ba (shekara goma).**

**Sosai cikin jikin Safiyyah ya bayyana kansa a watanni na biyar da yin dashensa, Safiyyah abin nema ya samu wai matar Dansanda ta haifi barawo, tafi Zayyan So da dokin isowar IVF Baby dinsu.**

**Zancen nasarar IVF da suka samu ya kai kunnen Mama Fatu daga bakin Yaya Zubaina, kasancewar komai Zayyan zaiyi sai yayi shawara da Zubaina. Yanzunma ya damka mata alhakin fara hada musu kayan haihuwar Baby ne inda yace, ta hada komai (unisex) don yaki yarda ma ayi *scan* a gano musu jinsin jaririn, yace shi kome Allah ya basu abin so ne da kauna da tattali a gareshi, walau mace walau namiji.**

**Safiyyah tun samun cikin ta bata je Katsina ba, kuma basu hadu da Mama ba, don Zayyan ya hanata tafiye-tafiye tun fitowarsu asibiti, wato tun zaunawar cikin. Ta kan dai kirata a waya tayi gaisuwar da bata wani tasiri wajen canza matsayinta a gun Mama Fatu.**

**Don haka Mama bata san cikin IVF ya kankama ba.**

**Har saida Zubaina tazo ta sameta kan wane shiri ya kamata suyi na haihuwar matar Baffa, kuma ince ko ta bada dakan yajin haihuwa da sauransu, don dole suyi gagarumin shiri, su yi duk abinda ya kamata a haihuwar Baffan Mama ta farko, bayan kwashe shekaru goma ba'a samu cikin ba.**

**Ta cigaba da gayawa Mama cikin farin ciki da taya dan uwanta murna,**

**"yanzu kinga Mama cikin taimakon Allah IVF din da sukayi**

**(dashen haihuwa) kamar da wasa ya zauna".**

**Ina wuta Mama Fatu ta jefasu shi da Safiyyah? Don babban ashar Mama ta saki, tana cewa "Safiyyah ta ja mata Da ga halaka, saboda bakin cikin ta kasa haihuwa ta hanyar da Allah ya tsara, saboda tana bakin cikin kada ya auro wata ita ta haifa masa naturally.**

**Mama bata taba zaton maganar da Zayyan yayi mata watannin baya cewa wai ta tunzura Safiyyah ga son yin IVF zasu aikata din ba, ta dauka magana ce kawai ta fatar bakinsu. Shiyasa bata wani hana su sosai tun a lokacin ba.**

**Mama tace ita ko a zamanin jahiliyyah bata taba jin inda aka haihu haihuwar dan halak ta hanyar Dashe ba.**

**Tace dan Dashe ba cikin zuri'arta ba, duk da Zayyan ya gaya mata tun kafin ayi bata taba daukar zancen wani *serious* ba, sai bayan data ji sun aikata din kuma**

**ya zauna. Ta fitini kanta da zage-zage. Zubaina ta rasa yadda zata yi ta ganar da Mama IVF ba haramun bane a addinance.**

**Tace a ranta Mama kamar wadda bata yi ilmin zamani ba? Koko ace ta take sanin, saboda son ranta.**

**Mama ta kafe akan ra'ayin ta na cewa ba dai cikin zuri'arta za'a ajiye dan Dashe ba. Har ita Zubainar Mama ta hadasu ta zage tas, tace itace babbar munafuka da ita kadai ake kulle-kulle a gidan Baffa, ita dashi duk an saka sunansu a minjaye su duka an shanye, to su kam wato itada sauran 'yan uwansa sunfi karfin gidan Alaramma.**

**Nan da nan kuma Mama ta figi wayarta ta kira Safiyyah. Don ta kasa hakura da zancen IVF.**

**Safiyyah na zaune a falonta, ta saka tirtsetsen cikinta a gaba, wanda kullum taji motsi a cikinsa sai tayi tazbihi ta**

**tsarkake kudura da iradar Ubangiji. Kunun gargajiya na “Tamba” take sha a kofin Mug, wayarta tayi ruri.**

**Koda ganin yau Mama da kanta ta kirata, Safiyyah farin ciki taji mai yawa, ta dauka a dokance cikin matukar girmamawa har da russunawarta, ta dauka sannu da jiki Mama zata yi mata, don tun fitowarta daga asibiti basu yi waya da Mama ba. Don ko kiran Mama tayi don ta gaidata Mama bata amsa kiranta sai taga dama. Kuma gashi yau ta kira ta da kanta ba sako ba. Don haka yau Safiyyah da taga kiran Mama cikin wayarta ba karamin farin ciki taji a ranta ba.**

**Amma tana dagawa da sallama jin gurnanin Mama kadai ta cikin wayar yasa taji gabanta ya fadi, mummunar faduwa.**

**Ta hadiyi miyau da kyar tana amsa wayar Mama cikin ladabi mai girma, Mama ta basar da gaisuwarta da ladabinta tace,**

**“Sannu Hakimar Baffa! Babbar mace Hakima a gidan Baffa! Ko ince sannu Hakimar Dandume ‘yar Mallam jikar Alaramma. Ni ba kira nayi don mu gaisa ba, kira nayi inji dalilin kawomin Dan dashe cikin zuri’ata mai tsafta.**

**Ashe karyar Malanta kuke babu sanin Allah cikin lamarinku, ki gayamin Ayar da ta ce in ka kasa haihuwa kayi dashen ciki, ko wadda tace dashen ciki ya halatta, zan so kwarai sanin dalilinki na baiwa kanki abinda Allah bai ga damar baki ba, saboda tsoron kada Baffa ya sake ki ne ko don kada ya kara aure da wadda zata haihu?**

**Da zai yi dayan biyun wadannan din da tuni bai yi ba? Yau kuke tare dashi? Ko yau aka fara jiran haihuwar taki?**

**Shin ana aure dole ne Safiyyah, ko Baffana shine autan maza da kika bi kika laqe masa haka? Alhalin bazaki amfanar dashi komai ba?**

**In kina nufin 'ya'yan dashe zaki ke kawomin cikin jikokina kuma in amsa kin yi kuskure, don bazan amsa ba, ba dai ni Fatuma ce zan goya dan Dashe a bayana da sunan jika ba.**

**Don haka tun wuri ki nemi Kakar diyanki in kin haifa a can Dandume, bani Fatun Bello Rafindadi ba, don ban yarda da halaccin haihuwarsu a addinin musulunci ba…...".**

**Safiyyah kasa karasa sauraron Mama tayi, ta saki wayar a kan kujera tana fidda hawaye masu zafi.**

**Ba cin mutuncin Mama gareta ne ya sata kuka ba. Face jin a fakaice Mama na son tabo mutuncin iyayenta, cewa basu san Allah ba. Alhalin su ko sanin anyi dashen ma basu yi ba.**

**Zayyan bai san da wannan wayar da Mama ta bugowa Sophie ba, itama kuma bata gaya masa ba, ita kadai ta bar**

**abun a ranta yayi ta cinta wanda ya sabbaba mata sabuwar damuwa kuma.**

**A rashin saninta shima Mama ta kira shi har gabanta, tayi masa nasa wankin babban bargon akan Dashe da suka yi kwatankwacin nata, tace "ya bata kunya ya rasa mazantaka, ya bari Safiyyah ta mayar da shi waina a tanda, sai yadda taga dama take juyashi, tunda har ta ja shi suyi dashen Da da ilminsa da komai babu iznin ita data haife shi.**

**A karshe ta gaya masa cewa "wannan dan ko an haife shi ba jikanta bane, na Alaramma ne shikadai".**

**Maganar nan tayi masa zafi kwarai, Mama na son sheganta masa Da ne tun ba'a haifeshi ba ko yaya? Wannan cikin da yadda yake son sa tun bai zo duniya ba? Ya kidima ya shiga rudu, ya shiga tashin hankali mai yawa akan kalaman Mama.**

**A iya saninsa ya gayawa Mama zancen zasu yi IVF, kuma bata yi wani mummunan umarni a kai ba. Cewa tayi kawai in sun ga shi zai fishshesu to suje su yi.**

**Don haka tunda ya dawo gida a ranar Safiyyah ta kasa gane kansa, amma koda wasa bai gaya mata komai ba akan zuwansa Katsina, itama kuma ta ja bakinta tayi shiru bata gaya masa wayar da suka yi da Mama akan cikin ta ba.**

**Haka kowannesu ya bar abun a ransa yana damunsa, har zuwa sanda suka manta da shi suka cigaba da shirin taryar Baby dinsu, cike da wata irin soyayya ta daban ga yaron, ko yarinyar, tun bai zo duniya ba.**

****** **** ******

**Cikin Safiyyah ya shiga watanni na bakwai, karkashin kyakkyawar kulawar**

likitocin ta, kulawarsu, tattalinsu da burinsu duka ya koma kan cikin. Wani abun mamaki Zayyan din da a baya yake cewa bai damu da haihuwa ba blah blah blah… sai gashi da akayi wa Sophie dashen Dan, sai yazo yafi kowa son shi, da dokin a haifa masa shi ya dauka.

Har dakin da Babyn zai rayu bayan an yaye shi daga nono Zayyan ya ware a kusa da nasu shi da Safiyyah.

Ya zuba komai na bukatar yara 'toddlers'. Mama Fatu dai ko me yasa? Daga baya bakinta ya mutu akan batun cikin, bata kara aibatawa ba, bayan wancan wankin babban bargon data yi musu. Ganin dukkansu sun dauke mata kafa.

Wannan ya biyo bayan ranar da tayi arba da Safiyyah da tirtsetsen cikinta a gabanta, aka ce Uwa-Uwa ce ba'a sake ki saidai uwardaki, shi da kansa ya hakura da abinda Mama tayi masa ya dauko Safiyyah da tsohon cikinta

**musamman ya kawo ta don ta gaida Mama, daga ranar bakin Mama dana ‘ya’yanta yayi la’asar daga gorin Sophie ta kasa haihuwa, sun yarda ko yaya ne dai ashe akwai kwan haihuwa irinna kowacce ‘ya mace a jikinta, suka gasgata jita-jitan da suke ji din, na cewa tabbas ta samu ciki daga bakin Zubaina, wanda a da suka kasa yarda da gangan.**

**Saboda a ranar ta same su bakidaya a gidan mahaifan nasu (banda Zubaina), suna tsaka da family *meeting* kamar yadda suka saba tare da Baba Murtala akan habakar Estates dinsu na nan Katsina, da sauran fannoni na cigaban rayuwarsu data ‘ya’yansu masu tasowa.**

**Baba Murtala wanda shine makwafin Ubansu a halin yanzu, duk *meetings* din da suke yi a karshen kowanne wata in dai yana gari da shi a ciki, akan rayuwarsu data ‘ya’yansu data Estate din ‘ya’yan Mama ake meeting din, a kowacce asabar din karshen wata, inda**

**Baba Murtala yake shige musu gaba a komai, don kula da habakar dukiyarsu da cigaban rayuwarsu.**

**Duk da Mama ta amsa gaisuwarta, ta kuma ganta da tirtsetsen ciki ta kasa cewa a ranta “Alhamdulillah Baffa zai haihu”, haka ta kasa cewa “Allah ya raba lafiya” saboda can a kasan ranta tana jin wani iri babu dadi, saboda tuntuni ta riga ta sakawa kanta wani negative thought haka (gurbataccen tunani) akan ‘In-vitro Fertilization’.**

**Mama in ta tuna dan Zayyan dinta na farko a duniya, haihuwar Baffanta na fari dan dashe ne (IVF Baby) ne sai taji gara ma bai haifa ba.**

**Yawan korafin Mama akan rashin halaccin IVF yasa Zayyan ya sake bazama neman fatawar Malamai mabambanta, amma kamar can baya, har yau bai ji fatawa sahihiyar da ta haramtashi ba. Saidai malamai suce *surrogacy* shine haramun (wata ta daukar ma mace cikin**

**da sperm din mijinta ta haifar mata dan saboda ita bazata iya haihuwa ba).**

**Amma a duka binciken da yayi na addini akan In-Vitro Fertilization, amsar da yake samu shine;**

**"*IVF is permissible in ISLAM with the condition that it involves the gametes of the married couple and adheres to the sanctity of the marital union, aligning with Islamic principles of lineage preservation*".**

**Ma'ana; Dashen haihuwa ya halatta a muulunci bisa sharadin cewa kwayayen haihuwar da za'ayi amfani dasu su kasance na ma'auratan ne, don a kare martabar aure da samar da zuri'a tsarkakakkiya kamar yadda dokokin musulunci suka tanada".**

******* **** ******

**"The IVF Mother"**

**A wannan lokacin da cikin ta ya shiga watanni na takwas Zayyan baya nisa da gidansa. Haka duk inda yaje Safiyyah na ransa, baya awa biyu bai kirata a waya don tabbatar da lafiyarta ba.**

**Tun cikin nada wata bakwai Zayyan da Safiyyah da taimakon Yayarsa Zubaina sun gama tanadar duk wani abinda jaririn zai bukata, shi da Yaya Zubaina suke shirye-shiryensu ba tareda sun saka Zubaidah ba, har *feeder* da gadon baccin jariri yana nan sun ajiye a cikin dakin sa. Kuma komai suka tashi saya sai sun zabo ajin farko na 'yan gatan jarirai.**

**A ranar da cikin Safiyya ya shiga watan haihuwa ba yadda Safiyyyah bata yi da Zayyan ya maidata Dandume ta haihu a can ba, ya kafe yaki amincewa.**

**Yace "kina wasa ne kema yarinya.**

**Ya kamata ki san cewa *we have to take extra care of this Baby,* tunda dai kin ga da yadda Allah yasa aka sameshi. Bazan barki ki koma Dandume haka kawai inje kiyi haihuwar gida ba, lallai sai a asibitin da ake kula daku anan tun farko zan bari ki haihu, in yaso Ammi ta kawo wadda zata kula da ke gidannan, to wannan kuwa, bazan ki amincewa ba, hankalina ma zai fi kwanciya in ya kasance muna tare koyaushe, fiyeda ina nan nesa, ku kuna can Dandume".**

**A can gidan su Safiyyah Ammi tuni ta soma hada kayan haihuwa, su yajin jego, garin yin kunun kanwa da kanwar kanta duk ta tanada da sauransu, haka ta hada su rankatakaf ta daure jiran haihuwa kawai ake.**

**Da EDD dinta ya rage saura sati biyu shida kansa ya roko Ammi ta basu mai zaman jego. Sai Ammi tace Sabah da Rayyah su shirya su koma Abuja su taimakawa Yayarsu, don masha Allah**

**‘yan matan Ammi sun horu, ba abunda basu iya ba na manya kasancewar su rainon Tsoffi.**

**Har Rayha autar su ta girma Ammi bata san komai na hidimarta da rainonta ba, Sabah da Rayyah ne suka yi raino da hidimarta. Haka in Anti Dije ta haihu su suke mata komai da babba ke yiwa Maijego harda saka ruwan wanka.**

**Haihuwar Safiyyah daban ce da sauran haihuwa shiyasa iyayenta basu takura ta dawo gida ta haihu a gabansu ba.**

**Zayyan daga baya ya yiwa su malam bayanin IVF na asibiti aka yi mata, kuma malam a matsayin shi na babban malami bai yi *challenging* IVF ba, ya dubeshi ta kowacce fuska ta addini bai ga inda ya zama haramtacce ba.**

**Don haka ya bisu da addu’a da fatan Allah ya sauki Safiyyah lafiya.**

**Yanzunma Sabah da Rayyah data turawa Safiyya tana da tabbacin zasu iya, shiyasa ta turo su tunda Anti Dije bazata bar gidanta taje jegonta ba, amma hankalinta bakidaya yana kan babbar 'yarta mafi soyuwa a ranta "Nana Safiyyah". Dare da rana tana yi mata addu'ar sauka lafiya da samun saukin nakuda a kowacce sallahr farillarta.**

**Da murna da doki sosai su Sabah suke shirin tafiya Abuja, don kwatakwata tun komawarsu Safiyyah can bai fi sau biyu suka taba zuwa gidan Yayar tasu ba, shima dubiyarta suka je da bata da lafiya, na farkon kuma sun je ganin gidan ne sanda zasu koma can da zama, malam baya barinsu sam, don kowacce da maganar aurenta a kanta in ka dauke Rayha autar Ammi.**

**A motar haya su Rayyah suka tafi Abuja su biyu. Tun kafin su iso Safiyyah ta ware musu dakin da zasu sauka cike da dokin ganin kannen nata, ta aje masu duk**

**abinda ta san zasu bukata, wannan shine zuwansu Abuja karo na biyu tun dawowarsu Safiyya nan daga Zaria.**

**Sabah dama tafi Rayyah baki, kuma tafi duk sauran kannenta faram-faram da jama'ah. Tunda Zayyan ya je dauko su a tashar Jabi tana gidan gaba Rayyah na baya, shida ita suke hirar tsokanar juna a cikin motar. Zayyan yana tsokanarta da amaryar robarshi, tazo bikon shi, taga baya zuwa zance yanzu, Sabah tace "haba dai inzo bikon ka, na dai zo taron Da na wallahi, kaima kasan kayi min tsufa Yaya Zayyan", Zayyan yak ama baki ciki dariya da mamaki yace "really? Rayyah, yaushe 'yar kauyen matar nan ta kile haka?"**

**Rayyah dai dariya take tana jinsu. Sabah ta kara cewa "Saboda Allah Rayyah nida nake da sarbadeden saurayi irin Jabir a gefe, yaro matashi me jini a jika, dan late twenties, me zan yi da Yaya**

**Zayyan? Wannan kayan tsufan ai sai Nana Safiyyah".**

**Zayyan ya tuntsure da dariya harda bugun sityari yace "amma kin yankeni! Saina gayawa Sophie, kina kira ma darling dinta tsufa tun yanzu".**

**Tunda su Sabah suka zo gidan suke wani irin kula da Safiyyah da komai na kulawar gidan ya koma wuyansu, ko tsinke basa bari ta kawar, ko abinci taci nan zasu kawo mata ruwa ta wanke hannu daga zaune. Zayyan kuma ya wadatasu da kayan dadi suke ta fama, duk fitar da yayi ya dawo sai ya riko musu abinmotsa baki, musamman Rufaida Yughurt da Rufaidah Shawarma da Pizza din Dominos da suke matukar so.**

**Yanzu kam kowa yaga Sophie ya san dan cikin ta ya gama duk wani shirye-shiryensa na isowa duniya. Tashi sai da dabara kwanciya ma haka.**

****** ***** ******

**Safiyyah ta fara wata irin naquda mai matukar wahala ranar wata Litinin, Zayyan baya gida yaje supervising ginin wani sabon Estate da yake ginawa a unguwar Jahi. Kasancewar tunda watan haihuwar Sophie ya kama baya yarda yayi nisa da tsakiyar Abuja.**

**Sabah ta kira shi a waya ta gaya masa yazo su tafi asibiti Aunty Safiyyah fa ta fara nakuda.**

**Nan da nan daa inda yake ya kira asibitinta suka tura motarsu ta daukosu daga gida, shikuma ya bar komai da yake yi a Jahi, ya karya kan motarsa yayi kwana zuwa asibitin. Suka iso kusan a tare da motar asibitin data dauko su Safiyyah.**

**Har da shi aka hadu aka gungura gadon Safiyyah zuwa dakin haihuwa.**

**A cikin awannin da basu gaza uku ba Safiyyah ta haifo santalelen yaron ta**

**namiji mai kama da shi sak. Akan idanunsa, kanta bisa cinyoyinsa, yana mai tayata nishin haihuwar cike da tausayi kamar tare da shi suke labour, yana karanto addu'a yana tofa mata. ganin halin da Sophie ke ciki a wannan lokacin ya kara masa son Mamansa Haj. Fatu, yau ya yarda haihuwa ba karamin al'amari bace ga mata, gashin kanta ya wargaje akan cinyoyinsa yana *supporting* dinta da kalamai na karfafawa, bai gushe ba yana mata addu'a har ta haifo masa Danliti, kuma *photocopy* dinsa, bulelen yaro lafiyayye mai kama dashi sak.**

**Amma me? Likitoci sun yi sun yi yaron yayi kuka bayan isowarsa abu ya faskara, *stillbirth*!**

***** **** ****

**Zayyan sai ya rintse idanunsa a hankali, daidai sanda tunaninsa ya zo nan, yana mai tuno kyakkyawar fuskar jaririn da ya gani a ranar, dan su shi da**

**Sophie, sai ya ji komai na *memories* din wancan lokacin ya dawo masa sabo. Wato lokacin rayuwarsu daga shi sai Safiyyah a gefensa. Amma a hakan ya daure ya cigaba da tunano al'amuran da suka gabata din, a kokarinsa na nemo maslaha da warwara, wadanda duk ba masu dadin tunawa bane a gareshi.**

**Abin kunya da bakin cikin da yafi kowanne girma a gareshi shine, daga Mama har yaranta duka aka rasa wanda zai zo ya duba Safiyyah a asibiti, balle su jajanta ko yi musu ta'aziyyah na yaron da suka rasa, alhalin sunfi kowa sanin halin da suka shiga da wahalar da suka sha akan cikin wadda bazata lissafu ba kafin samunsa, da wadda suka sha bayan samuwarshi, in ka cire Yaya Zubaina da ta kira su a waya, tayi ta lallashinsu, ta kuma tunasar dasu muhimmancin yarda da kaddara da tawakkali akan jarrabawar Ubangiji kowacce iri ce.**

**Saboda Baban Muntaqa baya barinta tafiye-tafiye sosai, amma kwarai taso zuwa har Abuja din, har lokacin Zubaina a garin Kano take aure. Kullum sai ta doko musu waya ta bata lokaci ta lallashesu, tana tunatar da su muhimmancin yin hakuri, da tagomashin da Allah ya tanadarwa wadanda suka rasa 'ya'yansu suna kanana, tace kada susa damuwar hakan a ransu. Allah da ya basu wannan din, a lokacin da suka riga suka fidda rai da samun haihuwa, shi zai kuma basu wani kota IVF dinne cikin kudura da buwayarsa.**

**Daga shi har Safiyyah a wannan dan tsukun kusan zautuwa sukayi a zuci da zahiri, saboda duk wata soyayyarsu da burinsu da kawar zuciyoyinsu ya koma ga zuwan Babyn nan duniya, sun gama tanadin irin tattalinsa da zasuyi cike da soyayya da kauna na iyaye, da kuma tarbiyyar da zasu bashi duk sun gama tsarawa. Kai har makarantar da zasu kai**

**yaron sun zaba tun bai zo duniya ba saboda tsabar dokinsu ga isowarsa.**

**Kwarai su kadai suka san irin wahalar da suka sha kafin Allah ya basu shi ta hanyar 'In-Vitro Fertilization'. Da irin spending din da sukayi akan samuwar cikin da rainonsa. Hakika tattalin arzikinsa ya girgiza akan haihuwar babyn nan da shirin tarbarsa.**

**To ina ruwan Allah! Kana naka shima yana nashi. Kuma nasa shine gaskiya. Duk jarrabawar da yayi nufi ga bayinsa shi ya san ladan daya tanadar musu akanta, zai kuma baiwa bayinsa wannan ladan a duniya ko a kiyama, akan hakurin da suka yi, in har sun yi hakurin dominsa ne sun tsarkake shi.**

**In kaga wadannan ma'auratan a wannan lokacin na makokin jaririnsu, sai sun yi matukar baka tausayin da nan da nan zai saka ka zubda musu hawaye.**

**Domin sun rasa duk wani karsashi na jikin dan adam, da kuzarin su na cikin gida da waje. Can zaka hango su tsakiyar makeken gadon su manne cikin jikin juna, suna faman sauke ajiyar zuciya ba mai iya baiwa dan uwansa baki. Ba mijin ba, ba kuma matar ba, ba mai iya lallashin dan uwansa koda da kalmar “sannu” ta fatar baki ne. Wannan ya faru bayan an sallami Safiyyah daga gadon asibiti.**

**Babban bacin ransa yadda Mama dasu Ya Zubaida duk suka yi shakulatin bangaro dasu. Abun yayi matukar bashi mamaki da tsoro, bai yi zaton kiyayyarsu da Sophie ta kai haka ba, tunda in akan haihuwa ne ai gashi ta haifa musu Allah ne bai barshi ba. Tun daga lokacin ya fahimci kiyayyarsu da Sophie maras dalili ce, amma ya zaiyi?**

**Abun ya tsaye masa a rai kwarai. Ya san tun fil azal jinin Mama bai hadu dana Sophie ba, amma bai taba tunanin**

**abun ya rikide zuwa tsana tsagwaro irin wannan ba har a gun kannensa da babbar Yayarsa, da har zata dau ciki watanni tara ta haife dan babu rai, amma su kasa ko jajanta mata su kasa zuwa su kuma kasa kiran waya wannan abun ya tsaye masa a rai fiyeda zatonsu.**

**Abinda shi bai sani ba, tun daga lokacin da Safiyyah ta yanke shawarar yin Dashen haihuwa saboda gorinsu da tsangwamarsu, daga lokacinne kuma ta samu rashin son da suke yi mata ya rikide ya kara matsayi zuwa tsagwaron tsana, dama kuma sun sha alwashin koda ta haifi dan da rai tunda ta hanyar IVF ne ta samu cikinsa bazasu taba rika mata shi a matsayin Da kamar sauran 'ya'yansu kuma jikokin Baba Bello ba. Saidai ta kai Dandume su Alaramma su goya mata.**

**Bai manta da lokacin da ya kira Mama ba, tun suna asibitin da Safiyyah ta haihu kafin a sallameta, ya gaya mata**

**Safiyyah ta sauka, amma yaron ko shurawa bai yi ba.**

**Yasa hankaci ya tsane idanunsa ba tareda Mama ta san idonsa ruwa yake fiddawa ba, budar bakin Mama sai cewa tayi, “yo daman wannan dan nata irin sauran ‘ya’yan mutane ne da za’a zaci dole zai rayu? Dasa mata shi fa akayi ta karfi da yaji, to meye abun mamaki ko damuwa don ya zo babu rai?**

**Shin in tambayeku; ku duka kaida Safiyyahr, wai ana yiwa Ubangiji dole ne akan abinda bai ga damar bayarwa ba? Matarnan taka Safiyyah ‘juya’ ce Baffa, na kara fadi gaskiya juya ce, ku yarda ko kada ku yarda kuma ya rage naku.**

**Da zata haihu da tuni ta haihu kamar yadda kowacce mace ke haihuwa *naturally*. Idan ka sake yarda aka yi Dashen haihuwar Da da maniyyinka Baffa Allah ya isa ban yafe maka ba!**

**Tunda dai mata masu haihuwar nan ta gaske ba karewa suka yi a duniya ba!”.**

**Wannan maganar ba karamin firgita shi da gigita shi ta yi ba, da sauri ya cire wayar a kunnensa ya duba yana tantamar anya Mamansa Haj. Fatu ce wannan? Kodai *wrong number* ya kira?**

**Sai a lokacin ma ya tuna cewa ai ko sau daya Mama Fatu tun samun cikin Safiyyah haka siddan bata taba kiransu tace Allah ya inganta ba, ko Allah ya sauki Safiyyah lafiya, a lokacin da take goyon cikin.**

**Ance ba'a fushi da iyaye, amma hakika Zayyan ransa ya sosu sosai da attitude din mahaifiyarsa, abunda Mama Fatu tayi ga iyalinsa bai taba zaton uwa zata yi shi ga dan data haifa ba. Har hakan yasa ya dan dauke kafa daga Katsina, na dan wani lokaci.**

**Ya maida hankali ga taya su Sabah kula da lafiyar Sophie, su su kula da ita daga safe zuwa dare, shikuma ya yi nasa jegon daga dare zuwa safe.**

**A lokacin da Sophie take jegonnan ne kuma ya fahimci wani abu a halittarsa, wato jikinsa baida jimirin hakuri da rashin matarsa na lokaci mai tsaho.**

**Kusan kullum Safiyyah na barci irinna masu jego, shi kuma yana fama da shan ruwan kanwa, domin kwantar da sha'awarsa ta da namiji, kwarai ya kan gaza hakuri da ita cikin dare, baya kuma son ketare iyakar Ubangiji don har lokacin jinin biki Safiyyah take yi.**

**Ga Safiyyah da kunya, ire-iren hanyoyin nan na kwantar da hankalin miji a yayin biki ko al'ada nauyinsu take ji, wani irin nauyi abun yake yi mata, sosai take jin kunya in ya nuna mata irin abubuwan da yake so tayi masa wadanda su kadai zasu iya kwantar da hankalinsa, duk kokarinsa na fahimtar da ita shida ita babu sauran kunya ta wannan fannin, shekara goma ba wasa ba, ta bude idonta suyi irin rayuwar data dace dasu amma Safiyyah kunya da nauyi da gidadanci**

**basa barinta, irin dai *upbringing* na gidan manya data riga samu da kuma rashin *good socialization* da zai bata damar samun *exposure* akan kula da miji, ko irin 'yan karance-karancennan na zamani da ake daukar ilmin rayuwar aure a cikinsu Safiyyah bata yi. Kaidai barta a karance-karancen da zai zurfafa ilmin ta na Architecture.**

**Ganin karatun hikayoyin soyayyah take a matsayin bata lokaci ko rashin tarbiyyah. *Not because she doesn't love him.* Amma ta gaza sanin hanyoyin kula da bukatunshi na aure yadda ya kamata, alhalin karshen duk wani so da soyayyarta ta diya mace a duniya tasan na mijinta Zayyan Rafindadi ne.**

**A'ah ita dabi'arta na kunya, russunar da ido, da kana'a, *nature* dinta ne da Allah ya halicceta dasu tun fil azal, kunya da kawaici da rashin zaqewa akan *sexual relationship* dinsu. Komai shi yake yi a gadon aurensu. Ita saidai ya barta**

**dasu rufe ido da ji masa kunya, da kiran sunansa. Wannan ba zai zamo abun mamaki ba, in aka yi la'akari da irin (decent upbringing) din da Safiyyah ta samu a gida.**

**Har Sophie ta yada wanka Zayyan bai je Katsina ba, ya kuma gama shirya surprising dinta da tarewarsu a sabon gidansu dake cikin shahararren Estate dinsa da ya kammala, wanda sai yanzu Allah yayi kammaluwarshi, watau SUNSET ESTATE, Estate dinsu shida Safiyyah dake GUZAPE. A ranar data yada wanka wato ranar da ta kwana 40 da haihuwa ya shirya komawarsu gidan.**

**Cikin ikon Allah a ranar sai ga mahaifinta Malam Usman da kansa a gidansu ranar da suke shirye-shiryen tashi. Haroun ya kawo shi har Abuja tun daga Dandume, a motar Haroun din.**

**Nan suka shiga hidima da bakuntar babban bakonsu Malam, Zayyan da Safiyyah da su Sabah kowa hidima yake**

**da zuwan Malam, su dora wannan tukunya su sauke wannan, ana wadata malam da cimaka ta alfarma. Ya wuni sur tare dasu cikin kauna da soyayyahr Uba mai girma, ya yi musu nasiha da wa'azi sosai akan muhimmancin karbar jarrabawar Ubangiji kowacce iri ce, komai dacin ta, da ribar dake cikin hakan watarana.**

**Ya tunasar dasu tanadin da Ubangiji yayiwa iyayen da suka haifi da ya koma. Tare dashi aka tare ranar da yamma SUNSET ESTATE. Ya kwana tare dasu a sabon gidan a 'guest wing' Haroun kuma a hotel ya kwana, kusan kwanan zaune sukayi ranar suka raba dare a falon Safiyyah shida Zayyan da Safiyyah, yana mai basu sirrin addu'oin neman biyan bukata, abinda ya tadowa Zayyan kewar Baba Bello. Suka kasa tafiya suje su kwanta har asubah suna like da Mallam.**

**Zayyan ya kara jin kansa maraya sosai da soyayyar da Malam kema**

**Safiyyah, sai yanzu yafi jin kewar Baba Bello, ya san da Baba yana raye da abubwan dake faruwa da yawa basu faru ba, da tuni shi da Safiyyah sun ga gata a wannan haihuwar tasu, da kauna da tattali, a wannan lokacin da ba abunda suka fi bukata fiyeda kaunar iyaye da *support* dinsu.**

**Tabbas da Baba Bello na raye, ba zai watsar masa da iyali yadda Mama tayi ba, alhalin tana ikirarin tana sonsa tana kuma kaunarsa, a matsayin tilon dan data haifa namiji ta kasa taya shi son iyalinsa. Sai yaji idanunsa sun kawo ruwa da hamma a lokaci guda, har Malam ya lura yace su tashi su je su kwanta haka.**

**Da malam zai koma a washegari yace tunda Safiyyah ta yada wanka, ta kuma samu lafiya zai wuce da Sabah da Rayyah Dandume.**

**Karon ta na farko da sake haduwa da Haroun kenan, tun bayan aurenta da yazo washegari daukar Malam zasu wuce.**

**Gabadaya Haroun din Malam ya canza mata, ya zama babban mutum, Haroun ya samu cigaba sosai ta kowanne fanni na rayuwarsa, harkar danyen man fetur yake yi yanzu da 'Dangote Refinery', saboda abinda ya karanta kenan a jami'ar Maiduguri wato (Petro-chemical Engineering).**

**Bayan gaisuwarta da Haroun ya amsa ya kuma yi mata ta'aziyyah bai bar wata kalma ta kara shiga tsakaninsu ba. Bai ko kalleta ba, abin ya tsaye mata don kuwa Haroun a can baya yafi kowa shiga sha'aninta ita ke basar dashi. Sanda akayi aurenta kuma ya koma Nsukka yana hada kwalin karatunsa na biyu kuma tun bayan aurenta in zata iya tunawa Haroun bai taba kiranta a waya ko sau daya ba.**

**Al'amarinta da Yayanta Ridhwan (Yaya Shaikh) shi yafi komai bata mamaki akan na Haroun din Ammi, don in Haroun kishi yake tayi aure ta barshi, alhalin an san yana sonta tun tana**

**karama, itama kuma ta san yana sonata koda bai taba furta mata ba. To Yaya Shaikh kuma fa?**

**Kalmar so ko kwalli daya bata taba gittawa a tsakaninta dashi ba. Gara Haroun zata ce hatta Ammi ta sha gaya mata son ta yake yi, tun tana karama, amma yana kallon kansa a wanda bai isa ya aureta din ba, kasancewasa almajiri ga Mallam.**

**A wannan zuwan da Malam yayi ne yake gaya mata cewa anyi auren Yaya Sheikh a Doha (Qatar), ya auri wata Shuwa Arab haifaffiyar Maiduguri da suka hadu a karatu mai suna Assafe.**

**Da Malam yace zasu tafi tare dasu Sabah Zayyan ki yayi, don yaga yadda zaman nasu ya zamewa Safiyyah abin debe kewa, bata shiga damuwa da tunani saboda kullum suna gefenta suna kwasarta da hirar Ammi, sai ya shigo falon suke musu sallama su shiga dakinsu data basu. Don haka zamansu tare da ita**

**ya taimaka ainun wajen dawowar walwalarta.**

**Sai ya roki Malam alfarmar ya bar su Sabah su cigaba da zama tare dasu zuwa bayan sallah, don a lokacin an kusa shiga watan Ramadan saura sati guda wata mai alfarma ya kama.**

**Da kyar Malam ya yarda ya barsu, amma yace sallah da kwana uku lallai-lallai ya gansu sun dawo Dandume.**

**Malam da Haroun suka kama hanyar komawa Dandume washegari.**

**Kulawar mijin kwarai irin Arch. Zayyan Bello Rafindadi, da addu'ar *caring* iyaye masu riko da addini irin nata, sun taimaka matuka gaya wajen dawowar nutsuwar Safiyyah, bayan rashin IVF babyn da suka yi. A kullum yana karfafata da cewa "data haihu, da bata haihu ba shifa yana sonta a haka, she will forever remain his ALTER EGO,**

**sa'annan the only partner da yake son ya rayu da ita a duniyarsa da lahirarsa.**

**Ba wani abu wai shi rashin haihuwa da zaisa ya juya mata baya. Yana rokon Allah ya taya shi akan hakan. Shi ita ya aura ba abinda zata haifa masa ba da baima sanshi ba.**

**Cikin kalaman sa na koyaushe Zayyan ya kan ce mata "koda zasu mutu basu haihu ba, bazai taba amfani da hakan ya wulakantata ko ya goranta mata ba, ko ya juya mata baya ba wai dalilin rashin haihuwa.**

**Ire-iren kalamansa masu dadi kenan da suka taru suka farfado da Safiyyah, ta soma komawa harkokin ta na yau da kullum, bayan rasa dan da suka haifa ta hanyar Dashe (IVF).**

**A wannan gabar ne kuma bayan dawowarsu SUNSET ESTATE Zayyan ya bata gwaggawaban jari, yace ta soma business din duk da take so, duk don ta**

**kwantar da hankalinta, da kokarinsa na faranta mata, a bisa wuyar data sha wajen samun ciki da haihuwar In Vitro Fertilized Baby dinsu, wanda ya kira da suna a cikin zuciyarsa "Areef".**

******* ***** ******

**Kudin project din wani Estate da yayiwa gwamnati ne ya fito a goman karshe na watan Ramadhan, ya samu kudi masu kauri a hannunsa, aljihunsa yayi nauyi sosai. Abinki da Da nagari, ba wanda ya fara tunawa as usual idan ya samu kudi masu kauri a lokacin sai mahaifiyarsa, Mama Fatu.**

**Tuni ya manta da bacin ran da Mama ta saka shi a ciki watanni kadan baya da suka gabata, don shi duk wata nasararsa a rayuwa, yana fara dangantata ne da iyayensa.**

**Don haka sune na farko da yake tunawa idan alkhairi irin wannan ya same**

**shi. Yayi ma Baba Bello Sadaqah sannan yayiwa Mama Fatu hidima. Gashi ya jima bai je Katsina ba yayi kewar Mama. Don haka ya samu Safiyyah har daki yake gaya mata cikin farin ciki.**

**"Sophie kina ina ne? Zo daga kusa ki ji?"**

**Ta fito daga daki tana daura kallabinta, "gani nan Habiby, wani abu?"**

**Suka game a karamin falonta, da rabi-rabin runguma, saboda ya taho da sassarfa ne itama ta fito da sauri, ya riko kugunta ya zagayeta da hannayensa biyu yana murmushi irin na namijin da aljihunsa ya cika da albarka a gaban iyalinsa. Yace ma Safiyyah.**

**"Wannan sallahr so nake zan gwangwaje Mama da wani abu mai daraja, wane kaya ne na kwalliyar mata suka fi kowanne daraja?"**

**Safiyyah na murmushi ta sakalo hannayenta a wuyansa itama, tace "Gold!**

**(Zinare). Shine karshen kwalliyar mata mai daraja".**

**Yace "to Alhamdulillah. Zan sayama Mama sarka da dan kunne da zobe da warwaro na zinare don in gwangwajeta ba zatonta. Na san Mama da son kwalliya. Kudinnan dana gaya miki inata jira su fito na project din Bwari, yau sun fito cikin ikon Allah.**

**Yace "bana taba manta wata sallah ina dan shekara goma. Baba yazo bashi da kudi isasshe a hannunsa, yace iyalinshi mu hakura da kayan sallah, saboda ya samu yayi wasu abubuwan muhimmai da 'yan kudin hannunsa.**

**Mama sai tace "ai ba komai Babansu, Allah ya dada rufa mana asiri Baban Baffa.**

**Sai ta dauki sarkarta ta zinare ta siyar, tayi mana kayan sallah, ta baiwa Baba ragowar kudin tace,**

**“kayi duk hidimarka da sauran kudinnan Babansu Baffa”.**

**Tun lokacin abun ya tsaya min a rai. Don naga wani irin feeling na godiya da bazan taba mantawa ba a fuskar Baba ga Mama. Na kudurce nikuma sai na biya Mama ‘gold’ dinta duk sanda Allah ya bani gwaggwabar dama.**

**Ya rubuta cheque na kudi masu yawa ya baiwa Safiyyah wadanda har saida suka bata tsoro, yace “Sophie, so nake Mama na tayi gayu da babban Zinare, ta fito kamar tauraruwa Zahra a cikin mata a wannan sallahr”.**

**Safiyyah ta karba tana jinjinawa halarcin Zayyan akan son iyayensa, tace “amma Habiby, tare da kai zamuje mu zabo ko? Yace “a’ah ni mace ne? Ina nasan design mai kyau? Kawai kije ki zabo, sannan ki sayawa su Zahra suma duka kanana da bai kai na Mama girma**

**ba. Da kuma amaryata Sabah da kanwata ta kaina, Rayyah".**

**Nan suka zauna bisa doguwar kujera three seater, yayi mata bayanin yadda yakeson na kowa ya kasance, da sauran mutanen da zasu yiwa kayan sallah a cikin kudin bayan sakon Mama, dama duk shekara ya saba hakan, 'yan uwanshi kaf da nata, da iyayenta da nashi babu wanda baya yima kayan sallah na gani na fada. Kai hatta dan almajirin gidansu Safiyyah wani yaron dake zama gidansu yana zuwarma Ammi aike mai suna Saminu, ya shaida soyayyar Zayyan ga ahalin Safiyyah, don duk shekara bandirin shaddah baya wuceshi shima, duk sallah karama Zayyan bai mantawa dashi. Balle kuma kannenta uku, wato Sabah da Rayyah da Rayha, koda ba'a hannunsu zasu yi sallah ba ya maida yi musu kayan sallah cikin *obligations* dinsa (hakkinsa), tun bayan dawowarsu Abuja.**

**Sosai Safiyyah ta yi masa addu’ar karin budi da nasara cikin al’amuransa, tayi godiya yadda ya dace macen kwarai ta godema mijinta in yayi hidima ta bajinta irin wannan, ta kuma kara alfahari da Habiby dinta domin ya cika dan halas din da kowacce Uwa zata yi fatan haifar mai kaunarta da yi mata halarci kamarshi.**

**Baya taba iya yin dogon fushi da Mama Fatu (no matter how) yadda zata bakanta masa da halinta.**

**A kullum fatanta shine na samun ‘ya’yan da zasu yo gadon wadannan nagartattun halayen nasa, Zayyan Bello ya cika dan halas, uwa da ubanshi babu sama dasu a komai, tana addu’ar Allah ya bata ‘ya’ya daga gareshi su gado komai nasa, itama su ji kanta a tsufanta, ko ba don bata da shi ba.**

**A washegarin ranar suka je wani dankareren shagon zinare suka zabi *latest design* na *set* din wani *white gold* saukar jiya-jiya daga Dubai. Ya lashe miliyoyin kudin da Zayyan ya warewa Mama har da dori. Ta kuma sayawa sauran kannensa dan kunne kowacce yadda yace tayi. Sannan suka zarce kasuwar Wuse market tayi siyayyar komai da ya lissafa mata na kayan sallar jama'arsu, karkashin rakiyar kannenta su Rayyah, kaya ta zabowa su Zaitoon na gani na fada, masu tsada da quality, ta hada ma Mama da saitin turarukan *(Aventus for Her)* da ya taba gaya mata cewa dashi kadai Mama Fatu take amfani a matsayin nata neman albarkar, ta sayi wani tsadaddden akwati dan karami mai kyau, ta zauna ta jera turarukan nan da saitin (white gold) din a cikin akwatin gwanin ban sha'awa sukayi kyau a cikinsa. Kai**

**kace wata yarinya budurwa za'a kaiwa toshin sallah.**

**Sannan ta siyowa dukkan kannenshi da kannenta kaya kamar yadda ya tsara.**

**Da Zayyan ya dawo gida ta nuna masa sayayyar duka tayi masa bayanin na kowa, yayi murna sosai da ganin sakon Mama da kannenshi, ya jinjina ma fasaharta da iya zaben design din zinare. Amma yana bude na su Sabah ya dauki atamfar yana juyawa a hannun shi, ko daga kalarta da rashin nauyinta ya san bata fi atamfar dubu takwas ba, ya dubi Sophie sama da kasa ya hade rai yace.**

**"Safiyya menene haka? Me kike nufi da hakan?"**

**Hankalinta ya tashi, ta dauka wani abu ne tayi masa ba daidai ba, sai taji yace yanzu don me zaki siyowa su Sabah**

**kaya masu arha, su Hatoon ki siyo Swiss laces masu tsada, shin akwai bambamci tsakaninsu ne a gurina? Ban ji dadin abinnan da kika yi ba ko kadan, baki kyauta min ba".**

**Sai ta soma bashi hakuri, tace "ba haka bane Habiby, kudin ne sunyi kasa sosai, sai naga cewa su Zahra yafi dacewa da wannan, su din kannenka ne da kuke ciki daya, hakkinka ne ka yi musu komai yanzu, musamman da hakkinsu kamar a wuyanka yake, su Sabah kuwa Ihsani ne tsakaninku wanda bai zame maka dole ba".**

**Cikin takaicin kalamanta yace "sannu Mrs. Right, Gwanin na iya sarkin iyawa, toh canjin da kika dawo mun dashi me zanyi dashi? Idan har na isa dake ki koma kasuwar nan, abinda kikayi wa su Hatoon, shi nake so inga anyi wa su Sabah…".**

**Dolenta suka koma kasuwa washegari aka sake siyo kayansu Sabah, don ransa ya baci sosai a ranar, ya dauke mata wuta da wannan abinda tayi, har saida ta gyara kuskurenta, ta kawo ta nuna masa ta bashi hakuri. Sannan ya sauko, ta hadawa kowa nashi aka aika kayan Katsina. Infact duk kannensa da aka kai musu kayan sun yaba, kowa yayi murna ana ta bugo waya ana yima Yaya Baffa godiya don sun dauka shi da kansa yaje ya sayo masu.**

**Mama kam kuka ta saka, tace wai yau Baffa ya tuna mata Baba Bello, komai Baba zai saya mata sai ya zabo na kerewa sa'a, don ya san ta da son *special* abu da basu cika gari ba, Mama tun asalinta mace ce mai son gayu da kashe kala, tana matukar son kayan ado na yayi, tana harka ta jiki sosai da manyan matan 'yan bokon Katsina, saboda farin jinin Baba Bello.**

**Da sallah tazo, Zayyan da Safiyyah dasu Sabah suka yi shiri suka wuce Katsina don halartar shagalin bikin sallah kamar yadda mafi akasarin mazauna birnin tarayyah ke yin sallah a garuruwansu na haihuwa.**

**Gidan marigayi Prof. Bello Rafindadi gida ne da ake yin hidimar abinci ta alfarma duk ranar sallah, gate dinsu a bude yake. Wannan ya shiga wannan ya fita. Ana dafa abinci kala-kala ana bayarwa ga baki da makwabta. Haka ake yi duk sallah tun Baba Bello yana raye. To yau ma hakan ce ta kasance a gidan.**

**Ya kasance a kowanne washegarin sallah Mama Fatu tana gayyatar matan abokan Baba da kawayenta, suzo gidanta a ci a sha da cimaka ta alfarma da snacks, su wuni sur har yamma suna hira, zaki gansu duka hamshakan mata ne kusan su**

**goma a falon Mama, ana hira ana nishadi, to ko bayan rasuwarshi Haj. Fatu ta cigaba da al'adar tata, ta gayyato mutanenta ranar sallah.**

**Wannan shekarar ma kamar ko wacce, kawayen Mama sun zo harda matar VC mai ci a yanzu na jami'ar Umaru Musa 'Yar adua, Safiyyah tazo falon ita da kannenta zasu yiwa mutanen Mama gaisuwar sallah, Sophie ta sha 'swiss lace' dinta 'purple' me kyau, kannenta Sabah da Rayyah dake biye bayanta sun sako kayan da Zayyan ya siya musu na sallah iri daya sak da na yaran Mama wato su Hatoon, su Sabah sun yi kwalliyar sallah da kayan ne saboda Uncle Zayyan yana gidan, suna so su nuna mishi godiyarsu, ta hanyar saka kayan.**

**Don yace dasu da yamma in sha Allah idan ya dawo daga cikin gari za'a yi**

**(family picture) harda su kafin ya maidasu Dandume gobe kamar yadda ya alqawartawa Malam. Idan su Zahra da Zaitoon sun iso daga gidajensu. Shiyasa suka saka kayan ba tareda sun kawo tunanin komai a ran su ba.**

**Suna shiga falon Mama tayi arba dasu, ta kalli kayan dake jikinsu, nan da nan annurin fuskarta ya dauke kaman an aiko mata da saqon mutuwa. Tana tozali da kayan jikinsu Sabah ta danna ashar a zuciyarta, tace a ranta lallai ma Safiyyah da take rainawa ta bari tayi kauri da yawa, ta samu Baffa da yawa, me Safiyyah ke nufi na sakawa kauyawan kannenta kaya irin nasu Hatoon?**

**Haka suka karaso suka gaishe da Mama da kawayenta Mama na zabga musu harara daga su har Safiyyah din. Hajiya Yabi kawar Mama ta lura da irin**

**kallon da Mama ke musu sai kawai ta bude baki tace.**

**"Wai ni kam Haj. Fatu, Safiyyah har yanzu bata haihu ba ko?"**

**A gaban kawayenta Mama tace "tayani tambaya, shiru, har yanzu, tamkar Malam yaci shirwa". Haj. Yabi ta ce "kuma kuke zaune haka baku tashi tsaye akai ba? A can kan tudu layin gidan iyaye na akwai wani mai bada maganin haihuwa, maganinshi kaifiyyan, in kunaso zan karbo mata".**

**Sai ta kalli Safiyyah wadda hankalinta ya soma tashi ranta kuma ya soma baci da jin zancen da suke yi a kanta, ai har abada ba ita ba sake neman haihuwa tawata hanyar balle ta hanyar malaman tsubbu, ta riga ta tuba wa Allah da Habibiy dinta, tace bazata sake ba. Haj. Yabi tace.**

**“Diyata Safiyyah ina fatan zaki sha maganin in an amso, don magani ne me tsada. Kar na karba kizo baki sha ba”.**

**Safiyya ta gyada kai kawai amma ko motsi da bakinta ta kasa. Mama ta zucciya da banzan data yi musu, ta daka mata tsawa a cikin mutane tace “baki ji ne ana miki magana kinyi shiru, kar ta kashe kudinta a banza a wofi ta karbo miki maganin baki sha ba.**

**Ni ban ma cika son harkar maganin gargajiya ba Haj. Yabi, nafi yarda da asibiti, amma tunda na matsu na ga diyan Baffa gara a jarraba can din, ba’a san inda za’a dace ba, tunda anyi na asibitin duk ba nasara”.**

**Duk sauran matan suka ce “exactly, gara a jarraba na gargajiya”.**

**Baki daya falon sai ya karade da zancen rashin haihuwar Safiyyah har**

**tsayin shekara goma da aure, kannen sa daga mai biyu sai mai uku, kowacce na tofa abinda take tunanin shi ya hana Safiyyah haihuwa, har da masu cewa ko PCOS gareta, don mafi akasari shi yake hana mata haihuwa yanzu.**

**Safiyyah da kannenta duk sai sukayi jigum-jigum a zaune, suka rasa abinda ke musu dadi, ba zaginta ake ba amma hakan fallasa ne da gori a fakaice, suka rasa abunda zasu ce, duk Safiyya ta tsargu da kanta, taji kamar tayi wani gagarumin laifi ko abun kunya, wanda al'umma ta kasa yi mata uzurinsa, wani irin kuka na takaici ya taso mata.**

**Sabah ta fahimci hakan, tayi maza ta kama hannunta suka mike suka bar falon, uffan basu ce ba.**

**Suna fita Hajiya Yabi ta dubi Mama cikin damuwa tace,**

**“ina fatan dai ba maganar da nayi bace ta bata ran surukar tamu?”**

**Mama tace “oho mata, ita ta sani, daga abun kirki? Yarinya sai kafirin zurfin ciki da nuku-nuku, gata da sumumu-kasau irin nasu na ‘ya’yan Alarammomi da ka kan rasa gane zuciyarsu”.**

**Fitarsu harabar gidan suka ci karo da shi yana kokarin shigowa da hancin motarsa bakar ‘Ford Mustang,’ Arch. Zayyan ya sha adon sallah masha Allah dashi cikin farar shaddah bugaggiyar Wagambari babbar, bugun hannu, ba karamin kyau da kwarjini da kamala shigar yau ta kara masa ba. ta kuma kara fiddo zahirin kuruciyarsa ainun.**

**Da annuri sosai ya shigo gidan, amma yana ganin fuskarta ya gano akwai abunda ya faru da ya canza *mood* dinta. Suna tsaye a kofar shiga babban falon**

**gidan itada Sabah. Ya adana motar a *parking lot* na gidansu a nitse, bai fito ba ya sauke glass na barin da yake zaune, sai ya yafitota da hannunsa, yace.**

**"Sabah, ku ara min Yaya Safiyyah mana, ku shiga gida zan ganta, gata nan zuwa yanzu".**

**Sabah da Rayyah har suna hada baki wajen cewa "Toh! Uncle Zayyan". Suka juya zuwa cikin gida.**

**Ganin Safiyyah taki motsawa daga inda take tsaye bayan wucewar su Sabah ciki, sai ya fito ya kama hannunta, dole ta bishi kamar rakumi da akala zuwa motar, ya bude suka shiga gidan gaban motar ya rufe, dama glassanta duka masu duhu ne (tinted), motar tana kunne, don haka AC na aiki. Ga kamshin 'Car fresh' din motar mai dadin kamshi da ya hade da kamshin turaren jikin Zayyan na mazan da suka amsa sunansu (Ultraviolet*)*, su suka hadu**

**suka dawo da nutsuwa da salama a zuciyar matarsa Safiyyah, ta jingina kanta a jikin kujerar bayanta, ta hau sauke ajiyar zuciya a jejjere, ba tareda ta ko san tana yi ba.**

**A hankali Zayyan ya mika hannayenshi biyu ya rungomota jikinsa, bakinshi a kasan wuyanta ya sumbaceta lightly, yace.**

**"Sophie yaya akayi ne? Wani abu ya faru da bana nan ne? Na ganki *moody*".**

**Safiyyah tayi shiru, haka kawai taji kwalla na kara ciko mata, tace "Habiby, ina so in haihu ne, kuma da wuri!" Yace "Yaa Subhanallah! Ita haihuwar nan ba'a hutawa da yin ta? Tukunnama yaushe aka gama jegonta? Kuma shin me ya kawo zancenta?"**

**Daga Safiyyah babu amsa, sai ma idonta daya karasa cikowa taf! Da hawaye. Kiris suke jira su sauka kan kuncinta.**

**Zayyan yayi-yayi ta gaya masa abinda ya kawo zancen haihuwa amma Safiyyah ta ki. Kada ya zama cewa ko ta kai karar Mama da kawayenta wajensa ne.**

**A karshema da ya dameta da tambaya sai ta kifa kai a kirjinsa ta fashe da kuka mai cin rai.**

**Bai iya yin komai ba ko hanata kukan a wannan lokacin, banda ya rungumeta cikin kirjinsa tsam-tsam, yana shafa bayanta a hankali cikin lallashi. Ya kuma barta tayi kukanta ma'ishi, yana magana cikin lallashi, kauna da soyayyah masu yawan gaske, wadda ta bayyana kanta a zuciya da *tone* din furucinsa, Zayyan yace.**

**“Ki kara hakuri kinji Safiyyah, haihuwa da samun ‘ya’ya duka lokaci ne, in kuma Allah bai ga damar bamu ba…. inaso ki sawa ranki WANI HANIN GA ALLAH BAIWA ne”.**

**Ya fahimci an mata gorin haihuwa ne *as usual*. Amma kowanene bai kyauta masa ba suna cikin farin cikin ranar sallah, ranar celebration din musulmi. Sai ya kira Sabah a waya yace “ta robar, me ya faru ne da Sophie da bana nan? Kunje wani wuri ne an bata mata rai?”**

**Yasan Rayyah ko kusa bazata fada masa ba, don zurfin cikinta irinna Safiyyah ne, kuma bata da yawan magana, amma Sabah tsaf zai ji komai, har abinda bai tambaya ba, don tasu tazo daya sosai.**

**Sabah tace, “kawai-kawai, daga munzo falon Mama mun sameta da kawayenta mukayi musu gaisuwar sallah,**

**shine wata mata tayi mata zancen haihuwa, nan aka fara zancen rashin haihuwarta, hadda cewa za'a karbo mata maganin gargajiya wajen mai bada maganin haihuwa".**

**Baki daya Zayyan ya rikice, ransa kuma ya baci, don ya tsani a kuma zancen zuwa gun malamai karbo maganin haihuwa, yace "wanene da wannan maganar?" Sabah tace "oho bansanta ba, amma tana zaune a gefen Mama, wata fara mai jiki haka". Yace "Maman, me tace toh?"**

**Da yake Sabah bata da tsoro sai tace "ba abunda Mama tace, illa ma cewa tayi ta tabbata ta sha maganin da matar zata karbo mata don kudi me yawa za'a saka a karbo. Tace kuma itama bata yarda da maganin gargajiya ba, kawai don ta matsu taga diyoyinka ne".**

**Zayyan sai ya rasa me zai ce ma. Amma ransa yafi na Sophie baci. Karshe ya kashe wayar bayan ya gama sauraron Sabah, yace “toh Sophie don Allah banda bakin baki hakuri, bani da kalmar baki hakuri, amma kiyi hakuri ki kuma kara akan naki”.**

**Washegari da wuri ya daukesu zuwa Dandume, don kada a kara bata mata rai a gidansu.**

**Ya kaisu har cikin gida ya shiga ya gaida Ammi da Malam. Yayi musu godiyar aron ‘yammatan gidan da aka basu na lokaci mai tsaho.**

**Bai jima sosai ba ya fito yace ma Safiyyah ta kwana da Ammi, sai gobe zai dawo ya dauketa su wuce Abuja.**

**Ammi kam ta san halin yaranta ta iya karantarsu su duka, da ganinsu kuma ta san wani abu ya faru a Rafindadi,**

**amma dai bata ce komai ba, ta barsu a hakan. Suma basu tada zancen ba sai wanda ya shafesu.**

**Yana komawa gida ya tarar da Mama tana zaune ita kadai, mai aikinta Ankudi nata tattare mata falon da bakinta suka bata.**

**Ya shigo ya zauna a gajiye, yana ta kumburi, ya gaisheta, sai ya koma gefe yayi shiru, Mama tace "a kawo maka abinci ne?" Ya ce "a koshe nake Mama". Mai aikin na fita yace,**

**"Please Mama me ya faru tsakanin Safiyyah da mutanenki a gidannan?" Mama tayi salati ta sallame tace.**

**"Koda naji! Ai dama na san za'a rina wai an saci zanin mahaukaciya.**

**Toh Sannu ubana, nace sannu ubana da ya haifi uwata, matse bakina sai in gaya maka tunda tuhumar abinda ya**

**bata ran matarka ne ya kawo ka ba gaisheni ba.**

**Sallamamme kawai, kaje kauye an wanke ka a minjaye an baka ka shanye, an aikoka ka mun rashin kunya ko, toh ba zan fadi me ya faru ba duk yadda tace maka hakan akayi, akwai abunda zakayi ne? Ko karya ake mata ta haihu dinne?**

**Da ta haihu za'a yi mata zancen amso magani? Ka amsa ni mana, rasa kunya beran tanka?**

**Ai wallahi Baffa mu zuba ni da kai, in dai jimirinka matar ka ta fada maka abu kazo ka tuhumeni to tayi kadan, ko uwarta bata isa ba. Baffa anya kuwa lafiyarka kalau?"**

**Sai Mama ta hau matse ido tana fadin, "Safiyyah ta kai Babanta Makkah da kudinka, addu'arsa taci akanka Baffa, an janye min kai bakidaya".**

**Kawai yayi shiru, ranshi na kuna, yace "Mama haihuwar nan fa Allah ke bayarwa ba mutum ba, ba dabararshi ba.**

**Babu wanda ya janye miki ni Mama, amma Mama ki dinga yi wa Sophie uzuri akan lamarin haihuwarnan, tunda dai ba dabararta ce zata bata ba.**

**Kuma wallahi Mama ta fi ki son ta haifa miki jika, amma Mama ace bama ke ba wasu daban suna shiga cikin maganar haihuwarta saboda kin basu fuska ai bai dace ba, ina dai ce Safiyyah tayi haihuwar nan ba jimawa kowa ya shaida tana haihuwar? Allah ne yayi hukuncinsa a kai dagabaya?**

**Shin Mama wannan bai isa wanke mata zargin rashin haihuwa da gorin ta ba?".**

**Mama salatinta da sallaminta ya karu, tace "yau Baffa dani kake sa'insa**

**akan matarka, don ance za'a taimaka mata da maganin haihuwa?**

**Ai kuwa baku so zaman lafiya dani ba. Nabi haihuwar da ta yin da gudu mai kama da babu na tattake ba takalmi a kafa ta!".**

**Ganin Mama ta taso gabadaya kamar zata rufe shi da duka sai ya kwantar da kai ya koma baiwa Mama hakuri, don yaga ta hassala sosai irin yadda bai taba gani ba. Da kyar ya samu ya lallasheta amma tace masa daga yau in ya kara zuwa ya tuhumeta akan an batawa matarsa rai, sai ta yi masa bacin ran da zai dade bai manta ba.**

**Zayyan yau da kyar ya samu Mama ta hakura da fadan suka koma hirar sallama da juna, don gobe in sha Allah da safe zasu kama hanyar komawa Abuja shi da Safiyyah, kuma ya san zai jima bai zo Katsina ba.**

***** ***** ****

**Tunda suka dawo Abuja yake tattalin Safiyyah da farin cikinta. Duk abinda ya san yana faranta mata shi yake yi, duk abinda ya san yana bata mata rai ya nesantata da shi.**

**Har wani dan *outing* ya tsirar musu fita yanzu kullum da daddare suje *eateries* ko shawarma *joint* daban-daban, girki kuwa Safiyyah iya cikinsu take yi su biyu ma'aikatan gidan su suke yin nasu. Ni dai mai rubutu! Nan kusa ban ga mace 'yar gatan miji wadda miji ya gatanta ya ke tattali don ya mantar da ita matsalar rashin haihuwa, sannan ya girmama matsayinta a zuciyarshi duk da haka, wato duk da rashin haihuwar, irin Mrs. Safiyyah Rafindadi ba.**

**Yammacin wata Lahadi ya dawo gidansa bayan motarsa shaqare da cefane**

**da *provision* dinsu yadda ya saba duk karshen wata, Safiyyah ya samu tayi daidai da takardun zanenshi akan gado wai tana zane, ko sallamarshi kanta a duke ta amsa ba tareda ta dago ba, wai kada tayi kuskure cikin zanen da take yi, don a lokacin *idea* din zanen ke tuttudowa a cikin kanta.**

**Ya cire bakar babbar rigarshi ta bakin yadin voile din filtex ya ajiye a gefenta, yayi mata duban rahma yace.**

**"Lallai ma Sophie, wato zane kike shiyasa ko kallo ban isheki ba, balle in saka ran zaki mike kiyi welcoming dina?"**

**Still bata dago ba sai 'yar dariya data yi, ta cigaba da Zanenta bilhaqqi, don IDEA da hikimar zane sun cika kwakwalwarta a daidai wannan lokacin, so kawai take ta juyesu akan takarda don kada su gudu.**

**"Afuwan Habiby, Afuwan kaji? Amma don Allah kada ka katseni".**

**Zayyan ya rasa me take zanawa haka da har ta kasa bashi attention dinta ko yaya, ya karaso gabanta ya tsugunna yana leka zanen, ya dora hannu saman bayanta cikin wata irin siga ta kulawar miji zuwa ga matar da yake matukar so.**

**"To ko zan iya sanin me kike zanawa haka? Arch. Safiyyah Rafindadi? Na ga kamar ba gida ba, ba kuma Estate ba".**

**Sa a lokacin ta dago da murmushi tana kallon sassanyar fuskarshi, da kwantaccen sajensa ya kara ma fuskar kwarjini, fuskar da bata taba gajiya da kalla da sajenda bata gajiya da shafowa da hannunta koyaushe. Yanzunma haka ta kai hannu ta shafi sajen nasa with so much love, tace.**

**"Habiby yau tsegumi kakeso? To ba wani abu bane nake zanawa irin naka ba,**

**ko irin wanda ka sani, ni yau "Ultra-Modern Market" ce nake zanawa irin ta turawa.**

**Ka tuna sanda muka yi tafiyar nan zuwa conference din "Ranar Masu Zane ta Duniya (World Architecture Day) da aka gayyace ka a birnin Berlin?" Muka ga kasuwar nan ta zamani harka ce min ta burge ka? Da zaka iya da ka zana ta?**

**To tun lokacin abun na raina, ina jiran ranar da zan samu nutsuwa in kwaikwayeta in zana.**

**To tsarin ta na dauka yanzu nake nawa zanen a kansa".**

**Da admiration sosai yake kallon zanen nata yana mamaki, kodayake in dai Sophiensa ce ai bai kamata yayi mamaki ba, in dai akan hikimar zane ne, in bata fishi ba, to zasu yi kunnen Doki, duk da yana gaba da ita a kwalin karatu.**

**Ya shiga tattara takardun wuri guda yana turesu gefe yana fadin.**

**“Ko kina sane da cewa kuma yau ce ranar cin abincin Zayyan ta duniya? It’s my lunch time! Yanzu dai ayi hakuri da zanennan a kawomin abinci, yunwa sosai nake ji a duniya, in na gama kuma a dumama min shimfida irin dumamawar da aka dade ba’a yi min ba.**

**Baby, na rasa gane kan ki tun *last week* kike *avoiding* dina cikin dabara”.**

**Murmushi tayi, don ta gane me yake nufi, ta dauki kayan zanen da takardun ta kai daya dakin ta adana su ta dawo. Kuma daga lokacin ta manta da zancen sabgar zanen kasuwa ta shiga hidimar hadawa Habibinta abinci, mai rai da lafiya wanda ta tabbatar zai gamsar da shi.**

**Lafiya kalau suka ci abincin dare tare, tana shiga toilet da zummar tayi wanka, sai taga isowar bakon watanta.**

**Tsaki tayi, daga haka ta soma kuncin rai ita kadai, sau tari hakan ce**

**take kasancewa da ita duk sanda taga isowar period dinta, ta shiga kunci kenan, tunda alama ce ta cewa ciki dai bai samu ba har yanzu.**

**Haka tayi wankan cikin dacin rai da bacin rai mai tsanani, domin ta saka rai, dama kuma in period dinta ya kusa, sau da dama *behaviour* dinta ya kan dan canza, ta zama 'moody'. Shi bai san dalili ba amma a satinnan ya lura ta rage shige masa, kuma tana kakkauce ma haduwarsu a shimfida. Ashe dalilin duk wannan ne, period ne ya kusa yin sallama.**

**Ta fito daga wankan kenan ta ganshi kwance a gadonsu daga shi sai shorts, yayi dai-dai a tsakiyar gado irinna jiran isowar uwargida yana waya, sai kawai taji ranta n abaci, aikin Habiby kenan soyayya da iya romance amma bai damu da haihuwa ba, Safiyyah ta fada a ranta. Daga yadda yake wayar (with respect) ta fahimci shi da Baba Murtala ne.**

**Sai ta zauna akan *stool* din mudubi tana shafa lotion a jikinta a hankali, cikin son bata masa lokaci da rashin kuzari a tare da ita. Me ke damun Sophie ne?**

**Idonsa ya kai ga saman kirjinta wanda ya ciko sosai saboda haihuwar data yi duk jikinta ya zama danye (fresh) dashi.**

**Sha'awar matar tashi da baya taba gundura da ita (duk da baya samun yadda yakeso daga gareta saboda alkunyarta) nan take tazo mashi. Gashi yanada tafiya Lagos a washegari, kan wani muhimmin project na ginin *flyover* da Baba Murtala ya samo masa kwangilar yinsa.**

**Hasali Baba Murtala aka baiwa kwangilar, amma ya barwa dan nasa, yace shi yayi madadinsa, don yana son ya shigar dashi harkar ginin *bridges* da *flyovers* bayan harkarsu da yafi sabawa da ita ta 'Real Estate'.**

**Ya gama wayar ya ajiyeta a gefensa, a lokacin ita kuma Safiyyah ta gama laqailaqan shafa man nata, ta sanya kayan barcinta masu dan kauri, tazo ta haye can kuryar gado ta kwanta, ta ja lallausar duvet ta rufe rabin jikinta.**

**Zayyan ba haka yaken son ganinta ba, don alamu ne na bazata marabceshi ba, shikuma gaskiya yau din wata sabuwar samartaka ce ta bakunceshi, jin kansa yake *at the zenith of his thirties*. Ga tafiyar da zaiyi a washegari wadda zata daukeshi kusan sati biyu babu dumin Safiyyah a gefe.**

**Yayi maza ya daga duvet din nata shima ya shige, ya mika hannu yayi musu light up. Amma da ya kai hannunshi gareta janyewa tayi kamar yasaka mata shocking, ta koma can karshen gado ta lafe abinta, tana faman kuncin rai.**

**Da matukar lallashi a cikin sautinsa da taushin muryar da ba koyaushe yake mata amfani dashi ba, Zayyan yace "kada**

**ki mun haka Sophie. I'm thirsty. Na lura fa tun shekaranjiya kike avoiding haduwarmu a gadon nan, kike min wannan ciccijewar dana kasa gane ta mecece. Ko meye dalilin wannan kuncin ran da kikeyi yanzu?"**

**Murya can kasa Safiyyah tace,**

**"Nifa babu komai".**

**Zayyan ya mirgina ya shige cikin jikin Safiyyah da azama, sosai yabi ya kanainayeta ta ko'ina ya like mata, ya ninketa bakidaya a cikin kirjinsa, yana gaya mata cikin radar jan hankalin masoyi da iya lallashin mace.**

**"Idan kika juya min baya a daren yau, komai zai iya faruwa dani Sophie, kin san ke ce kadai maganin damuwar nan tawa, daga ke banida wata.**

**Babu wani uzurinki da zan iya karba yau, sati guda kenan kina doje min, alhalin ban yi miki laifin komai ba".**

**Ya kai bakinsa saitin kunnenta yana cewa da ita cikin rada "hakurina ya kare Safiyyah, ki dubi girman Allah ki dubi darajar aure ki karbeni ko *one round* ne, haba Sophie me kike so inyi ne?"**

**Maganarsa ta karshen nan har kunya ta bata. Amma Safiyyah ko gezau, don yau wani miskilanci ne ya sameta babu gaira babu dalili, tayi kememe tayi kemadagas ta ki yarda da shi da lallashinsa. Ta kuma kasa bude baki tayi masa bayanin cewa period dinta ya zo, ya canza mood dinta, don ta san kota fada din, in dai Zayyan ne ba hakura zai yi ba, bazai fasa cewa (she should try and find another way to comfort him) ba, ita kam ta fara gajiya da nacin Zayyan, tun bayan data haihu abin nasa karuwa yake, mutum ne *very* romantic sosai.**

**Ita bata san cewa yanzu ne ta zama mace sosai a wurinsa ba, yafi samun nutsuwa da gamsuwa da ita a yanzu, fiyeda kafin ta haihu, tunda ta yada jego**

**ya koma sabon ango shikuma, ya laqe mata kamar kaska, don tafi masa gardi da zaqi yanzun.**

**Wannan ya biyo bayan kayan gyaran da Yaya Zubaina ta aiko mata na "Manzil Alwafir" dake Kaduna.**

**(Duk wasu matsaloli na aphrodisiac ko gyaran aure "Manzil Alwafir" sunada maganinsu, including treatment na cutar PCOS da sauran matsalolin da suka shafi mata don gyara matantaka da inganta rayuwar aure.**

**Manzil na aika kayansu ko'ina cikin Najeriya, za'a iya tuntubarsu ta wannan layin waya 09045065562).**

**Safiyyah kam ta karba ne gun karamar uwarta Anti Dije bayan haihuwarta tayi amfani da kayan Manzil yadda ya kamata, bata ko san amfaninsu ba, bata kuma san abinda zasu jawo mata kenan ba.**

**Yayi lallashin, yayi ban bakin, yayi ban hakurin in ma laifi yayi mata bai sani ba, amma Safiyyah ko a jikinta, ta ki bashi *access* din komai, koda kuwa na ya samu damar da zai sumbaceta ne. A karshe ma da ya fitineta da lallashin sai ta bara baki ta abinda ke cin ranta.**

**"Ni kam wai don Allah Habiby, na dauka don samun haihuwa ake wahalar yin abinnan?**

**To ni gara a daina kwata-kwata, tunda ba haihuwa zai ke sa in yi ba…..".**

**Ta fada masa hakan cikin kuncin rai, tareda kankame jikinta waje daya, har da kyallin hawaye cikin idonta da yake iya gani ta dan hasken fitilar *dim light.***

**Wannan maganar data fada ne tasa ya fusata, ransa ya baci, komai ya fita kansa, saiya janye jikinsa ya juya mata baya, yayi rub da ciki bisa cikinsa ya rungume hannuwansa a kirjinsa, domin**

**Sophie ta gama kular dashi. Zayyan ya rufe idanunsa yana yaki da zuciyarsa mai cewa ya saka karfinsa na da namiji yau a kan Sophie kawai, ta haka ne zai goge rainin da ya fahimci ya fara samun muhalli a tsakaninsu, wato ya kwaci hakkinsa kota wane hali jikin Safiyyah tunda dai Allah shaida ne kan bashi da wata matar sai ita, baida inda zai je ya sauke wannan bukatan sai gurinta. Ga tafiya ta sati har biyu a gabansa.**

**Wata zuciyar na tankwarashi da cewa "Sophie ce, His alter ego! Matsayinta ya wuce (marital rape) a gareshi, kada Allah ya nuna masa ranar da zai sakama Safiyyah karfi, don biyan bukatar ransa ko saboda hutun gangar jikinsa, yace a ransa wato lamarin mace babu abinda ya kaishi ban takaici da ban haushi wani lokacin, musamman idan kayi saken da ta san karfin soyayyarta a ranka.**

**To daga sannan ka gama shiga uku, ka gama yawo a hannunta.**

**Yace a ransa to ita Safiyyah bayan sanin *weak point* dinsa data riga tayi, cikin lamarinta na yanzu harda rashin godiya, tunda ta ina ya rage ta ko ya kuskure ma nata bukatun data kasa haihuwar, har da zata gaya masa bakar magana haka, wai tarayyar su ta aurantayya kullum bata sakawa ta haihu?**

**Wannan maganar ce tasa ya hakura, ya juya mata baya shima amma ya kasa ko runtsawa a daren har goshin asubahi.**

**A takaice Zayyan shi kadai yasan irin azabar da ya dandana shi da zuciyarsa a daren yau.**

**Amma Safiyyah ko a jikinta, tace banda sawa da yake tayi tana jika gashinta yana kakkaryewa kullum saboda yawan wanka, ita wahala abin yake bata yanzu, saboda bata yin komai cikin dadin**

**rai kamar can baya. Hankalin ta ya bar kan soyayyar miji, kacokam ya koma na soyayyar samun Dan kanta.**

**Abin ya fita kanta kwatakwata tunda bai sawa ta samu cikin haihuwa. Kamar akan dole take bashi hakkin nasa yanzu, tun bayan haihuwarta.**

**Wanda hakan ya jefa shi a damuwa da rashin samun satisfaction da ita yanzu, idan ma ta kyale shi din kenan, baya samun yadda yake so daga gareta, don ta dauke zuciyarta daga kan sexual life dinsu, ta mayar kacokam kan son haihuwa.**

**Da safe ta hada masa breakfast amma ko kallonta bai yi ba itada tebirin breakfast din nata, ya dau wanka da karin guga, ya murza hadaddiyar hular 'Tonak' a saman goshinsa, kai sai ka rantse da Allah ba shine ya kwana *begging* matarshi yana matse ciki tana jansa a kasa ba sabida yadda yabi ya daure fuskar nan tam. Ta gaisheshi, karo**

**na farko da yaki amsa gaisuwar Sophie ta safe, a tsayin shekarunsu goma da aure.**

**Bata damu ba, ta hau gyaran dakin da suka kwana tana fadi a ranta Zayyan sai da haka, in ba haka ba tsofeta zaiyi da kwarzaba irin tasa don baya gajiya, tun bata ajiye masu yi mata addu'a ba.**

**Ya dauki 'brief case' din shi ya fice, sai ta 'text messege' ya gaya mata ya kama hanyar Lagos, a takaice ya gaya mata zasu fara project din da ya gaya mata shi da Baba Murtala.**

**Bata ga text din nasa ba sai bayan ya jima da barin gidan, har ya shiga jirgi lokacin, jikinta kuma sai yayi sanyi lokacin data karanta, bata san tafiya ce dashi ba, ta kuma ga rashin kyautawarta ga Habiby dinta koda ace ba tafiya zaiyi ba, wannan ne karo na farko daya taba yi mata sallamar tafiya wani gari a waya.**

**Ta ji babu dadi har ranta, anya Zayyan ya cancanci *unfavourable***

***treatment* din da take masa a satinnan, don kawai bata jin dadin zuciyarta kan rashin haihuwa sai ta huce komai a kansa?**

**Kada dai ya kasance shaidan ne yake yi mata ingiza mai kantu, don ta zama butulu, ungrateful ga ni'imomin Ubangiji a gareta, ta zama mara godiyar Allah da rashin gode masa bias alfarmar mijin kwarai daya bata?**

**A take jikinta ya kara yin la'asar, ta yi maza ta shiga kiran layukan wayarsa, amma cikin rashin sa'a a lokacin Zayyan ya shigar da wayarsa 'flight mode' don ya shiga jirgi ha ra zarga belt, ya kashe dukkan wayoyinsa.**

**Bai kunna ba har saida ya sauka a filin jirgin Murtala Mohammed, inda ya tarar da "Seyi", direban gidan Baba Murtala kenan ya na jiran saukarshi.**

**Seyi ya dauke shi da trolly dinsa zuwa gidan Arch. Murtala Babangida**

**dake Ikoyi, da bacin ran Safiyyah fal ransa.**

****** **** ******

**Kasancewar gidan Arch. Murtala babban gida ne na zamani ginin (Bungalow) a shiyyar Ikoyi har da tankasheshen sassan baki, anan Baba Murtala yasa aka saukeshi.**

**Saida yayi sallahr azuhur yayi wanka ya huta, sannan Baba Murtala ya turo Seyi, don yayi masa jagora zuwa cikin gida wajensa.**

**Har falon da iyalin sa kadai ke shiga Baba Murtala yayi umarni ga Seyi ya kai shi.**

**Baba Murtala dai kamar ya hadiye dan nasa saboda kulawa da maraba, ya rasa ina yaka saka ina yaka aje da shi, duk sanda yazo gidan haka yake nan-nan da shi, Zayyan na shirin zama akan kilishi**

**Baba Murtala yace "zo zauna nan a gefena kaji Zayyan, Da na na kaina, kullum na ganka ji nake kamar da Bello nake tare.**

**Ka jima ba ka zo gidan naku ba, yaushe rabon ma ka zo har na manta, bana jin duk kannenka ka san su gabadaya".**

**Ya dauki waya ya kira maidakinsa Haj. Nana Aisha, wadda ita kadai ce matarsa tun ta lalle, yace da ita "Da na Zayyan ya iso. Maza a Shiryo abincin rana a kawo mana nida shi, muna karamin falona".**

**Daga nan inda suke zaune Zayyan na iya jin muryar Haj. Nana tana kwalawa daya daga cikin 'ya'yanta mata kira.**

**"Azeezah! Azeezah!"**

**Daga can nesa ya jiyo amsawar Azeezah din, da wata 'yar gayun murya ta yanga da lalaci, tace.**

**“Na’am, I am coming Mum”. (Ma’ana ina zuwa Mama).**

**Ta fito daga dakinta ta iske Maman nasu a kitchen, tana shiga Haj. Nana ta hau fada “sai ki kule a daki da waya a hannu, ki barni da aikin abinci nikadai ko, na rasa mace irinki Azeezah, komai naki kamar bana mace ba, sai kwalliyar banza da iyayin wofi kika sani, amma harkar kitchen data hankali ko oho, ni Nana Aisha ina tausayawa mai tsautsayin mijin duk da ya kwashe ki”.**

**Azeezah ta zumburo baki, kafin tayi dariya, bata dai ce komai ba. In da sabo ta saba da wannan gorin na Mum dinta. Abin haushin har Daddy haduwa suke suyi tayi mata gori. Cewa ita muna mata ce. Duk abu na matan kwarai baza’a sameta ciki ba sai chatting a waya da midnight call. Mum din tace,**

**“ki dauki abincin da na shirya daga dining ki kaiwa Daddy da bakonsa a**

**falonsa, na kai dining yace a kai musu falonsa".**

**Azeezah ta ce "toh" sannan ta juya don cika umarnin mahaifiyar tata tana cewa a ranta ko waye wannan bakon da Daddy ya kai har karamin falonsa wanda su kadai ke da access din shiga wajen.**

**Tana tafiya cikin rangaji tamkar reshen bishiya ko hawainiyar da bata son taka kasa don yanga da iya takun tafiya. Tamkar budurwar Dawisu don class da iya ado.**

**Haj. Nana tace kiyi sauri mana, kina wannan tafiyar taki kamar ta hawainiya, yace a kai da sauri. Shi da dan sa ne dan wajen marigayi Bello Rafindadi.**

**Kiyi maza kai musu, kizo ki rakani saloon Agege".**

**A bakin kofar shiga falon ta tube takalminta dauke da katon tray ta shiga falon, saida ta shiga sannan ta tuna bata yi sallama ba, tayi maza ta koma tayi**

**sallamar ciki muryarta ta 'yan gayu, don tasan kadan da aikin Baba ya dizgata gaban bakonsa, akan rashin sallama.**

**Ilai kuwa saida Baba Murtala ya ce "da baki koma kinyi sallamar nan ba Azeezah da tamu ce dani da ke".**

**Zayyan ya dago kai daga kan wayarsa yana kallon 'yar gayun yarinyar dake shigowa. Bata da tsayi can kamar Safiyyah amma tafi Sophie kakkauran jiki irinna 'yan ajebo, ya sake kallon ta karo na biyu yana tuna sanda ya santa lokacin aurensa da Sophie da suka je Rafindadi tareda Mamanta Haj. Nana lokacin bata fi shekaru goma sha biyu ba, lokacin ko kirgen dangi bata fara ba, yayi mamaki da yaga itace yau tayi wannan girman haka na farat daya?**

**Yanzu akalla zata yi shekaru ashirin da biyu, komai na budurci da hutu ya nuna a jikinta.**

**Ta shigo da tankareren tray din da gidajen manyan masu kudi kawai zaka ga irinsa, ta ajiye akan center table din dake gabansu, ta gaida shi a gajarce ko amsawa Zayyan bai iya yayi ba, sakamakon wani tunani maras tushe da ya zo ya sarkeshi a nan take.**

**Tunani ne yazo masa cewa. Ba don ba don ba, ai da ya gwada cewa Baba Murtala ya bashi auren 'yarsa Azeezah ya kara da ita, in yaso ta haifa masa Da, ya dauka ya baima Sophie ta rike ta rainar masa a matsayin nata, a huta matsalar haihuwa dake damun Sophie.**

**Abinki da namiji wanda ya fito daga gida cikin kishirwar mace, a take ransa ya kyasa masa Azeezah. Yayi ta kawata masa suffofinta.**

**Ba Azeezah ba da take zukekiyar yarinya mai class, wanke hannu ka taba, da iya gayu da takun tafiya mai jan hankalin da namiji, a wannan lokacin ko**

**wadda bata kaita komai bama Zayyan ya gani kyasawa zaiyi a ransa.**

**Saboda wawakeken gibin da Safiyyah ta bari a ransa daren jiya da yau da safe kafin ya fito daga gida.**

**Sanye take da fitted gown ta wani bakin lace mai adon ruwan gold, rigar ta bi dirin jikinta ta kwanta sosai, ta fidda duk wani tudu da kwari na jikinta, a kanta kananun kalba ne na karin gashi (attachment) wanda in ba gaya maka tayi ba bazaka taba gane cewa sakawa tayi ba, ta yi ado dashi ta dunkuleshi ta baya, wani kuma ta zubo dashi gefen fuskarta.**

**Baba Murtala ya lura da kallon 'yar shi Azeezah da Zayyan yake tayi a sace, har ta juya zata bar dakin, tana gaida shi amma tsabar yayi nisa a tunani bai ma ji gaisuwar tata ba.**

**Tunani kawai yake yana sake cewa a ransa "ba don ba don ba! Ai kawai da ya gwada neman aurenta".**

**Baba Murtala yayi murmushi yace "kanwarka kenan, marar kan gadon gidan, "Azeezah!".**

**Duk cikinsu itace sai a hankali, komai sai an kwabeta na rasa mai yasa bata taso da kan gado ba, ita ba ta fari ba ita ba auta ba.**

**Ko don ita kadai ce mace a cikinsu?"**

**Azeezah ta ciji lebe tasan mawuyaci ne dama Baba bai dizgata ba shiyasa bata so Mum ta saka ta kawo masa abinci falo musamman idan yana tare da baki.**

**Baba Murtala yayi murmushi yace "tana gaisheka" nan da nan ya shiga nutsuwarsa ya yi maza ya canza fuska ya mayar da ita ya dinke tsaf, ya amsa a gajarce kuma ciki-ciki. Azeezah bata damu ba, ta juya zuwa kofa, duk dakin ya bade da kamshin wani sassanyan turaren Humra na mata data shafa, mai sanyaya rai. Zayyan ya bita da kallo, kugunta**

**kamar zai karye don shape, sai kadawa bom-boms keyi kamar da gayya take juya jikinta.**

**"Yaa Subhanallah" inji Zayyan a zuciyarsa. Baba Murtala ya lura dan nasa ya tafi da yawa sai ya cetoshi da cewa,**

**"bisimillah Zayyan, mu ci abinci ko?**

**Muna da wuraren zuwa da yawa a yau, da abubuwan da zamu fara gabatarwa fal. Don haka ka ci abinci ka koshi ka ji ko.**

**Na gaya maka two weeks project ne, so probably zaka zauna anan Lagos har kwana goma sha hudu".**

**Zayyan ya gyada kai, ya nutsu ya maida hankalinsa ga Baban nasa, ya bude warmers din alfarma da Azeezah ta ajiye musu ya fara serving dinsu shi da Baba, kowa a faranti daban.**

**Baba Murtala ya kasa shiru da canzawar yanayinsa. Don gabadaya walwalarsa ta dauke.**

**"Zayyan are you okay? Azeezah ce fa, kanwarka ta gidannan naga kamar baka gane kanwar taka ba, last week ta kammala karatun digirinta a Cyprus ta dawo gida".**

**Zayyan yaji kunya tunda Baba ya gane kalar kallon da yakema diyarsa, a fili yace "umh" kawai, don jikinsa yayi sanyi kuma, a ransa yace "karewar hutu a kasar waje tayi karatu. To akul! Dina".**

**Suna cin abinci Baban ya shiga bashi labarin diyarsa Azeezah, a lokacin da tana kankanuwa, yace hasali duk cikin yaransa Azeezah daban ta zo, itace bata da kwakwalwar karatu sai ta giggiwa, kullum ta karshen aji take dauka a makaranta.**

**Ya samu ta gama sakandire da kyar da sidin ludayi, sai tasa rigimar ya kaita**

**waje tayi karatu don sakamakonta bai yi kyau ba, da kyar ya samu wata makarantar kudi (private university) ta dauketa a kasar Cyprus, shi yasa da ya kaita makarantar ya barta ta karanci abinda malaman jami'ar suka zaba mata (Make up Artistry) sabida kanta bai jan karatu sam.**

**Kuma da yake tana da interest akan kwalliya din tun tana karama hobby dinta ce, ta tsaya ta maida hankali ta kawo masa dan shakwa-shakwan certificate na zama professional Make-up Artist.**

**Yace komai Azeezah tayi sai an yi mata gyara, komai sai an saka ta a hanya, kuma bazata rike na yau ba gobe sai an maimaita, in ba haka ba sai an ga kuskure da wauta a ciki, ya tambayi Zayyan, shin ko ya taba ganin yarinya mai gurgun bahagon personality irin na 'yarsa Azeezah?"**

**Sai kuma yagirgiza kai, cikin alhini yace.**

**Ba don kamar ta daya da ni ba, da tabbas nace canzawa Haj. Nana ita akayi a asibiti, don dakikiya ce ta gaske Azeezah".**

**Abun ya baiwa Zayyan matukar dariya, musamman ta sigar da Baba yake bashi labarin kamar da sa'ansa yake hira, har sai da Zayyan ya murmusa, ya ce "haba dai Baba!" Yace "Allah Zayyan Azeezah halinta sai ita, ni dai nan kusa ban taba ji ko ganin yarinya mai son rayuwar jin dadi na rashin kangado da son kyale kyalen duniya irin Azeezah ba.**

**Itace ta biyun karshe a cikinsu, amma kamar diyar fari sabida tsabar wauta da rashin sanin ya kamata, duk cikin 'ya'yansa yace babu mai son duniyarta, da son rayuwar hutu da jin dadi zallah na wuce kima irin Azeezah.**

**Can Baba Murtala yace "a kullum in lamarinta ya dameni ina gaya mata bamu zo duniya don mu huta ba, babu wani jin dadi ga dan adam a wannan**

**rayuwar sama da ya bautawa Allah ya nemi abin rufin asirinsa, hutu sai a aljannah, jin dadi zai dauwama ne kadai idan ka bautawa Ubangiji da lokacinka da lafiyar daya baka. Ka tsare sallolinka.**

**Kullum nayi gabas, ita sai tayi yamma, in nayi kudu, sai tayi arewa. Kamar bani na haifeta ba. Bata gado halin kowa cikin mu ba tsakanin ni da Haj. Nana wajen sanin abinda ya kamata a rayuwa. Halinta na son kyale-kyalen duniya sai ince a rariya Azeezah ta tsinci abinta.**

**Yace daga Ashraf sai Aman sai ita. sai kuma autansu Saifullahi, suke nan yake dasu a gabansa yanzu. Babban dansa Walid ya jima da rasuwa a dalilin cutar koda, haka mai binsa mace Taqiyyah ta rasu gun haihuwa.**

**Zayyan ya muskuta cikin jinjina labarin Azeezah da mahaifinta yake bashi, a cikin yanayin sautin Baba Murtala yana nuna matukar bakin**

**cikinsa da damuwarsa akan halayen diyar tasa cikin karyewar murya irin ta mahaifin kwarai da ya damu da tarbiyyar 'ya'yansa, ya kuma tsaya ya karancesu sosai, dukkan dabi'unta yace ko kadan baya sonsu, kuma basa masa dadi a rai, ba yadda zaiyi da ita ne, ya kasa canzata, da ana sayarda halin kwarai da ko nawa ne ya saka ya sayawa Azeezah ya canza mata halayenta, sai Zayyan yace a ransa.**

**"Allah daya gari bambam kenan! Ita wannan komai nata 'opposite' din na Nana Safiyyahrsa!**

**Sophie abinda bata so kenan wato kwalliya, gayu da kyale-kyalen zamani, Safiyyah bata damu taji dadi ba, ita dai tayi ibadah, kuma ta kan ce duk wani abu da zai janyo mata idon mutane kanta, ko ya zame mata kyalkyalin da zai ja hankalin maza a kanta, ko ya janyo idon mutane gareta wanda har zaisa suyi mata kallo na biyu, bata maraba dashi.**

**Watau Safiyyah bata son ta burge kowa don a wurinta ido guba ne.**

**Komai da Baba Murtala yace halin Azeezah ne sai ya ganshi kishiyar na Safiyyah *in one way or the other*. Duk yadda ya so ya yakice tunanin Azeezah da labarinta tun a wurin hakan bai samu gareshi ba.**

**Har karanta wasikar jaki yakeyi shikadai. Yana comparing and contrasting halayen nasu. Yace Safiyyah mai kokari ce, kuma zaqaqura a harkar, karatu abin mamaki ita kuma wannnan Babanta yace dakikiya ce.**

**Safiyyah mai gudun duniya wannan mai matukar son duniya, da son jin dadin dake cikinta. Yayinda Sophie ko kadan bata damu da jin dadi ba.**

**Baudaddun halayenta da yaji daga bakin Babanta yana mai kuka dasu, shi a matsayinsa na namiji sai suka bashi sha'awa, sabida wasu exceptional**

**characteristics ne da bai saba ji ba, akwai abin so da sha'awa a cikinsu duk da haka, *is rare* a samu irinta, shi sai yaga ba matsala bane halayen nata face abin sha'awa tunda mace ce. Karewa ma su suka ja masa wani sabon attraction akan Azeezah Murtala, wanda yasa ya shiga damuwa da lamarinta, madadin yaji baya sonta ko ya tsani halayen nata. Kwalliya ai abar so ce ga Da namiji, haka yake so Sophie ta koma, mace 'yar zamani mai ji da class da gayu, amma ita kullum sai Hijabi.**

**Yayi ta tunanin yadda yaga Azeezah take twisting jikinta in tana tafiya kamar tarwada a cikin ruwa, kai kamar da gayya take juya lafiyayyun cikakkun mazaunanta suna wani girgiza cikin tafiyar da hankalin mai kallonsu.**

**Tunanin halittar Azeezah da ya samu kansa ciki ya kuma dinga yi masa dadi ne yasa bayan ya koma masaukinsa, sai kawai ya kwanta rigingine ya ki kunna**

**wayoyinsa kwata-kwata, don ma kada a katse masa tunanin da yake ciki a lokacin.**

**Yanata karfafa kansa kan me zai hana ya gwada yiwa Baba Murtala maganar ya bashi diyarshi Azeezah ya aura? Shi yana son kwalliyar, yana son kyale-kyalen nata, shine abinda ya rasa a nasa iyalin, da kuma….. Azeezah kawai ta burgeshi. Kuma ga dukkan alamu AZEEZAH MURTALA ta hada duka abubuwan da ya rasa a gidansa.**

**Safiyyah ta fado masa a rai, a lokacin da yaji kwanyarsa ta lullube da tunanin auren Azeezah, yana ta tuna jerarrun hakoranta, kissable lips dinta. Wani irin a jere ya hau sakin ajiyar zuciya ba sassautawa, yana gayawa kansa koma wane irin tunani ne ya samu damar kutsowa cikin rayuwarsa akan wata diya mace daban bayan Safiyyah a yau, Safiyyah ce sila, ita ta bada kofa, ta bashi dama, ita ta jawo masa koma menene.**

**Data watsar dashi daren jiya ya kwana da fushinta, ta barwa matan duniya shi akan titi suke daukar hankalinsa, taki alkinta masa sha'awarsa, sabida rigimarta na son wata haihuwa da bata isa ta baiwa kanta ba, karshe ta barshi *stranded* (a ragaice) bisa titi yana satar kallon 'yammata.**

**Hausawa ma sunce "sai bango ya tsage kadangare ke samun kafar shiga". Don haka kara aure da diyar Baba Murtala gareshi yanzu ba zai zama laifi ba, don kare kansa daga fadawa wani hali na daban. Shi kadai yasan yadda ya wayi gari jiya da Sophie ta juya masa baya taki tallafarsa. Sophie taki ta gane shi mai tsananin son kasancewa da mace ne, haka halittarsa take, son samu matarsa Safiyyah ta daina saka kunya irin wadda ita Safiyyah ke sakawa a tsakaninsu, tayi kokarin gyara (sexual life) dinsu, ta maida hankali a kanta fiye da komai ta hakura da batun haihuwa tunda Allah bai ga**

**damar basu ba, amma a'ah ita Sophie yanzu ba soyayyarsa ce a gabanta ba, kullum hankalinta naga kulafucin son samun Da tareda shi, ita dai ta samu haihuwa ta kowacce hanya, hankalinta ya tashi daga kan wajibinta (kula da aurenta) zuwa abinda ba wajibi ba (neman haihuwa).**

**Haihuwa idan Allah bai ga damar bata ba wa ya isa ya bata? Yayi duk iya kokarinsa akan Sophie ta yarda da hakan abu ya faskara. A wannan lokacin Arch. Zayyan Bello, ya tabbatarwa kansa cewa yanada bukatar kara aure, musamman da yake da tabbacin kowa zai aura zata bi bayan son da yake yiwa uwargidansa Safiyyah ne.**

**A duk yadda *nature* din Safiyyah yake yana son abarsa a haka, yana darajjata, yana daukaka martabar al'amarinta a duniyarsa da cikin rayuwarsa fiyeda na kowacce mace, bayan wadda ta kawo shi duniya (Mama),**

**amma yau ya tsinci kansa dumu-dumu da son kara aure bayan Safiyyah, amma ga wani hanzari; macen duk da zai aura, zata zamo masa matar biyan bukatar gangar jikinsa ne kawai, sabida ta wannan fannin Safiyyah ta gaza, amma soyayyarsa da kaunarsa har abada suna ga "stammerer Hijabhie dinsa ta gargajiya wato Arch. Safiyyah Usman Dandume".**

**Sannan kowacece Allah ya rubuta zai aura, ko da kuwa Azeezah dince ko watanta, idan ta haihu Safiyyah zai kyautarwa abinda ta haifa, in sha Allahu.**

**Wannan wani alkawari ne da Zayyan yayi da zuciyarsa yau, bayan samun kansa da sha'awar kara aure, zai haifi Da da matar ya mallakawa Sophie, in dai Dansa ne halalinsa to zai kyautar dashi ga Safiyyah. In fact, sai sun yi da wajewa/yarjejeniyar nan da kowacece Allah ya rubuta masa zai aura, kafin ya yarda ya aureta.**

**Zai fito fili ya gaya mata shi ba don rashin haihuwar matarshi ko rashin sonta ne yasa zai kara aure ba, kawai dai…. Kawai abar kaza cikin gashinta inji Zayyan, amma 'infatuation' na son kara aure ya sameshi, irin wanda ka iya faruwa da kowanne lafiyayyen Da namiji, mai cikkar lafiya da cikkar kurucciya kamarsa, ga wadatar arziki da yalwar jin dadin duniya da yake ciki a wannan lokacin, yana da damar auren mace fiye da daya, da addini ya riga ya bashi, duk son da yake yiwa Safiyyah bazai hana shi cika sunnah ba yanzu, watakila yawan son da yake mata shi yake sawa Safiyyah ke ganin yana matsa mata, soyayyarsa ta yi mata yawa, shi kuma ke sakawa take garashi yadda takeso in yazo da bukatarsa gareta kamar ta samu gare-gare abin wasan yara.**

**Ya tuna rabon da ya gaisa da Mama Fatu yau kwana biyu kenan, don haka ya kunna daya daga wayoyinsa da ba'a**

**sanshi sosai da layin ba, don ya kira Mama su gaisa, Safiyyah kam ya riga ya bata hutu bazai ko kirata ba.Amma yana kunnawa sakonta na shigowa har guda uku a jere.**

**A cikin sakonta na farko afujajan take tambayarsa saukarsa lafiya a jihar Ikko, da yanda ta damu da ya bude waya taji lafiyarsa suyi magana ko yaya ne.**

**A sakonta na biyu kuma tace "tayi regretting laifinta, tana so ya bata dama ko yaya ne in ya dawo tanaso suyi magana, ya bata dama tayi repenting. A cikin sakon ta gaya masa uzurinta na ranar 'mood swings' ne irin na zuwan al'ada (jinin haila) amma tayi nadamar yadda ta kasa yi masa bayani ko biyar dashi ta yadda zai fahimta!"**

**'I'm so SORRY Habibiyyyy!"**

**Zayyan kasa bata amsa yayi, ya kuma kasa kiranta, yana blaming dinta da duk wani hali na sha'awar Azeezah**

**daya riga ya tsinci kansa a ciki yanzu babu gaira babu dalili.**

**Ya share Safiyyah bai bata amsa ba, domin hakika ta kai shi bango har fiyeda zatonta, maza zasu iya jure kowanne irin bahagon yaren matansu amma banda (sex denial). Duk da haka shi Zayyan ya tabbatarwa kansa a kowanne hali kuma cikin kowanne yanayi sunansa Arch. Zayyan Bello, mijin Safiyyah Usman Dandume, babu abinda zai canza *title* dinnan, balle har don tayi masa wani laifi ya canza mata shi, ko ya canza matsayinta a wurinsa….**

**Kullum yana gayawa kansa ya dinga yiwa Sophie uzuri, uzuri sau saba'in kafin yayi mata hukunci da tauye hakkinshi a shimfida da take yi yanzu, tunda a can baya ai ba haka take ba (while she was in her twenties). Tsananin son haihuwa data sakawa ranta a yanzu da *frustration* na rashin samunta, shi yake ta canza halayenta daga (normal**

**behaviors) dinta daya riga ya shaida zuwa wasu halaye kala dabam, da sukasa ta fidda ranta akan kowa da komai har dashi kansa.**

**Domin a halin yanzu Safiyyah ta kallafa ranta a kan son samun Da dashi ta kuma baiwa son haihuwar muhimmanci har fiye da soyayyarsu mai tarihi da kuma rayuwar auratayyarsu.**

**Ya kira Mama ne da niyyar su gaisa kawai, don sun kwana biyu basu gaisa din ba. Mama Fatu ta amsa da farin cikin jin muryarsa, don sun kwana biyu basu yi waya ko ganin juna ba, bai je Katsina ba, Mama ta kira sunansa "Baffan Mama!" tana cewa cikin tsokana.**

**"Ni Baffan Mama ina ka shiga ne kwana biyu ko wayarka babu balle kyallinka? Ko Hakimar taka diyar Alaramma ta murza kambu, ta hanaka zuwa Katsina wannan watan kwata-kwata?"**

**Yace "haba dai Mama, haba don Allah, nifa dadina dake kenan, zargi da zato mara tushe a kan Sophie.**

**To ni bama tare ma, ina Lagos gidan Baba Murtala tana gida Abuja ita, muna wannan project din dana gaya miki zamu yi kwanaki nida Baba".**

**Sai kuma ya sassauta murya ya ce cikin lallashi.**

**"Don Allah don Annabi Mama ki dinga kyautatama Sophie zato. Mama don Allah. Ba wanda ya isa ya hanani zuwa inda kike".**

**Mama cikin gundura da zancen tace "to naji, yaushe zaka dawo daga Lagos din?" Zayyan yace "ganinan dai Mama, amma Baba yace zan jima, akalla zamu kai sati biyu anan kafin kammala project dinnan".**

**Cikin subutar baki za'ace ko zarar bunu, Zayyan ya nisa ya ce cikin rage sauti kamar mai tsoron kada wani ya ji**

**shi ya furtama Mama abinda ke ta yawo a ransa.**

**“Mama yau sai na ga yarinyar gidannan, kanwata Azeezah, ta wajen Haj. Nana Aisha, ta girma fiyeda zatona, kawai naji ta kwanta min, har naketa cewa a raina “ba don ba don ba….???”**

**Zayyan ya hadiyi miyau da kyar, sai yayi shiru kadan na wucin gadi, yua kasa karasawa. Mama tayi gyaran murya tace,**

**“ehem, ina jinka Baffa, ba don ba don ba me?”**

**Yayi ta maza yace “Na ce da sai na yi wa Baba Murtala zancenta, in ji ko bai yi mata miji ba?”.**

**Mama Fatu ta yi kabbara a ranta har kabbarar tata fito fili bata sani ba, cikin kokarin hadiye dokinta da zumudinta ga zancen, kada ya gane girman excitedness dinta, ta ce,**

**“Ina zuwa Baffa”.**

**Sai ta katse wayar tasu, ta fadi gaban Ubangiji ta fuskanci gabas ta yi sujjadah akan goshinta ta ce.**

**“Allah na gode maKa da Ka nuna min wannan ranar ina raye, ranar da alkadarin diyar Alaramma ya karye a zuciyar Baffa.**

**Yau Baffa da kansa ya ce min ya ga wata mace daban yana so bayan diyar Alaramma ba tareda na saka shi kona tursasashi ba”. Mama har ta share hawayen farin ciki da gyalenta. Ta rasa ina zata tsoma ranta don dadi da farin ciki.**

**Saida ta nutsu, sannan ta yi gyaran murya ta sake kiransa, with so much excitedness Mama ta ce,**

**“Baffa har yanzu kana kan layi?”**

**Ya ce, “Eh Mama”. Ta ce, “To ka saurareni da kyau kaji abinda zan gaya maka yanzu, maza kayi gaggawar sanar**

**da Baban naku, ina tabbatar maka yanzu ne za ka yi aure mai suna aure idan aka dace, aure na gata da mutunci, auren babban gida daya dace da kai.**

**Sauran al'amuran ka bar komai a hannuna, in dai ka gaya wa Alhajin naku ka gama naka, ko lefe ni zan hada maka komai kaji Baffa".**

**Ya yi mamakin yadda daga 'yar magana ta subutar baki Mama ta dauki zancen da matukar muhimmanci irin haka.**

**A daren da kyar Zayyan ya iya yayi barci saboda tunani, a karshe ya tabbatarwa kansa ya kuma gayawa kansa kara aure shi ne kadai solution na dukkan matsalolinsu shida Safiyyah ta kowanne bangare ya duba yaga hakan shine kadai maslaha.**

**Amma daga bangaren ita Safiyyah shin hakan zai zamo *solution* a gareta? Kuma ta wace hanya zai bi ya gaya mata**

**yau shi Zayyan ya ga wata mace daban a duniya bayan ita ya kalla sai biyu, kuma yana so zai aura ya hada da ita? Duk da cewa ba haramun zai aikata ba, kuma bai taba yi wa Safiyyah alkawarin ba zai kara aure ba, amma Hausawa suka ce, wai ido da kunya!**

**Saboda nauyin idanun Safiyyah da ya fara ji tun yanzu, tun ma kafin ya sanar da Azeezah din ko mahaifinta, sai yayi maza ya kara kashe wayarsa, gani yake yana bude baki don yin magana da Safiyyah za ta ji abinda ke binne a zuciyarsa yau, wanda yake shirin aikata mata, wato sha'awarsa ta kara aure. Don haka kashe wayoyinsa shi yafi masa komai sauki.**

**Washegari tunda sassafe wayar Mama ce ta tashe shi daga baccin da ya samu bayan ya yi sallar asubah.**

**Kuma yana dagawa ko gama gaisawa ba su yi ba, ta ce, "Baffa mu gode wa Allah, mu kara gode maSa.**

**Yanzun nan na gama magana da uwar gidan Alh. Murtala wato Hajiya Nana Aisha, na tambaye ta ko an yi wa Azeezah miji, ta ce tukunna, amma akwai yaron da take tare da shi a Cyprus kafin ta dawo.**

**Saboda haka don Allah don Annabi Baffa kada ka yi da wasa cikin maganar nan, da zafi-zafi a kan bugi karfe".**

**Shi dokin Mama a kan maganar ya fara ba shi mamaki, kamar dama a jirace ta ke da ya kyasa wata ya gaya mata?**

**Ya ce, "Mama ki bi a hankali, *I haven't decided yet*".**

**Mama ta ce, "Zancen banza da wofi kenan, ni har na saka Zubaida a fara hada lefe na alfarma, don ni wurina yanzu ne zaka yi aure na mutunci a inda ya dace**

**Baffa, kuma aure daidai class dinka da matsayinka".**

**Bai ce komai ba har Mama ta kashe wayarta. Ya ce, "Hummm! Mama kenan. Kowa in bai da kudi da *reputation* to ba mutum ba ne mai mutunci a idonta.**

**Ba wannan dalilin ne ya sa ya furta abinda yake ransa a kan Azeezah kenan ba, a'a shi ra'ayi ne da sha'awa suka zarge wuyanshi.**

**Daidai lokacin Baba Murtala ya kira shi a waya ya ce masa yana jiransa su karya kumallo.**

**A gurguje ya yi wanka ya shirya cikin ash colour yadin filtex mara kauri, ya sanya hula kalar kayan jikinsa data ciza sosai. Nan Zayyan ya fito a Zayyan dinsa, tamkar saurayi dan ashirin da bakwai ba mijin mace daya ba.**

**Ya gama feshe illahirin jikinsa da *ultraviolet* dinsa, sannan ya rufo dakinsa ya karanta addu'ar fita gida da neman sa'a sannan ya nufi cikin gidan.**

**Har addu'a Zayyan yake a ransa, Allah ya sa Azeezah ba ta falon, ko bata tashi barci ba, domin *emotions* dinsa a kanta suna kasa boyuwa in ya ganta har gashi Baba Murtala jiya ya kusa ramfo shi, watakila shiyasa ya shiga ba shi labarin rayuwarta.**

**Addu'arsa bata karbu ba, domin kuwa yana shiga falon Baban da ita ya fara yin tozali, tana zubawa Baba Murtala tea mai ganyen na’a-na’a.**

**Azeezah ta sha kwalliyar safe har ta gode Allah cikin wani ubansu combination na swiss lace da atamfar super orange and black.**

**Zuciyar Zayyan ta doka ta sake dokawa da wani sabon *infatuation* da sha’awar Azeezah, amma a hakan ya daure yasa tsahonsa ya shiga cikin falon da sallama dauke a bakinsa. Cikin dakewa da karfin halin kauda idanunsa daga gare ta.**

**Baba Murtala ya ce, “Zo daga nan gefena Zayyan mu sha tea. Ke Azeezah**

**hada masa shayin na'a-na'a ya wartsake makoshinsa".**

**Ya durkusa gefen Baba ya zauna yana gaisheshi da safiya.**

**Azeezah ta mike zata bar wajen, Baba Murtala ya ce, "Shin ke wace irin sakarya ce da kullum sai an ce ki gaida mutane sannan zaki gaishe su? Kuma shin baki ji nace ki hada masa tea irin nawa ba?"**

**A gaskiya Azeezah ta tsani yadda Baba ke dizga ta a gaban yaron nan, don ta lura wani matsayi yake da shi mai girma a gun Babansu, tunda dan Arch. Bello Rafindadi ne, wanda tun haihuwarta ta ke jinsa bakin Baba da girman abotarsu a bakin Babanta Arch. Murtala Babangida.**

**To ya za ta yi? Haka ta juyo da zummar gaishe shi, yayin da idanunta suka fada a cikin nasa. Saura kadan zuciyar Azeezah ta narke kamar yadda kitse yake narkewa in ya shiga rana.**

**Hatta kalmar gaisuwar makalewa ta yi a makoshin Azeezah Murtala, domin sai yau ne tayi ma Zayyan Bello kallo na hakika don jiya ko kallon fuskarsa bata yi ba. Duk wata jijiyar da ke cikin jikinta sai da ta saki, ta karbi kwantaccen sakon da ke cikin idanunsa zuwa gare ta, kafafunta ma rawa suka hau yi, ta shiga gaishe shi da shakakkiyar murya da dimaucewa.**

**Baba Murtala ya kara bada ita da cewa,**

**"To shayin ma wato sai na sake cewa ki hada masa karo na uku ko Azeezah?"**

**Saura kadan Azeezah ta fashe da kuka, sabida bazata iya hada wannan shayin ba. Hannunta da jikinta duka rawa suke. Zayyan ya cece ta da cewa.**

**"Kyaleta ta je Baba, ni ko Safiyyah bata hada mun shayi, da kaina nake hadawa, kyaleta zan hada da kaina Baba".**

**Tsaki Baba Murtala ya yi, yana ta korafi dai a kan halin sangartar diyar tasa, har yana cewa, yana jin tausayin duk mijin da zai kwashe ta. Domin kuwa ba haka uwarta take ba.**

**Murmushi Zayyan ya yi, beautiful serene smiles dinsa, wani tsadadden miskilin murmushi da ba koyaushe yake yin irinsa ba, ya ce.**

**"To Baba ni in rage maka dawainiya mana? Ni ina sonta a haka, ka ba ni ina so".**

**Sakatoto da baki Baba Murtala ya yi yana kallon dan nasa, kafin ya ce, "Tau? Ubanka nake dai ba Kakanka ba, balle ka maida ni abokin wasan ka, ni ba sa'an wasanka ba ne Zayyan da za ka tsokane ni.**

**Barni in sha 'tea' dina cikin dadin rai, kada ka sa ya huce min da shiriritarku". Ya daga kofin shayinsa ya kurba.**

**Zayyan ya dinga murmushi yana cewa, "In dai za ka ba ni Baba, ba zan yi maka wasa ko shiririta ba nima, ai babu irin wannan wasan tsakaninmu nida kai Baba. Uba ne da tilon Dan sa".**

**Kawai sai ya ga Baba Murtala ya daddage ya fashe da kuka.**

**Jikin Zayyan ya yi sanyi, don ya dauka zafin maganarsa Baba Murtala ya ji, amma sai Baba ya kama hannunsa ya rike yana kallonsa da kauna ido fal hawaye.**

**Ya ce, "Bar ganin ina zubda hawaye, Bello na tuno. Ya taba cewa, ba don ka yi aure da wuri ba da zai fi so ka auri daya daga cikin 'ya'yana mata don kara dankon zumuncinmu.**

**A lokacin sai na ce masa, kada ya kara irin wannan maganar kada mu taba tunanin yi muku auren hadi, wanda a karshe bata zumunci yake zama.**

**Yau da ka furta da bakinka cewa, kana son Azeezah, duk da yadda nake ta**

**kushe ta a idanunka, tun zuwanka Zayyan ban yabi halin Azeezah ko daya a kunnenka ba, ko sau daya ban fadi alkhairi akanta ba, sai hakan ya tuna min da abinda Bello ya taba ce min a kanka.**

**Ya taba ce min, yana son baudaddiyar halayyarka, abin da kowa bai so ko ake ganin disadvantage dinsa, sau tari kai shi kake so. Abinda baya burge kowa kai shi yake burgeka.**

**Ya ce auren da ka yi shi kadai ya mara maka baya saboda daga Hajiya Fatu har 'yan uwanka mata babu mai son auren saboda diyar Alaramma ce kuma stammerer.**

**Da wannan nake cewa, ni kuma na baka Azeezah, ka nemi yardarta, in Allah ya sa ta amince da zarar mun gama wannan project din, sai mu durfafi daurin aurenku".**

**Shayin da basu sha ba kenan a yau, haka suka fita suka barshi a wurin ya huce.**

Baba Murtala farin ciki ya hana shi sukuni, suna tafe a hanya direban Baban na sharara gudu da su a bayan Hyundai din Alhaji Murtala, sai ya ji Baba na waya da Azeezah din.

"Azeezah kina gida ne?"

"Mun fita ni da Mama Agege, amma muna hanyar komawa gida yanzu haka".

Ya ce, "To ki shirya tarbar bako yau da daddare, wajen karfe takwas in na dawo gida".

A dukunkune da fuska ta ajiye wayar don ta yi tsammanin ya dauko mata malamin da ya ce zai dauko ya dinga koya mata karatun addini a gida ne.

Ita a wurinta ta wuce zama gaban Malamin islamiyya yanzu. Baba Murtala kuma ya ce, ko izfi goma ya san bata hada ba.

Don haka ko da suka dawo gida ita da Mama, bata yi wani kyakkyawan minti

**goma a falo ba, ta gudu dakinta tasa sakata.**

**Zayyan sai goshin magriba suka dawo gidan shi da Baba, don haka masallaci suka wuce kai tsaye, wanda ke like da gidan Alhaji Murtala.**

**Can suka zauna suka bi jam'i har bayan da aka idar da sallar isha. Ko a masallacin Addu'a yake cikin ransa, idan nemansa da Azeezah alkhairi ne a gare su, shi da Safiyyah, Allah ya bashi kwarin gwiwar iya tsayawa a gaban wata macen da sunan neman soyayya ba Safiyyah Dandume ba.**

**Da suka fito daga masallaci Baba ya ce su wuce cikin gida su yi dinner, sai ya ce ma Baba yana zuwa.**

**Ya koma masaukinsa ya sake wanka, yau Zayyan kananun kaya ya saka, shirt da wandon jeans baki Tommy Hilfiger. Zai fesa turare kawai idanun Sophie suka fado cikin nashi idanun, sai ya fasa.**

**Don ji ya yi tamkar hakan ya zama cin fuska a gare ta.**

***"To na nawa kuma Malam Zayyan? Tunda gaka ka dauki wankan zuwa zance gun budurwa?"***

**Wata zuciyar ta tambaya ta kuma kara masa da ce masa, "*You are no longer a trusted husband to Sophie, you are now a "man" like other men, who are guided by their heart desires and emotions*".**

**Ma'ana; kai yanzu ba dan amanar Safiyyah bane. Ba mijin da zata bugi kirji ta yarda dashi bane. A yanzun daya kake da sauran maza babu banbanci, wadanda ke tafiya akan muradin zuciyarsu da shaukin dake zukatansu".**

**Wannan tunanin ne ya sa jikinsa yin sanyi kalau, ya maida turaren muhallinsa ya ajiye. Ya fasa fesawa.**

**Amma sai wata zuciyar ta tabbatar masa da cewa, kara aure ba cin amana bane ga maza, ba kuma cin fuska ne ga Sophie ba. Karewa ma, yana ganin zai**

**nemi wannan auren ne don ya samar mata maslaha a zama da shi, sannan ya nemo mata nutsuwa da kwanciyar hankalin data rasa a cikin rayuwarsu.**

**Muhimmi shine zai yi auren nan ne ma don ta samu Da daga gareshi. Wanda ya yi alkawarin nata ne da duk macen da ya haifa, kuma hakan maslahar ta ce a rayuwa da Mama, duk wata tsangwama, duk wani zargi na ta mallake shi zai kau daga idanun Mama yanzu.**

**Da wannan tunanin ya dan samu karsashin nufar cikin gida. Wai shi Zayyan ne yau zai je zance gun budurwa ba Safiyyah ba. Yana taku a hankali kamar ya fasa zuwa zancen, musamman da yake jin tamkar idanun Safiyyah na kallonsa.**

**Amma da ya tuno surar Azeezah da iya kwalliyarta sai nan da nan wata zuciyar ta ce,**

**"Zayyan kada ka bada maza mana, polygamy ba kanka farau ba".**

**Ya samu Baba yana waya, tuni an shirya musu abincin dare. Ya yafito shi da hannun damansa don ya zauna gefensa *as usual*.**

**Sai da ya gama wayar sannan suka fara cin abincin Baba na masa hira. Duk da Baba Murtala ya fahimci yau ya kasa sakin jikinsa da shi, shi ya sa ma yake kara jan hirar tasu don ba ya so surukuta ta shiga tsakaninsa da Dan nasa Zayyan tun yanzu. Yafiso su ci gabada gudanar da rayuwarsu normal ta uba da Da yadda suke yinta.**

**Sai da suka kammala Baba Murtala ya ce, ya shiga daga falon Hajiya Nana za ta turo masa Azeezah.**

**Bai jima da zama ba Hajiya Nana ta turo ta falon. Azeezah ta shigo fuska a turbune don ta dauka ko Malamin islamiyyar ne ya fara zuwa, don daga Mama har Alhajinsu ba wanda ya gaya mata cewa Zayyan ne. Don haka da ta ganshi a falon ta kusan sakin fitsari daga tsaye. Duk ta rude, domin kwarai Zayyan**

**mijin Safiyyah ke da kwarjini a idanun ‘yammata.**

**Rasa me za ta ce ta yi, tunda dai ai ta san babu wata manufa da Baba zai turo mata shi in ba ta neman aure ko dalili makamancinsa ba.**

**“Zauna mana Azeezah”.**

**Zayyan ya fadi cikin tsare ta da idanunsa da suka kara ruda ta.**

**Haka ta dosana ta zauna a nesa da shi akan hannun kujera.**

**Ya gyara zama ya ce,**

**“Kun dawo kenan?”**

**Ta amsa da “Eh”. Tana wasa da ‘yan yatsunta.**

**Sai ya yi gyaran murya ya ce, “toh dai Azeezah, ba sai mun ja ta da nisa ba, tunda dukkanmu ba yau muka san juna ba. Kuma diyan Baba ne mu duka ba bakin juna bane.**

**Sannan ni ba yaro bane kamarki, na kusa shiga shekaru arba'in, kin ga kenan babu bukatar yin kwane-kwane ko bata wa junanmu lokaci.**

**Azeezah na ganki a gidanku, gaban iyayenki kuma na yaba, in short I admire you, zan so kara ki cikin iyalina idan kin amince.**

**Sunana Zayyan Bello, kamar yadda kika riga kika sani, ni dan marigayi aminin Baba ne. Ina da mace daya mai suna Safiyya, wadda tunda muka yi aure sama da shekaru goma ba mu taba samun matsalar da muka kasa warwarewa a tsakaninmu ba".**

**Ya dan nisa kafin ya sassauta murya ya cigaba da cewa.**

**"Azeezah ni da matata muna da fahimtar juna, ina son kara aure ba don ta rage ni da komai ba, ina kuma barar shigowarki cikinmu, don kara dankon zumuncin gidanmu da gidanku. Idan har kin amince bana so abin ya dauki lokaci,**

**don ni da ke babu bukatar sanin asalin juna, sai amincewarki kadai nake nema".**

**Duk wata kalma guda daya da yake yi a kan matarshi kular da Azeezah ta ke yi, har ta ce a ranta, wai shi wannan a wurinsa haka ake zuwa neman soyayyar budurwa? Da alama farin shiga ne gun zuwa zance wajen budurwa 'yar zamani kamarta.**

**Ba zai maida hankali wajen gaya mata irin kamun da soyayyarta ta yi masa ba, sai wani yan-yan-yan akan tsakaninsa da matarsa?**

**Kamar ta yi kuka saboda ba wannan take son ji ba, ta ce cikin gatse.**

**"Kuna da irin wannan fahimtar juna da soyayyar kai da matarka, to meye naka na son kara aure, kuma me ka zo nema a gare ni tunda ba so ba ne ya kawoka? In zumunci ne ai da abinku na ganku kaida Baba, so ko dani ko babu ni zaku cigaba da abinku yadda na riskeshi".**

**Tana fadin hakan ta sha mur sosai, ta dora kafa daya kan daya, don ta tsani rainin hankali irinna maza.**

**Kwarai tambayar tata ta shammace shi, har ya rasa amsar da zai bata, hakan yasa ya baiwa kansa assignment na 'yan sakanni. Don ya samu amsa kwakkwara da zai bata.**

**Yana ganinta yarinya, mai tarin wauta, ashe-ashe tasan abinda take yi? Meye dalilin son kara aurensa? In har yanada komai da yake bukata a gidansa? Shine assignment dinda shima ya baiwa kansa a yanzu.**

**Dalilai da yawa masu muhimmanci sun yi mujazar wannan son karin auren, domin yana ganin shine kadai maslaha a gare su shida Safiyyah, don yana sha'awar mace irin Azeezah a gidansa da rayuwarsa, yana son mace 'yar gayu, mai wayewar kai, domin likely mace mai body shape dinta da irin dirarrun dugadugan kafar Azeezah itace daidai shi. Ustazancin Sophie yayi masa yawa, tsayin**

**shekarun da sukayi tare da zata canza da tuni canza to ba'a sakewa mutum nature dinsa, wanda shi yake hana ta sakin jiki su yi irin soyayyar da shi yake so, *for over a decade* da aurenshi da Sophie yana ganin bai samu sakewarta da shi a gadon aurensu irin yadda yake so ya kai sau goma ba, saboda kunyarta da kawaicinta akan hakan, amma ba don bata sonshi ba.**

**Azeezah za ta yi *bridging* wannan *gap* din, ga dukkan alamu, duk da tarin *negativities* dinta da mahaifinta ke kuka dasu, shi ba zai zame masa matsala ba in dai zai samu yadda yake so da ita, yake kuma kwadayin samu a gidan aurensa, ko da kuwa Safiyyah ta haihu, hakan ba zai hana shi wannan auren ba.**

**Sannan idan Allah ya nufa ya samu haihuwa da Azeezah kafin Safiyyah dan ko 'yar na farko da yardar ubangiji zai zamanto tukwicin kauna ta gaskiya ne da zai yiwa Safiyyah.**

**A takaice *sexual dysfunction* din Safiyyah da neman mata yaro daga gareshi, su ne dalili kuma silar son kara aurensa.**

**Azeezah ta kafe shi da idanunta tana jiran amsa, tana kuma ankare da yadda tambayarta ta jefa shi a gumi da tunani. Zayyan ya dago a hankali suka hada ido, sai ya yi mata murmushin da ya kara narka zuciyarta a kansa.**

**Ya ce, "kisa a ranki babu namijin da zai zo neman aure a inda babu burbushin soyayya a ransa. *I like you* Azeezah, amma don Allah kalmar SO dinnan ki yimin jinkirinta, har sai na tantance ta a raina, kada in fade ta a lokacin da bai dace ba.**

**Na yi miki alkawarin adalci da farin ciki a gidana, don ke kanwata ce da ba zan iya cutarwa ba, ina son aurenki bisa yarda da amincewarki".**

**Maganganun nasa sun ki zauna mata daidai a kwanyarta, don jinsu ta ke tamkar rainin wayo. Amma me?**

**Zayyan din ya zo da karfin chemistry din da ya fizge zuciyarta nan da nan zuwa gare shi, har ta ke jin ba za ta iya ce masa dole sai ya takura kansa ya furta mata abin da ta ke son ji ba, tunda dai ya ce babu namijin da zai zo neman aure a inda babu burbushin soyayyar mace a ransa.**

**Zayyan ya katse mata tunanin da ya jefa ta da cewa,**

***"Can I go ahead Azeezah*****? Kin yarda iyaye su shigo cikin lamarinmu, in sanya ki cikin iyalina?"**

**Azeezah ta juyar da kai gefe, zuciyarta na bugawa da shigar SO farat daya, babu bata lokaci zuciyar tace itafa ta yi na'am da dan mutanen Rafindadi. Ko ma dai me yake nufi da cewa ta yi masa uzurin jinkirin kalmar soyayya zuwa wani lokaci za ta yi wannan uzurin, domin ta tabbata wuyarta a yi auren, tunda har ya kawo kansa ya yi confessing na neman amincewarta da bakinsa.**

**Tana wannan tunanin, ya sake maimaita tambayarsa na neman yardarta har ya ce,**

**"Kamar yadda ki ka gani ni ba yaro ba ne Azeezah, ba zan iya *long dating* dake ba, *I truly admire you*, ki ba ni yardarki".**

**Sai ta samu kanta da gyada kai kawai, ta kuma tambaye shi ko yaransu nawa shi da maidakinsa Safiyyah?**

**Zayyan ya dan ciza lebensa cikin 'yar damuwa kafin ya ce.**

**"Muna fatan Allah ya kawo su nan gaba. In kuma daga wajenki Allah ya bamu, ina neman alfarmar ki baiwa Safiyyah ko me ki ka haifa na farko. Na tabbatar miki za ta yi masa rikon da ko ke ba za ki yi masa ba tunda Da na ne. Za ta yi masa tarbiyyah irin wadda ko ke ba za ki yi masa ba. Za ki yi mana wannan alfarmar Azeezah?"**

**Wani abu a halin Azeezah shi ne, ba ta boye abin da ke ranta. Ita ma bata so a**

**boye mata. Ko kuma tarin kuruciya ne ya debe ta a wancan lokacin? Har ta yi masa alkawarin yi masa wannan alfarmar.**

**Ta ce, "Allah da Ya halicce ni bai yi ni da son hidima da hayaniyar yara ba. Amma zan so in san kai da ita din waye mai matsalar haihuwa, don ka ce min kun yi kusan sama da shekaru goma tare?"**

**Wani abu da ba zai iya ba shi ne, yin zancen nan da wani, wanda ya kasance sirrinsu shi da Safiyyah, don haka ya ce da Azeezah, *"We are all fit and healthy Azeezah, muna jiran hukuncin Ubangiji a kai. Now, tell me about your* samari? Su nawa ne?"**

**Azeezah ta yi wata 'yar shashashar dariya ta ce, "To me ye ruwanka da su "Dan Daddy?" (sunan da ta sa masa kenan, wato dan Babanta Alhaji Murtala, don Baban ma ce masa yake Dan wajena, tun ba su hadu ba ta sha jin yana ma mamansu Hajiya Nana zancensa), tunda dai kai Allah ya kashe ya baiwa Azeezar?"**

**Sai bayan ta fadi hakan cikin subutar baki sai ta ji kunya sosai, shi kuma Zayyan sai kansa ya kumbura. Abinka da namiji a hannun wayayyar yarinya, tuni Azeezah ta sa ya sake da ita, ta bashi labarin ita cikin masu sonta mutum daya ne soyayyarsu ta yi nisa a makaranta, wato wani mai suna Faris. Sun hadu ne a Cyprus.**

**Bayan dawowarsu daga karatu ya zo nan gidansu zance, Baba ya ganshi da wani (haircut), wanda bai masa ba. Tun daga ranar Baba ya saka masa karan-tsana, wai askin 'yan iska ne akansa kada ya kara zuwar masa gida".**

**Dariya sosai Zayyan ke yi, Azeezah ta dauki hankalinsa sosai da salon maganarta ta 'yan gayu, ga iya Hira, musamman yanayin yadda ta ke magana cikin rangwada da karya kai, har da yada hannuwa cikin salo mai daukar hankalin da namiji.**

**Ya ce, "What I want to know now (abinda nakeson sani yanzu?), ke kina son**

**Faris din, ko kuwa Babana yayi miki kancal ne daya koreshi?"**

**Ta yi masa wata hararar love, ta ce, "In ma na so shi, to kafin in dora ido a kan Dan mutanen Rafindadi ne, shi kam sharp shooter ne, tuni ya sa na manta da kowa har ni da kaina ina mamaki".**

**Zayyan ya mike ya iso inda ta ke zaune, ya dan tsugunna kadan saman kanta, ya dafa hannun kujerar da ta ke zaune yana murmushi.**

**Azeezah ta shaki *ultraviolet* dinsa sosai, wanda ya riga ya kama jikinsa da ya fesa ko bai fesa ba, har ta kusa shidewa a wurin don wata soyayyarsa mai dadi data kara kamata.**

**Ya ce, "Insha Allah ni kuma na yi miki alkawarin ba za ki yi nadamar zaben Dan Rafindadi a matsayin abokin rayuwarki ba. In dai za ki girmama min Sophie, za ki taya ni lallabata da martaba ta to in sha Allah zamu zauna lafiya.**

**Ina tabbatar miki za ki same ni fiye da yadda kike so, ko kike burin samun abokin rayuwarki".**

**Tun daga ranar soyayyar shi da Azeezah ta kullu a gidan mahaifinta, kullum suka dawo aiki shi da Baba, to a falon da aka ware musu yake yada zango can Azeezah za ta kai mishi abincin ranar shi dana dare.**

**Tuni Hajiya Nana ta daina hada mishi kwano da Baba, har ranar Baba Murtala ke masa tsiya da cewa, Azeezah mai yankan kauna, haka kawai ta raba mishi kwano da dan wajensa.**

**Baba Murtala da Mama Fatu sun fi kowa farin cikin wannan al'amari, don kafin ya gama kwanakin aikinsa a Lagos Mama da Azeezah sun gaisa a waya a gabansa ya kai sau uku.**

**Hajiya Nana kam bata so ba, musamman jin Zayyan yana da mata, amma ganin yadda 'yar da uban duk suka mika wuya, sai ta sallama musu. Amma**

**kwarai ba ta son Azeezah da auren mai mata, don ita kadai ta rayu a gidan Alhaji Murtala tun daga kuruciya har girma. Kuma Azeezar nan ita kadai ta rage musu mace a gabansu.**

**Sai dai ta san Hajiya Fatu irin farin sani, a matsayinsu na matan abokan juna tun kuruciya, ta san Mama Fatu tun Architect Bello na raye, kuma a saninta ba ta da wata matsala da mijinta da al'umma, wannan ne ya yi *convincing* amincewar Hajiya Nana Aisha, don Mama ta kira ta officially ta ce ba jimawa za su kawo lefe.**

**Namiji kenan, duk inda yake sunansa namiji in dai a kan mace ne, ko idan ya so kara aure. Shi kansa yana mamakin wannan al'amari domin bai taba planning dinsa a kamus din rayuwarsa ba.**

**Rabonsa da ya kira Safiyya, ko ya saurari kiranta da sakonninta tun saukarsa a Lagos, da tozalinsa da 'yar Babansa Alhaji Murtala.**

**Kullum da dare kusan kwana yake yana questioning kansa, yana mai kalubalantar kansa a kan wannan hukuncin da ya yanke. Amma ba ya bari tuhumar ta yi nisa yake kare kansa ta hanyar gaya wa kansa hakan shi ne kadai solution ga dukkan matsalolinsa da Sophie.**

**Allah sarki Safiyyah, tana can Abuja amma ruhinta yana Lagos, cikin damuwar canjin farat daya data samu daga Habiby dinta, wai yau Habiby ne ko wayarta ya daina dagawa kuma bai kara nemanta ba har kwana takwas da tafiyarshi, a kan laifin da a ganinta bai kai ya kawo ba.**

**Shin me ta yi masa haka ma da zafi ne? Ba yau ta soma rejecting dinsa a aurantayya ba, amma bai taba daukar abin da zafi irin wannan karon ba.**

**Ba ta da masaniyar yana can Lagos yana banzar soyayya da diyar ubangidansa, wadda cikin dan kankanin**

**lokaci ta kunce masa lissafi, ta sauke masa hadda.**

**Ba ya ko tunawa sosai da Sophie sai ya zo kwanciya bacci, to yanzun ma saboda wayar tsakar dare (midnight call) da suka tsiri yi shi da Azeezah ba ya ko samun lokacin da zai yi missing dinta cikin dare. Abun da ya sani shi ne, son Safiyyah a zuciyarsa daga Allah ne, babu mai maye gurbinta. Babu mai tumbuke matsayinta, amma ya rigada yazama attracted and highly infatuated ga son auren Azeezah.**

**Yadda Mama Fatu ta dauki zancen auren Azeezah da matukar muhimmanci kamar dama a jirace take bai kamata ya bashi mamaki ba, amma hakika ya bashin. Don kafin ma ya baro Lagos Mama da Zubaidah sun gama hada lefe na gani a bada labari kamar diyar gwamna za a kaiwa, akwatuna dozen, masu matukar matsayi, babu ce kurum babu a cikin lefen da Zubaidah ta hada.**

**Ana i-gobe zai baro Lagos, shida Azeezah ido ya raina fata, sukayi wata irin sallama ta soyayya saura kadan suyi runguma yayi maza ya fice, zuciyar sa na balli balli. Da kyar ya kwanci kansa daga zarce iyaka. Mama ta gayawa Hajiya Nana cewa suna so su kawo lefe washegarin dawowarsa gida.**

**Abin dai tamkar tatsuniya ko kuwa almara. Komai da komai ya faru tamkar kiftawar ido, neman auren da bayarwa da saka rana duk sun faru ne cikin abin da bai gaza sati uku ba.**

**Ranar da ya koma Abuja bai ko gayawa Sophie yana hanya ba, bai tashi jin kunyar kansa da kansa ba, sai da ya yi tozali da Safiyyah.**

**Damuwar da ya jefa ta a ciki ashe har kwantar da ita zazzabin sati guda ta yi, ta rame ta yi fiyat, kamar da ka bushe ta zata fadi, amma kyawun nan na Safiyya yana nan daram, duk da muguwar ramar da ta yi.**

**Ya ji kunya in ya ce kunya, yana nufin kunya ta karshe da bai taba ji a rayuwarsa ba, don Sophie ba ta ma san da dawowarsa a ranar ba.**

**Tana kitchen tana dafa ruwan 'tea' da za ta saka a hantar cikinta dake raurawa, ta ji motsin shigowarsa falon, ta hanyar amfani da nashi safayan makullin gidan.**

**Safiyya ta juyo da sauri jin motsin shigowarsa da kamshin turarensa. Suka hada ido, sai ya ji kunyar da bai taba ji ta diya mace ba ta lullube shi, hade da wani irin 'guilt'.**

**Fuskar Sophie kadaran-kadahan, wato ba yabo ba fallasa ta ce, "Sannu da zuwa". Sannan ta juya tana ci gaba da juye ruwan zafin da ta kammala tafasawa a karamin 'tea flask'. Tana kokarin hadiye hawayen da ke son gangaro mata.**

**Zayyan ya canza gabadaya har wata kuruciya da fresh fatar jikinsa ta kara, alamu ne na yana cikin mabayyanin**

**kwanciyar hankali, hutu da jin dadin zamansa a Lagos, bai ma san halin da ya jefa ta ba. Ta sa dan yatsanta ta dauke hawayen da ya gangaro ta karshen idanunta.**

**Zayyan ya tako har inda take cikin shanye kunyar tasa, ya sanya hannayensa ya sakalo kugunta ya dora habarshi saman kafadunta yana sakale da *waist* dinta, ya ce cikin muryar rarrashi.**

**"Sophie I'm back, me ya faru da ke haka, irin wannan rama haka my Dear Safiyyah?"**

**Safiyyah ba ta taba hararar Zayyan bisa saninta ba sai yau, ta zabga masa harara ta zare hannayensa daga kugunta ta dau tea dinta da kofin mug ta bar wajen.**

**Haka ya biyo ta falon cikin karfin hali irin na Da namiji, ya ce.**

**"Laifuffukana ba za su lissafu ba gare ki Safiyyah, na sani. Amma ki gafarce ni yanzun ki fara ba ni abinci ba**

**don halina ba, I terribly miss your cooking".**

**Hawaye suka sulmiyo daga idon Safiyyah, wani weak point dinta kenan guda daya shima ya sani, ba ta iya barin Zayyan da yunwa, don haka shayin da bata sha ba kenan duk da itama yunwar take ji. Sai ta koma kitchen ta shiga hidimar girka masa abinci.**

**Shi kuma ya bi ta kitchen din ya zauna a kan *granite* yana ta baibaye ta da kalaman ban-hakuri da amsar laifi. Shi kansa ya rasa hujjarsa ta kin neman Safiyyah ko amsa wayarta har ya je Lagos ya dawo.**

**Gani ya rika yi yana daga wayarta ko tana jin muryarsa za ta gane ya fada komar wata macen ba ita ba, amma ba don laifin da ta yi masa a ranar da zai tafi ba.**

**Ta kammala dafa masa jallof din cous-cous da ya ji veggies da hanta sosai,**

**ta zubo a faffadan tray ta kai masa kan dining din dake cikin kitchen din.**

**A nan ya zauna yana ci, yana yima girkin Sophie cin yaushe gamo da kewa mai yawa.**

**Ya yi- ya yi ta zauna su ci tare ta ki tsayawa don in ta ci gaba da tsayuwa a wurin rauninta bakidaya da take boyewa zai bayyana kansa. Ta ji ciwon abin da ya yi mata, domin ya zarta hukunci a kan laifinta, a ganinta ya koma zalunci kuma ya dauki hakkinta.**

**Tunda ta bar kitchen din shima ya ji ba zai iya ci gaba da cin abincin ba, tashi ya yi ya biyo bayanta zuwa dakinta.**

**Tana canza kayan jikinta, tana kokarin daura towell don shiga wanka Zayyan ya zagaye ta cikin hannayensa, ya kai mata sumba a wuya, ta goce da zafin nama. Ya sake kai mata a bakinta, nan ma ta kwace, amma Zayyan bai bata damar hakan ba domin tuni ya samo bakinta ya soma yi mishi tsotson yaushe gamo.** ***As***

***usual* duk yadda ta so bijire ma Zayyan a wannan fannin da wuya ta ke samun nasara. Wuyarta ya soma kissing bakinta da nasa**

**Kuka ta saka masa, shi kuma ya soma lallashinta har da roko. Bai sakaya mata yadda bijirewarta gare shi ya saka shi sha'awar kara aure ba. Duk da bai fito fili ya fada mata har auren ya nema ba, an kuma bashi, amma kuma Safiyyah duk ta sha jinin jikinta.**

**Wanda hakan ya sa ta kara jin bacin ranta ya ninka na baya. Wani abu da Zayyan bai taba yi ba shi ne, tursasata kan ta yarda da shi, amma yau? Yadda yake so haka ya sarrafa Sophie, alhalin taki amincewa, yace saidai duk su mutu amma bazai iya hakurin ba, tana kuka tana gaya masa ta tsaneshi ta kuma tsani auren bakidaya. Ko a jikinsa, nemawa kansa nutsuwa kawai yake. Duk sha'awar Azeezah da ya kwaso a Lagos a nan ya sauke ta tas.**

**Sai da ya samarwa kansa nutsuwa yadda ya kamata sannan ya sassauta mata. Ya koma gefe hannunsa cikin tarin lallausar sumar kansa, ya rasa abinda ke masa dadi kuma. Yau shine da marital rape ga Sophie, amma ai ita ta jawo! Sama da sati uku kenan rabonsa da ita.**

**A kasalance ya dube ta tana kokarin suturta kanta da towel dinta da ya jefar gefe don ta shiga wanka ya ce,**

**"Safiyyah, ashe soyayya na komawa kiyayya saboda rashin haihuwa?"**

**Saura kadan Safiyyah ta zagi Zayyan yau, to kuma durawa soyayyar ashariya, amma 'Yan gidansu basa zagi sam. Ta galla masa harara idanun sun yi jazur da danshin hawaye, ta shige toilet.**

**Ya sanya shorts dinsa ya bita har toilet din, tana wanka a shower tana kuka, nan ma sake nanikarta yayi, suka yi wankan tare, ya nado ta a tawul ya dauko ta suka fito, ya shiga goge mata jiki da karamin towel, sannan ya dauki lotion**

**dinta na Nivea ya soma wani irin shafa mata a dukkan jikinta, tana ki tana komai sai da ya shirya ta tsaf, ya sanya mata bakar jallabiyyarsa, ya tarairayo ta ya aza bisa cinyoyinsa, sannan ya ce.**

**"Now tell me, me ye matsalarki Sophie? Ko kin daina sona ne Safiyyah?"**

**Ya dago habarta ya dube ta cikin ido, sai ta rufe idanun nata da ke zubar da hawaye har a lokacin. Ba zai gane irin ciwon da ta ke ji a ranta ba a kan rashin haihuwa da shi, haka ba zai gane yadda biris din da yayi da ita har tsayin sati biyu ya kassara zuciyarta ba.**

**Duk ma ba wannan ba, Zayyan bai taba iya wuni guda bai kirata a waya ba, amma yau kwana dai-dai har goma sha hudu! Zayyan ya kwashe ba ta ko ji muryarsa ba. Alhalin yana lafiya sumul kalau. Jikinta ya gama ba ta (something is fishy) don wannan ya zarce punishment kan duk wani laifi da yake ganin ta yi masa.**

**Ya yi rarrashin duniya yana rokonta ta yafe masa, wani abu ne ya kutso cikin rayuwarsa a wannan tafiyar da yayi, da ya hana shi kiranta.**

**Yayi ta zagaye-zagaye, ya kasa gaya mata komai, har dai ya samu ta ce masa ta hakura ta kuma yafe, amma don Allah tana rokon alfarmar su kara yin IVF ko ta samu sanyi a zuciyarta kamar kowacce mace.**

**Ya tuno da gargadin Mama a kan sake yin IVF, in ya gaya mata Mama ta hana kuma zai zama tamkar ya kara hada gaba tsakaninta da Mama, dama Ya Allah cika. Don haka ya samu gangara ya ce.**

**"Safiyyah tuni na samo mana solution a kan wannan matsalar, IVF mun yi shi a baya, wannan karon na canza shawara, na ce me zai hana in kara aure?**

**Mu yi fatan Allah ya kawo rabo na gaggawa?**

**Safiyyah na miki alkawarin ko me matar ta haifa na farko danki ne halak**

**malak dinki, ko shayarwa in kin so ke za ki shayar da shi”.**

**Safiyyah ta yi yunkurin mikewa daga cinyoyinsa ya sake maida ita ta zauna, don ta fara tunanin ko Zayyan ya fara shaye-shaye ne? Kalmar zai kara aure a wannan lokacin ita tafi komai bata mamaki, ba almararsa ta wata ta haifi Da ya kyautar mata ba.**

**Ta yarda da aka ce duk wadda ta ce namiji uba ne za ta kwana marainiya!**

**Haka kuma duk inda mijinki ya kai da sonki, kada ki dauka akwai bambanci tsakaninsa da sauran maza, duk sunansu MAZA!**

**Ta tsaya ma tana asarar hawayenta ya zama asara ko faduwar da babu tashi. Don haka Sophie ta share hawayenta, ta dube shi da idanun rahma ta ce.**

**"In kana ganin wannan shi ne mafita, kuma zai samar min sa’idah a wurin Mama da ‘yan uwanka, sannan zai sayo min soyayyar Mama ta yarda ban**

**mallake ka ba, kamar yadda kullum suke cewa, sannan hakan zai ba ka farin ciki Zayyan, sannan baza'a kara yimin gorin haihuwa ba, to (you have my full support) ka kara aurenka".**

**Ya yi sak da zuciya da idanu, yana kallonta kamar mai son karantar gaskiyar da ke cikin zuciyarta. Don bai taba zaton al'amarin zai zo masa haka cikin sauki daga Safiyyah ba. Ita ma ta dube shi cikin ido, yau babu kallon soyayya, ta ce,**

**"Yes, I mean it".**

**Ya ce, "Amma na ji wani suna daga bakinki wanda bada shi kika saba ambatar sunan mijinki ba, anya Safiyyah har zuciyarki kin amince in kara auren?"**

**Safiyyah ta buda hannuwa irinna matsalar taka ce ba tawa ba tace, "Habiby, na fada na kara Habiby, Habibiy, shikenan ko?**

**Ka yi hakuri tuntuben harshe ne nayi nace Zayyan!".**

**Amma ita a kasan zuciyarta ta san soyayyar ce ta ragu, ta yi flat a kasa daga wannan lokacin.**

****** **** ******

**Washegari ya shirya yayi mata sallama ya tafi Katsina, ita kuma ta yi amfani da wannan damar wajen yin azumi, ta wuni da azumin tadauwi'i a bakinta, tana tunani irin mai cin zuciya. Wai Zayyan ne ya gaya mata da bakinsa yau zai kara aure, don ya samo mata Ds daga gareshi, in ba ta yi da gaske ta yakice al'amarin daga ranta ba zai iya zauta kwakwalwarta.**

**Ko bayan da aka sha ruwa addu'a ta yi ta musamman a kan in tana da rabon haihuwa da Zayyan Allah ya kawo wannan rabon cikin gaggawa. Don ta tabbata bada wasa yake yi ba, da ya ce yana so zai kara aure. Dansa ko 'yarsa ne kadai za su maye mata gurbinsa a yanzu**

**da ya fara tunanin kawo wata macen cikin rayuwarsu.**

**Ta san tabbas daga wannan lokacin ta rasa previous Habiby dinta. Bazai kara dawowa irinna baya ba.**

**Ko da dai dama daga tafiyarsa Lagos zuwa yanzu ta san wannan ba Zayyan dinta data sani a baya bane, duk da yana kokarin wanke mata zuciya da kalamai na fatar baki, a banza man kare a wurinta.**

**Bayan ta yi sallar magriba ta sha ruwa, ta samu wayar Aunty Zubaina, tana dauka ko gaisawa Antin ba ta bari sun yi ba, tace,**

**"Safiyyah kina da masaniyar abin da ke faruwa kuwa, kuma da yardarki da amincewarki ake nema wa Zayyan auren diyar Baba Murtala?"**

**Sai da ta ji kirjinta ya bada dam! Bana jin maganar karin auren ba a'ah, na jin ko wa Zayyan zai aura. Amma tuni ta**

**sa ma ranta salama don haka ta ce wa Anti Zubaina cikin kasalalliyar murya.**

**“Ya dai gaya min ko na amince ya kara aure? Kuma jiya-jiya ne muka yi zancen Anti”.**

**Anti Zubaina ta ce, “To ai an gama komai, gobe za a kai lefe da kudin aure duka. Ya dace yayi miki cikakken bayani, ni banason munafurcin maza in sun tashi fitinar karin aure.**

**Amma ki bar ni da shi, zan gamu da shi wallahi, ba haka ake fada wa uwargida neman aure ba”.**

**Kasa cewa komai Safiyyah ta yi, don yanzu ta gama gano dalilin Zayyan na share ta a tafiyarsa Lagos, wato ya yi gam da katar da ‘yar masu kudi burin mahaifiyarsa.**

**Baba Murtala ya damesu ya shanye Baba Bello a kudi da tarin dukiya balle Zayyan. Ko me suke dashi yau a dalilin taimakon Baba Murtala ne. Safiyyah ta kara jin tausayin kanta, me zata yi yanzu?**

**Kuma me za ta ce a kai, banda yi musu fatan alkhairi?**

**Ammi kawai ta iya kira jikinta babu lakka, kuma ta kasa hawaye ko taji dama dama. Tana ajiyar zuciya ta labarta ma Ammi komai. A karshe ta ce,**

**"ki yi min addu'a Ammi, zuciyata tana tafarfasa, Zayyan ya shammaceni, abu ne da ban taba zato daga gareshi ba, saboda na tabbata wannan auren Zayyan zai yi shi ne don radin kansa, babu wanda ya tursasa shi ga yinsa.**

**Amma Ammi da a ce na haihu ko sau daya ne, ba zan taba damuwa don Zayyan ya kara aure ba".**

**Tausayin 'yar tata ya kama Ammi Hafsatu, ba tun yau ba tana sunsuno ranar faruwar hakan ga Safiyyah, duba da matsalar rashin haihuwarta da yanayin yadda mahaifiyarsa ke alakantarta, harda ita kanta Ammin.**

**Babu wata mu'amala ta surukuta ko girmamawa ko kulawa da ta ke samu**

**daga Hajiya Fatu a matsayinta na wadda ta wanke ‘ya sukutum ta basu. Babu ko gaisuwar mutunci ta zuwa gida kota waya, rabonta da su hadu ma da Haj. Fatu har ta manta, amma wace ita da za ta hana su aure don su samu haihuwar da Safiyya ta kasa yi musu?**

**Ammi ta sauke ajiyar zuciya ta shiga lallashin diyarta. Lallashi da karfafawa irin wanda ya dace kowacce uwa ta gari ta yi wa ‘yarta.**

**Ta ce, “Ki kwantar da hankalinki Nana Safiyya, kishiya ba kanki farau ba, haka rashin haihuwa. Kedai ki yi zaman aure domin bautar Allah ki kyalesu, in ya so tazo ta haifi ‘ya’ya dozen.**

**Ubangiji Subhanahu wata’ala da kanSa, ya ce Yana jin kunyarku (matan da bai baiwa haihuwa a duniya ba).**

**Ki dauki karin auren nasa a matsayin kaddararsa da taki, ba a matsayin gazawarki ko kasawarki ba.**

**Safiyyah na yarda da tarbiyyar da muka baki, kada kiyi amfani da hakan ki muzguna wa mijinki. Ki masa uzuri sau saba'in da Allah ya ce ki yi masa. Albarkarmu na tare dake in Sha Allah ba za ki taba wulakanta a dalilin rashin haihuwa ba".**

**Nasihar Ammi ta karfafe ta, ta zuba mata wani kwarin guiwa. Tun daga ranar sai ta maida komai ba komai ba, ta shiga harkokinta.**

**Koda Zayyan ya dawo daga Katsina bayan an gama komai na aurenshi da Azeezah sosai ya ga canji daga gare ta, ta shiga hidima da shi yadda ta saba.**

**Ganin haka shi kuma ya saki jikinsa ya ba ta labarin Azeezah kakaf! Da yadda al'amura suka wakana a Lagos, kai har irin hirarrakin da suka gudana tsakaninsa da Azeezah sai da ya kwashe gaya mata.**

**Kullum yana kwantar mata da hankali, yana kara jaddada mata**

**alkawarin adalci da na girman matsayinta in Sha Allah bai taba canzawa a gareshi. Kowa zai auro zai auro ta ne don ta haifi Da ta bata, shi ba wata soyayya a zuciyarsa bayan tata.**

**Don haka Safiyyah ta kwantar da hankalinta suka ci gaba da tsare-tsaren auren shi da ita. Maimakon kayan fadar kishiya tsabar kudi ya bata masu yawa, ya ce ta yi duk abin da ta ke so da su, don ya san bata da matsalar sutura.**

**Ya gaya mata ko sisinsa bai yi ciwon kai ba wajen hada wa Azeezah lefe, duk Mama da Zubaidah ne suka yi masa.**

**Wannan ya kara tabbatarwa da Sophie yanzu Mama ta yi surukar So. Baffa ya auro mata classy suruka irin wadda ta dade tana masa buri.**

****** **** ******

**An saka ranar daurin auren Zayyan da Azeezah sati biyu masu zuwa, wata daya da zuwan shi Lagos. Baya kiran Azeezah**

**a gaban Safiyyah, haka ko ita ta kira shi in Safiyyah na wuri bai amsawa.**

**Ranar daurin auren na matsowa fargabar Zayyan na karuwa saboda silent treatment din Safiyyah gare shi. Ko da can Safiyyah mai biyayya da yakanah ce, da kula da shi, kai dai barta da kunya da nuku-nuku a gado da kin yi masa yadda yake so, da dressing irin yadda yake son ta yi masa. Kullum Safiyyah kara samun nutsuwa take saboda nasihohin Ammi, kullum sai Ammi ta kira ta a waya ta karfafe ta, ta kuma gaya mata wani sirri cewa.**

**"Babban abinda ke kama miji, yasa 'guilt' ya baibaye shi in ya tsiri kara aure shi ne biyayya ba fandare masa ba.**

**Saboda the more ta yi creating distance a tsakaninsu, saboda kara aurensa, the more amaryar za ta samu damar kara shiga ransa da nesanta shi da soyayyarta, ta kuma samarwa kanta matsuguni a zuciyarsa".**

**Har gobe Safiyyah tana matukar son Zayyan dinta, in ma ta ce son ya ragu ko ya tafi to ta fada ne don ta ji dadin bakinta (out of frustration). Don haka Safiyyah ta tattara kishi ta ajiye a gefe, ta kuma barwa ranta cewa ko matar Zayyan ta tare ba dai ta tsaya rigimar kishi da ita ba.**

**In ma an karfafe shi ya yi auren ne don a muzguna mata, ko a nuna mata iyakarta ta rashin haihuwa, insha Allah za ta rungume 'ya'yan Zayyan kamar ita ta haife su.**

**Soyayyar nan tata da Zayyan natural ce, ba abinda zai sameta da yardar ubangiji saboda wani dalili na karin aure da ba kansa farau ba.**

**Zayyan bai taba yi mata alkawarin ba zai kara aure ba, ya dai yi mata alkawari na soyayya da amana. Don haka yanzu da auren ya zo masa bagatatan tsakaninta da shi sai fatan alkhairi, da addu'ar ya zamo mai adalci a gare su, kamar yadda shima kullum yake fata.**

**Safiyyah ba ta tashi susucewa ba sai ranar da ya ce ta hada mishi kaya a jakar matafiya zai je wajen kanwarta a Lagos. Daurin aure saura kwana uku lokacin.**

**Ganin ya dau sabon aski ya shigo da sababbin dinkuna na alfarma, ya ce ta zuba masa a jaka. Cikin dauriya duk ta ke yin yadda ya ce, da ta zo daukar masa turaren 'Ultraviolet' ne sai zuciyarta ta idasa tsinkewa.**

**Zayyan bai lura da cewa jikinta ya hau rawa sannan idanunta sun cicciko da kwalla ba, domin ta bashi baya tana zuge jakar, bayan ta cusa turaren, ya ce.**

**"Am, Sophie kinga na manta in gaya miki gobe Mama ta ce za'a zo a yi kafin Azeezah don bayan daurin aure da kwana uku Azeezah za ta tare".**

**To dama gidan tun sanda aka gina shi tagwayen gidaje ya yi wa kansa a matsayin (semi-detached bungalow) tun sanda aka gina Sunset Estate.**

**Don haka barin hagu ya bai wa iyayen Azeezah su yi mata kafi.**

**Ai kuwa washegari an ga barin dukiya a gidan Arch. Zayyan Bello Rafindadi. Wasu ubansu-ubansu royal furnitures kawai ake saukewa daga company a gidan. Su Yaya Zubaida an kasa tsaye an kasa zaune abin nema ya samu wai matar dan sanda ta haifi barawo, kai ka ce diyar gwamna Zayyan Bello ya auro, saboda dukiyar da aka tamfatsa a sassan Azeezah.**

**A can Lagos an fara biki na alfarma, haka a Katsina Mama ta yi gayya ta fita tsara an soma biki na bugawa a "Ovasion", za a daura auren Arch. Zayyan da Azeezah Murtala washegari asabar a gidan kakanninta da ke Masari a Katsina.**

**Bayan ya dawo daga Lagos duk jikinsa ba lakka, saboda sabon nauyin iyalin da ya tabbata zai dada hawa kansa. Washegarin ranar ne daurin aure a Masari zai je Katsina ne inda daga can**

**zasu dunguma zuwa main house dinsu Azeezah. Inda acan za'a daura auren. Safiyyah tun asubah tana kitchen sabida shi yana barcin gajiya tun dawowarsa, kafin ya tashi barci ta shirya musu karin kumallo mai rai da motsi data san yanaso; sinasir da waina da miyar ganyen alayyahu, Ugu leaf da hanta.**

**Suka karya kumallo a dining kafin ya shiga wanka tana ta faman tsokanarsa wai ya fara kyallin goshi, tun ba'a je dakin amarya ba. Harararta Zayyan yayi ya shige toilet.**

**Wajen wankan ma ita ta surka masa ruwan wankan, ta zuba turaren wanka mai dadin kamshi na *desire dunhill* a cikin ruwan, sannan ta ajiye masa bath gel dinsa na *Cien* a gefe da farin tawul, ta juya za ta ja masa kofar, sai ya riko hannunta cikin marairata da karaya.**

**"Sophie, karasa ladanki mana ki cuda min baya… na rantse ba ni da karfi yau".**

**Dariya ta yi ta ce a ranta,** ***za ka ji karfin sai zuwa dare inta iso”.***

**Wani abu kamar daci-daci a makogaronta ya taso mata, wani tukuki ya turnuke zuciyarta, don haka ta yi saurin janye hannunta daga cikin nasa ta fice ta rufo masa kofar, tana neman hadiye abin nan da ya yi mata tsaye a makogaro, amma ta kasa.**

**Tana bude baki don yin magana kuma ta san fashewa za ta yi da kuka, ko harshenta ya lankwashe ko ya karye gabadaya, don haka yi masa shirun ta fice da gudu-gudu shi ne mafi alkhairi a gareta.**

**Ya yi wankansa tsaf, ba karsashi ko na kwabo a jikinsa, musamman saboda shirun da Safiyyah ta yi masa. Ta kuma yi tafiyarta daga toilet din ko kallonsa bata kara yi ba.**

**Yana shiryawa a dakinsa cikin wata sabuwar bugaggiyar shadda ‘yar ubansu**

**wadda Baba Murtala ya dinka masa don fitar daurin aure.**

**Yana so ya kira Sophie ta daura masa links na hannun rigarshi da maballin wuyansa yadda ta saba, ya ji nauyin hakan ya kyale ta. Ko ba komai ta yi masa kokarin da 'psyche' dinsa bai taba bashi ba.**

**Da ya kammala shiryawa ya same ta a dakinta tana faman fiddo kaya daga wardrove tana shiryawa duk don ta maida kanta busy, ta hana kanta zama shiru balle wani mugun tunanin ya sarke ta. Daga bakin kofa ya tsaya hannayensa biyu zube cikin aljihu, ya yi kokarin su hada ido, amma Safiyya ta ki. Ta cigaba da ninke kaya.**

**Ba ya son ya taba jikinta kada ya jangwalo rauninta, don haka ya yi magana daga inda yake tsaye.**

**"Mun wuce Masari daurin aure sai wajen dare kuma in taron mata ya watse zan dawo Sophie".**

**Safiyyah ta hadiye miyon bakinta ta ce.**

**“Ällah ya sa a daura a sa’a, Allah ya sa abokiyar arzikinmu ce, Allah ya bada zuri’a mai albarka da ake nema.....”**

**Wadannan kalaman na karshe ta karasa su ne cikin rawar muryar da ba ta so rauni ya fito a cikinta ba.**

**Shi kansa ji ya yi ya kasa daurewa, don haka ya shigo cikin dakin sosai ya karasa ya rungume ta, ya ce.**

**“Ina rokon Allah ya sa zuri’ar nan ta fara samuwa daga gare ki Sophie, ina kara rokonSa ya fidda ni kunyarki wajen adalci.**

**Ina jaddada rokona gare shi da Ya ba ni zuri’ar nan tare da ke komai rashin yawanta.**

**Kada Allah ya nuna min ranar da zan fifita wata a kanki, a dalilin haihuwa…”**

**Su duka jikinsu da muryoyinsu rawa suke yi, Safiyyah na amsawa da "ameen".**

**“Allah ya fara kwantar da babyna a nan..." (ya sanya hannu kasan mararta) kafin kowacce mace ta samu wannan babbar alfarmar…...”**

**Fatar bakin Safiyyah na rawa ta kara amsawa da "ameen".**

**Da tsakanin mutuwar jiki Zayyan ya bar dakin Sophie, yayin da Safiyyah ta yi zaune dirshan a gefen gadonta ta sanya fuskarta cikin tafukanta rike da singlet dinshi da ya cire, ta cukuikuiye fuskarta a cikin singiletin, amma ba kuka ta ke yi ba.**

**Karfe hudu na yammacin ranar waliyyai suka daura auren Arch. Zayyan Bello Rafindadi da Azeezah Murtala Babangida, bisa sadaki na burga, wanda Mama ta bayar na wara-waran zinare manya guda uku.**

**Daga nan aka wuce reception na maza, already amarya tana Abuja tun jiya gidan mahaifinta da ke Katampe.**

**Sai yamma lis ya dawo Abuja, kuma ko da ya sauka a Abuja bai shiga gidansa ba Park din cikin Estate din ya nufa ya tsaya a jikin 'railer' yana tunani, daga baya ya wuce gidan amininsa Habibu Nahuce, daidai lokacin da aka kawo amarya Azizah dakinta.**

**Abin kunya har da Yaya Zubaida aka yi shimfidar gadon amarya, su Zaitoon kuwa sai yada ma Safiyyah habaici ake ana cewa, uwargida sai kin yi hakuri fah, ah toh Azeezah 'yar babban gida ce shi ya sa za ki ga komai nata daban.**

**Kada ki ga furnitures ubansu 'yan Dubai ki dauka Yaya Baffa ne ya saya mata. Kin san da uba ake ado ba da miji ba".**

**Kasancewar Aunty Dije ta zo ma Safiyyah dannar kirji a ranar, ta kuma ji**

**me suka ce, sai ta tashi zaune daga kishingidarta, a ranta tace lallai Zahra da Zaitoon basu da kunya, sai ta ce musu,**

**"Kun manta kuma wani lokacin abin an ce abin fini uba in fiki miji ne? Allah na tuba Safiyyah tun asalinta ba ta son tarkace ita, dan English parlon nan nata ya ishe ta, tunda ba 'yar sarki ba ce, ba 'yar gwamna ko shugaban kasa ba, a'a ita diyar magada Annabawa ce, wadanda duniya bata gabansu".**

**Zaitoon ta shaka sosai sai ta bar dakin.**

**Aunty Dije ta ce, "Marasa kunyar yara kawai, Allah ya hada ku da dangin miji masu irin halinku".**

**Sannan ta kara ja ma Sophie kunne a kan kada ta sake ta tanka su ko me za su ce mata, giyar farin ciki ke dibarsu. To Allah na kowa ne, kuma zai iya mata abin da ta kasa.**

**Sai da ‘yan kawo amarya suka ware Aunty Dije ta kada kan su Sabah su ma suka wuce guest house din da aka yi musu masauki a nan cikin Sunset Estate. Suka yi sallama da ita a kan cewa da safe ba za su shigo ba, sammako za su yi su juya gida abinsu.**

**To shi ne fa Zayyan bai shigo gidansa ba sai can dare kamar yadda ya faru a farkon littafin, fatansa shi ne Allah ya sa wannan auren da yayi bai zamo (biggest mistake of his life) ba, wato bai zamo babban kuskuren sa a rayuwa ba, maimakon nemo mafita ga matsalarsu shi da Safiyyah.**

**Kiran sallar asubahi ne ya dawo da shi daga 'down memory lane' din da ya tafi, wanda ya kunshi gwagwarmayar kuruciyarsu data soyayyarsu data rayuwar aurensu shi da Safiyyah. Da kuma ranar yau, wato ranar da "Azeezah Murtala" ta tare a gidansa.**

**Azeezah ta iso cikin rayuwarsu da fatansa na zata zamo maslaha ga matsalolinsu.**

**Da ya dawo kuma ya dade zaune cikin motarsa saida ya tabbatar 'yan kawo amarya sun watse, kuma maimakon ya tafi dakin uwargida yayi mata sallama ya wuce gun amarya sai ya zabi ya wuce masterbedroom dinsa, yayi tunanin rayuwar sa da Safiyyah tun farkon fari, because he lacked all the courage na dosar inda Safiyyah take a wannan daren.**

**Zayyan ya kwanta ne kawai rigingine a gadonsa yake wannan dogon tunanin. Don yanzu da Azeezah ta zama mallakinsa, bakin alkalami ya riga ya bushe sai yake jin kamar yayi kuskure, kuma kamar bai kyautawa Safiyyah ba. Kamar wannan shine kuskure mafi girma daya aikatawa rayuwarsa, maimakon kawo maslaha.**

***Mu duka ni da ku masu karatu dai mun san cewa "not all that glitters is gold". Azeezah nada duk abinda yake so a diya mace, while soyayyarsa naga Safiyyah diyar Malamai, amma kuma muna sane da cewa Zayyan ya manta cewa babu yadda za'a yi ka samu rayuwa dari bisa dari daidai da ra'ayinka da burinka, dole kowa yana da irin nasa nakasun a wurin abokin rayuwarsa.***

***A rayuwa, sau tari idan Allah ya baka wannan zai iya hana maka wancan kamar yadda Safiyyah ta kasance, duk dan Adam tara yake bai cika goma ba, ba duk abinda mukeso daga abokan rayuwarmu muke samu dari bisa dari daga garesu ba.***

***Duk da haka Zayyan yana da kyakkyawan fatan cewa 'Azeezah Murtala', will meet all his dreams in a woman, his expectations and beyond.***

***Mu biyo Arch. Zayyan da matansa Safiyyah da Azeezah a littafi na uku. Yanzu***

***ne zamu fara labarin Zayyan da Safiyyah. 1&2 shimfida ne.***

***SUMAYYAH ABDULKADIR -Takori***

***07030137870***

***(WHTSP only)***

***01/04/2025***

***(Wannan littafi na sayarwa ne, GUNDARIN LABARIN ZAIZO A MANHAJAR TELEGRAM KADAI)***